KRB2P001

Arewabooks@nanahaleema11

Faɗuwar da Narma tayi a wajan shi ya ɗauke hankalin su daga kan su Omar aka yi kanta a guje ana jijjigata amma Narma ko numfashi bata yi. Hankalin su ya tashi matuƙa aka ɗauki Narma aka tafi zuwa asibiti da gaggawa. Sen takaicin duniya ya ishe shi, ji yake kamar ya je ya saka wuyan Omar a gabas ya yanka kowa ya huta. Kowa ka kalli yanayin fuskarsa a cikin su kasan baya cikin walwala, ransu duk a ɓace yake da abinda ya faru.

Sai da daddare Narma ta buɗe ido ta kalli iyayen nata guda biyu da suke zaune kusa da ita, ta kalli yan uwanta suma da suke gefenta. Murya a shaƙe ta ce, "Dad Faruk ya tafi ko?." Maganar da tayi ne ya saka suka fahimci ta farka duk suka kalle ta.

Sen ya ja tsaki bai ce komai ba ya fita daga ɗakin, dan in ya cigaba da zama bai san abinda zai aikata mata ba. Mum ce ta ƙarasa inda take ta riƙe hannunta tace, "Narma ki yi shiru da maganar nan mu koma gida, yanzu kina kwance asibiti ne." Narma ta ce, "Mum in na rasa shi mutuwa zan yi." Ran Mum ya ɓaci amma bata nuna ba ta ce, "na ce ki yi min shiru ko?." Narma ta yi shiru tana tuna abubhwan da suka faru kanta ya yi nauyi sosai.

Babu jimawa suka nemi tafiya gida dan dukkan su basu da nutsuwa, ganin Narman ta dawo daidai ba laifi sai suka bar asibitin zuwa gida. Babu wanda ya yi mata maganar kowa ɗaki ya shiga dan ya huta dole itama ta kwanta amma ba dan tana son yin bacci ba.

Mum ta shiga wajan Sen ta same shi a tsaye a jikin window yana amsa waya yana cewa, "kayi duk abinda ya kamata ka yi, ni fa da zan samu dama direct prison nake so a kai shi, bana son wani ɓata lokaci wallahi."

Daga cikin wayar aka ce, "Calm down Sen, ba a kai mutum prison kai tsaye ba tare da laifin komai ba." A fusace ya ce, "ba na faɗa maka har gida shaƙe ni ba?."

"Wannan ma hujja ce da za a ɗaure shi life in prison ba, kuma dole kotu ce zata yanke hukunci." Sen ya ce, "Kaga ni bana son wani long process, me za a yi yanzu?."

Ya ce, "ka bar komai a hannuna, zan haɗa masa sharrin da bazai iya fitar da kansa ba. Sunan ka ma bazai fito ba, domin zamu saka masa cocaine a jikinsa mu sake shi, in ya fita kan titi sai mu tura masa Ndlea su kama shi. Da sun kama shi zan san abinda zan yi a miƙa shi kotu, daga nan sai a yanke masa hukunci a matsayin mai safarar cocaine, kaga shikenan sunan ka bai fito a maganar ba."

Dad ya yi tsaki ya ce, "Kana ji, ka killace min shi a wani waje, sannan ka tabbatar da anyi masa horon da hannunsa ma bazai iya ɗagawa ba. Ka yi masa horon da zai kasa banbance a duniya yake ko a lahira, ka tabbatar da ya kasa koda motsa yatsun hannunsa. Su kuma sauran biyun ku barsu su tafi, ina so su je su isar da saƙon Tiger bazai sake komawa Kano ba har abada!" Yana gama faɗar hakan ya yanke wayar ya juyo yana kallon Mum da take kallon sa.

"Tun farko ai na faɗa maka kar ka haɗa min yaɗa da ɗan daba amma ka ƙi ji, har ka ke ganin zai yi maka aiki da hukuma baza tayi maka ba. Yanzu ga abinda ka jawo mana, wannan babban cin mutunci ne ga family. Yʼar da na haifa namiji kamar sa ya zo har gidan nan ya ce yana so, saboda akwai ka bashi fuska da sake har yake ganin mu dashi ɗaya ne" Mum ta faɗa a fusace tana kallon Dad dan ita gabaɗaya laifin sa take gani.

Sen ya ce, "Nayi kuskure, ban ɗauka abin zai zo da haka ba, amma yanzu zan gyara komai."

"Ko ka gyara ai an riga da an aikata, yaro yazo har gidan nan kana faɗa yana faɗa kamar sa'ansa?. Sannan ya kalle ka ya ce yana son yaɗarka, akwai abinda yafi wannan cin fuska ne?."

Sen ya yi shiru bai ce komai ba amma shi kaɗai ya san zafin da yake ji a zuciyarsa. Mum ta sake cewa, "yanzu ya zamu yi da Narma? Na tabbatar asiri ya yi mata, tunda ya samu damar hawa mota tare da ita ba dole ya yi mata abinda zata haukace haka a kansa ba. Ka duba yanayin da take ciki, ga zafin zuciya, ga zafin asiri, ga zafin marin da ka yi mata ɗazu."

Sen ya ce, "London zan tura ta taje ta huta. sannan maganar Ashraf zata dawo, dama tun asali shi take so, aikin asiri da ya yi mata ne ya saka tace bata sonsa. Yanzu kuma maganar zata dawo, da zarar ta huta ta dawo zan aura mata Ashraf." Mum ta ce, "ya dai gama cutar mu wallahi, ya lalata mata tarihi gabaɗaya. Wai Narma yake so, just imagine" ta faɗa cikin da takaici tana kallon sa.

Sen ya ce, "zan tabbatar masa da tayi masa nisa, zan tabbatar masa da iya furta wannan kalma da ya yi guda uku ta ina sonta sai ya yi dana sani yafi sau dubu uku, zan nuna masa ni ba kanwar lasa bane, duk isakancin da yake ji dashi na dame shi na shanye. Zan tabbatar masa da ruwa ba sa'an kwando bane, zan lalata mara rayuwa, zan saka shi ya ji zafin da naji a zuciyata, zan saka ya ɗanɗana irin zafin da ya saka Narma tana ɗanɗanawa."

Mum a fusace ta ce, "meyasa ba za a ɓatar dashi daga duniyar ba gabaɗaya? In aka kashe shi an kashe banza da wofi, zamansa a duniya tamkar cin fuska ne a gare mu." Dad ya girgiza kai ya ce, "ki barni dashi akwai, mutuwa ai mai sauƙi ce ga rayuwarsa, in ya mutu yanzu ai ban ci riba ba, ban saka masa abinda ya saka min a zuciyata ba. Sai na gana masa azabar da zai manta a wanne gari yake sannan komai ya biyo baya." Zaman kurame suka koma a ɗakin, Mum tana nata tunanin haka shima Sen ɗin shiru ya yi yana tunani mai cike da dana sanin duk abinda ya aikata a baya, tabbas da bai haɗa Narma dashi ba da yanzu hakan bata faru ba, duk kuskurensa ne amma zai gyara.

Da safe haka suka tashi duk fuska babu walwala, Narma bata fito daga ɗaki ba sai da taji duk suna falo sannan ta fito tana takowa kamar kazar da ƙwai ya fashewa a ciki. Duk da kallo suka bita kafin Dad ya riƙo hannunta ya zaunar da ita kusa dashi yana kallon ta.

Gabaɗaya ta rame a lokaci ɗaya, tayi wani iri kamar ba Narman sa yʏar gayu ba, tsana da takaicin Omar suka sake yi masa dirar mikiya, suka dabaibaye masa zuciyar sa. Kallon Mahaifin nata ta yi kamar yadda yake kallon ta kafin ya ce, "Ya jikinki?."

Narma cikin sanyi murya mai ɗauke da rauni ta ce, "Dad babu sauƙi. Dad Ina son Faruk a yadda yake, Ina so na rayu dashi. Kuma Dad zaka iya mayar da Faruk yadda ka ke so, zaka iya sakawa Faruk wani abu kamar yadda ka ke buri. Ni ban damu da bashi da abinda ka ke faɗa ba, shi nake so kuma shi nake so na aura Dad"

ta faɗa tana kallon sa kamar yadda yake kallon ta. Ya gama gasgatawa asiri ya yiwa Narma hakan ya saka ya kwantar da murya ƙasa ya ce, "Daughter ki daina wannan maganar kinga baki da lafiya, ki bari ki samu lafiya zamu tattauna."

Narma ta ce, "Dad bazan taɓa dawowa daidai ba indai baka amince da aurena da shi ba. Dad ni na fara furta Ina son Faruk, a hankali shima ya fara sona, Dad Meyasa zaka ce bazan aure shi ba?. Don Allah Dad kar ka bari a cutar dashi kaji...." ta faɗa cikin karyewar murya tana kallon mahaifin nata. Rungumeta ya yi a jikinsa tana kuka sosai, cike da tausayi yake shafa bayanta dan ya san ba yin kanta bane aikin asiri ne.

Nabil ya ce, "zai biya bashin asirin da ya yiwa Narma, Dad bai kamata a bar shi ba" ya faɗa cike da damuwar halin da take ciki. Narma ta ɗago daga jikin Dad ta kalli Nabil ta ce, "ni bai yi min asiri ba, ni ce na dinga bibiyarsa har sai da ya fara sona. Ba asiri ya yi min ba, haka kawai nake sonsa. Najwa ta ce, "daman haka zaki tunani ai, haka zaki ɗauka babu abinda ya yi miki dan ba yin kan ki bane, ya saka miki soyayyarsa zuciyarki ta hanyar asiri, ke bazai fahimci ba asiri bane ba ai.."

Narma ta kalli Dad ta ce, "Daddy kana ji suna cewa asiri yayi min ko? Kuma ba asiri ya yi min ba Dad, ni ina sonsa ne kawai. Har yanzu ina ƙaunarsa, shi kaɗai nake so na aura, in ba shi ba ni bazan auri kowa a duniya ba zan mutu a haka. Dad Ina ka saka aka kai shi?." Bai bata amsa ba ya kalli Najwa ya ce, "Najwa ki shirya zaku tafi London this week."

Narma ta ce, "Dad babu inda zan je, babu inda zan je na bar Faruk ɗina a Nigeria. Ni dashi zan rayu, aurensa nake so nayi da shi kaɗai zan iya rayuwar duniya. Dad in kace bazan aure shi ba zaka iya rasa ni! Zan iya mutuwa na bar muku duniyar gabaɗaya." Babu wanda ya iya tanka mata a cikin su, tausayi take basu gabaɗaya sun san aikin asiri ne ba yin kanta bane.

Mum ta taso ta riƙe ta tana rarrrashi itama kuma tana kuka sosai. Mum da kanta ta bata tea ta sha, sannan ta bata maganinta na jiya ta sha, ta kaita ɗaki ta kwnatar da ita a kan gado tana shafa kanta. Narma sai magana take yi ita kaɗai idanunta a rufe kafin bacci ya ɗauketa.

Fitowa Mum tayi bayan ta yi bacci ta kalli Sen ta ce, "ya faɗa musu inda ya kai Narma aka yi mata asiri, yayi gaggawar warware asirin kafin ya kai ga yin dama sani!" Mum ta faɗa ido na cikowa da ƙwallar tausayin Narma. Dad bai ce komai ba amma tabbas zai san abinda zai yi akan asiri nan da ya yiwa Narma, dole ma ya warware shi kafin ya rasa yarsa.

Kano.

Didi tun a daren jiya da ta ga dare ya yi babu Omar babu labarinsa hankalinta ya tashi, ta kira wayarsa yafi sau babu adadi ba a ɗauka, ta kira ta su Bashir duk a banza bata samu hakan ya ɗaga mata hankali sosai. Har sha biyu na dare ta kasa bacci, ko ya ta ɗin ji motsi zata firgita ta kalli ƙofa amma babu Omar babu alamunsa. Gashi ta san shi mutum ne da duk inda yaje komai dare a gida yake kwana, baya kwana a wani waje in ba gida ba. Gabaɗaya hankalinta ya tashi, bata da nutsuwa bacci ko kulle ido bata yi ba tana tunanin dawowar sa.

Rashin baccin da bata yi da wuri ba ya saka ta makara sallah asuba, sai shida ta farka a firgice ta fito ta shiga ɗakin Omar amma baya ciki. Salati take yi a zuciyarta, ta kira wayarsa zuwa lokacin ma wayar a kashe take. Daƙyar ta iya yin sallah dan ba nutsuwar kirki gare ta ba, tana idarwa ta sake kiran su Bashir amma suma duk a kashe.

"Innalillahi wa'inna ilahir raji'un! Allah yasa ba masu garkuwa da mutane ne...." Sai kuma bata ƙarasa ba jikinta har rawa yake kamar mazari saboda tashin hankali. Ta rasa wanne tunani ma zata yi ta ji daɗi, ta damu da rashin Omar matuƙa, inda ya saba kwana a wani waje ne ma da sauƙi, to ta san duk daren duniya Omar sai ya dawo gida hakan shine yake ɗaga mata hankali.

Taci kukan ta ta gode Allah, fuskarta tayi ja sosai ta kasa aikata komai a gidan gabaɗaya jikinta a sanyaye yake. Gashi an wayi gari juma'a bata da karsashin iya yin abincin sadaka dan ta tabbatar bata da wannan ƙwarin guiwar shiyasa ma bata yi tunanin yi ba.

Karfe sha daya na safe tana zaune a falo ta zuba uban tagumi ta jiyo sallama, ai a haukace ya fito tsakar gidan idon ta ya haɗu da na Goje ya yi wujiga-wujiga. Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "Alhamdu lillah! Meyasa ku ka tayar min da hankali ne

Bashir? Meyasa baku kira ni kum faɗa min a can zaku kwana ba?. Ina Omar ɗin yake?." Bashir ya kalle ta ya ce, "Didi ba tare muke da Damisa ba" Didi da mamaki ta ce, "Kamar ya kenan? Ba tare ku ka tafi ba?."

"Tare muka tafi Didi."

"A Ina ya tsaya shi?." Bashir ya sauke numfashi ya ce, "Didi mahaifin yarinyar nan ne ya saka aka kama Damisa."

"Innalillahi wa'inna ilahir raji'un! Ya saka aka kama Omar kuma Bashir? Akan wanne dalili? Laifin me ya aikata masa aka kama shi?. Bashir ka bani amsa, Mustapha ku nake saurare ku faɗa min!"Ta faɗa a gigice tana kallon su. Goje ya ce, "Didi bai masa laifin komai ba, kawai saboda yaɗarsa tana sonsa shiyasa ya yanke wannan hukunci. Ya saka a kama shi da laifin wai yazo har gida zai kashe shi kuma zai sace masa yaɗarsa. Mu kan mu damu aka kama gabaɗaya, Sanata ɗin ya saka a sake mu wai dan mu zo mu sanar daku Omar bazai dawo ba har abada."

Jiri ne ya fara ɗaukar Didi tayi saurin dafa bango tare durƙushewa a wajan tana kuka sosai. Kuka take yi wanda ya hanata magana, kuka mai sauti mai nunu da tsantsar damuwar da take ciki. Ta ce, "Bashir sai da na ce masa kar ya je, sai da nace masa kar ya je yarinyar nan tafi ƙarfinsa amma Omar da yake baya jin magana sai da yaje. Sai da nacewa Omar kar ya yi wannan gangancin amma Omar ya ƙi jin maganata. Da ya ji maganata da yanzu muna tare dashi babu abinda ya same shi, da ya ji maganata da yanzu ba a kama shi ba" magana take cikin fitar hankali tana kuka sosai hakan ya karya zuciyar Bash da Goje.

"Ki yi haƙuri Didi, zamu san yadda zamu yi ya fito, mun san manya da yawa zamu je mu saka su shige mana gaba a fito da Omar."

"Bashir babu lallai su amince, amfani kawai suke yi daku amma in kun shiga matsala baza su iya shige muku gaba dan warware ta ba. Bashir in akace Omar baya nan ya zan yi? In aka ce Omar bazai dawo ba ya zanyi?. Ta ya zan iya rayuwa bana ganin Omar? Ya rayuwata zata kasance Omar yana wani waje ana bashi wahala ni ina nan?."

Goje ya ce, "ki kwantar da hankalin ki Didi zai dawo in sha Allah, zamu san abinda zamu yi. Zamu bi duk hanyar da zamu bi dan dawo dashi. Ba ke kaɗai zaki shiga damuwa ba in baya nan, har damu Didi." Bata kula shi ba sai kuka kawai da take yi,

Goje ma kukan yake yi ya fita dan fara neman mafitar dawo da Tigar ko ta hali ƙaƙa.

Didi sai da tasha kukan ta son ranta sannan ta iya tashi jiki a sanyaye ta shiga falo. Babu wanda zata faɗawa damuwarta, ta saba su biyu suke solving matsalar su basu da wasu dangi da suke warware musu matsala balle ta ce zaje ta faɗa masu. Hajja ce ta faɗo mata a rai, ta miƙe da sauri ta saka hijjabi ta fita zuwa gidan Hajja.

Hajja da take zaune ita da Salma ganin yanayin Didin duk sai suka kalle ta dan sun san ba haka ta saba shigowa ba. Wajan Hajja ta nufa ta durƙusa kusa da ita kawai ta fashe da kuka. Hajja hankalin ta ya tashi ta ce, "Aisha lafiya? Me ya faru kike kuka?." Bata daina kukan ba sai da ta gaji sannan ta kalli Hajja ta ce, "Hajja Omar."

Hajja cikin tashin hankali ta ce, "me ya same shi?." Didi cikin kuka ta faɗawa Hajja duk abinda ya faru sannan ta ce, "Hajja yana can Abuja sun kama shi, Hajja ya zanyi? Na rasa inda zan saka raina. gabaɗaya hankali a tashe yake."

Hajja ta ce, "Hasbunallahu wani'imal wakil! Amma Ummaru ya yi ganganci."

"Hajja babu yadda ban yi dashi ba amma taƙi ji, Omar in yaso yin abu ko duniya bata so in dai shi yana so sai ya yi, na bashi shawara akan haka amma yaƙi saurarena. Hajja in wani abun ya same shi ya zanyi?" Ta ƙarasa faɗa murya na rawa. Hajja ta ce, "ki daina kuka ki kwantar da hankalin ki, in sha Allah zai fito."

Didi ta ce, "ta ya zai fito Hajja? Ta ya ya Omar zai fito bayan furucin da Sanata ya yi a kansa?. Hajja Sanata ne fa ya saka aka kama shi, dawowar Omar gida abu ne mai matuƙar wahala." Hajja tayi ajiyar zuciya ta ce, "kar ki damu Aisha, zan yiwa mahaifin salma magana ko ya san Sanata ɗin. Ɗan kwangila ne wataƙila suna da wata alaqa dashi. Ki kwantar da hankalin ki mu bi komai a sannu kar ki damu." Didi ta goge idanun ta ta ce, "to Hajja. Na rasa inda zan kai kuka na shiyasa nazo gare ki." Hajja ta dafata cikin tausayi ta ce, "kar ki damu, in sha Allah yadda kika kawo min kukan ki zan zama silar share miki hawaye. Salma bata ruwa ta sha" ta faɗa tana kallon Salma. Salma ta miƙe ta kawo mata ruwa ita kanta tausayin Didi take ji.

Ruwa ta sha tana jan numfashi cikin tashin hankalin da take cikii,Hajja ta dinga rarrashin ta tana bata baki har ta ɗan nutsu sannan ta ce bara ta koma gida ta

dawo. Bayan ta fita Salma tayi tsaki ta ce, "Wannan Omar da ɗaukar dala ba gammo yake, Ina shi ina soyayya da yɗar Sen Sagir banda ɗage irin na sa?. Haka kawai ya tayarwa da baiwar Allah hankali bata ji ba bata gani ba." Hajja bata ce komai ba ta san Daddy zai zo tunda juma'a ce tayi alqawarin yi masa magana in yana da hanya a fito da Omar ko dan saboda Didi ɗin.

Da yamma kuwa sai ga Daddy bayan sun gaisa da Hajja take yi masa bayani akan Omar. Daddy ya ce, "wanne Sentor ɗin kenan?." Hajja ta kalli Salma ta ce, "Salma meye ma ta ce sunansa?." Salma ta ce, "Daddy Sen Sagir Sani take nufi." Daddy ya ce, "Kai! Shi ya saka aka kama shi?." Hajja ta ce, "eh shine. In kana da hanya ka yi masa magana don Allah ya sako shi ko dan yɗar uwar sa da bata da kowa sai shi, ta shiga damuwa sosai Allah, kaɗai ya san halin da zata iya in akace Omar bazai dawo ba."

Daddy ya ce, "Hajja na san shi, amma bani da wata kyakykyawar mu'amala dashi gaskiya saboda mutumin bashi da kirki ko kaɗan. Bashi da kirki bai san kirki ba kuma bashi da ɗaga ƙafa kwata-kwata. Amma zan bincika a mutanena ni akwai wanda yake da mu'amala mai kyau dashi sai ayi masa magana, ko Ali zan tambaya ko shi ko Khabir. amma fitowarsa gaskiya da wahala." Hajja ta sauke numfashi ta ce, "Don Allah ka hanzarta."

"In sha Allah zan yi Hajja."

"Yauwa Allah ya yi albarka."

"Amin Hajja. Batun tafiyar ku umra yaushe ki ke ganin zaku je?." Hajja ta ce, "Duk sanda aka ce a shirye nake." Daddy ya ce, "Shikenan Hajja, zaki ji ni in sha Allah." Ta amsa tana ta addu'a yana amsawa shi da Salma. Hajja ta ce, "na san Ali ma yana hanya, wannan karon ka yi masa shigar saurin kaini Saudia. Khabir daman shi ya ce England zai kaini, na ce Khabiru nayi me a can, wai ki huta." Daddy yayi dariya ya ce, "ɗan rigima kenan." Daga nan suka yi sallama Daddy ya tafi.

Arewabooks@nanahaleema11

Bayan sallar magriba Hajja ta tura Salma ta kira mata Didi suka dawo tare. Hajja ta bita da kallo ganin duk ta firgice ta ce, "Aysha ki kwantar da hankali ki don Allah, kalli yadda ki ka firgice lokaci ɗaya." Didi ta zauna kusa da Hajja tana murmushi kaɗan-kaɗan. Hajja ta ce, "Nayi magana da mahaifin Salma, ya ce min shi bashi da wata alaqa mai kyau da Sanata, amma akwai wanda zai yiwa magana zai same shi

in Allah ya taimaka za a dace. Amma ya maimaita min bashi da kirki sai dai mu dinga addu'a kawai."

Didi tayi ajiyar zuciya cikin sanyi ta ce, "Allah ya sa Hajja.." Hajja ta ce, "amin. Sannan ki ɗauko abinda zaki ɗauko a gidan ki taho nan ki kwana, in aka farga Omar baya nan akwai masu jin haushinsa da yawa zasu iya cewa zasu shigo gidan ku. A san bai saaba tafiya ya bar gida ba, in aka lura da baya nan za a iya samu damuwa." Didi ta ce, "To Hajja, amma babu abinda zai faru."

"A'a dai, gwara dai ki dawo nan ɗin hankalina zai fi kwanciya." Wayar Didi ce take ƙara ta duba taga AbdulHamid ne yake yi mata waya, ta kalli Hajja ta ce, "Hajja AbdulHamid ne yazo."

Hajja ta ce, "to ya shigo gidan nan sai ku tattauna, shigar sa gidan ku ke kaɗai babu daɗi." Didi ta ce, "to bara na kira shi sai yazo nan ɗin." Ta faɗa tana ɗaukar wayar ta sanar dashi inda zai zo kafin Hajja ta tura Salma ta shigo dashi. Da sallama ya shigo cikin kamalar sa ta ko yaushe, Salma tayi masa iso har falon Hajja ya shigo ya gaishe da Hajja da girmamawa ta amsa tana cewa, "Yau ai wajan uwar gidan kazo ko?." Murmushi ya yi ya ce, "Daman yau zuwan na ki ne."

Hajja ta ce, "Haba shiyasa ka sha kwalliya mana, dan wannan kwaliyya bata amarya ba ce." Murmushi ya yi yana kallon Didi da bata da walwala sosai duk fuskar ta ta canja. Hajja ta ce, "ya shirin biki? Saura kwana nawa ya rage ne?."

"Saura sati shida. Yanzu ma nazo akan batun gidan da za a je gani saboda shirye-shirye." Hajja ta ce, "kai har saura mako shida? Lallai abu yazo. Allah ya nuna mana ya tabbatar da alkhairi." Ya amsa da amin.

Hajja ta ce, "gashi tana cikin yanayi na damuwa. Omar ne aka kama shi Abuja ba tare da laifin komai ba." AbdulHamid ya ce, "Subahanallah! Yaushe hakan ya faru?."

"Jiya."

"Bata sanar dani ba, na dai damuwa a muryar ta." Hajja ta ce, "wallahi shine ya canja ta gabaɗaya."

AbdulHamid ya ce, "Ya aka yi hakan ya faru?." Labari Didi ta bashi muryarta har rawa take yi saboda damuwa, ya sauke numfashi bayan ta ya ce, "case ne na

manya gaskiya tunda da kansa ya saka aka kama shi, amma a shari'ance bashi da hurumin kama Omar dan bai yi masa laifin komai ba. To matsalar itace yadda ƙasar mu take sai a hankali." Hajja ta ce, "Wannan gaskiya ne, amma zamu san abinda zamu yi in sha Allah."

AbdulHamid ya ce, "nima zan yi ƙoƙari daga ɓangarena in sha Allah. Kar ki damu kin ji?" Ya faɗa yana kallon Didi. Kai ya girgiza kai bata ce komai ba. AbudlHamid ya ce, "Amma ba ke kaɗai zaki kwana a gidan ba ko?." Ta ɗaga kai ta ce, "Hajja ta ce na zauna a nan."

"Gaskiya haka ya kamata, za a iya amfani da rashin Omar don cutar da ke." Hajja ta miƙe ta basu waje daman Salma ta shige ciki tunda ta ajjiye masa ruwa da lemo.

Rarrashin Didi ya dinga yi har sai da ya ga ta ɗan kwantar da hankalinta, maganar gidan da ta kawo shi ma basu yi ba dan ya san ba a nutse take ba sai ta dawo hankalinta sa tattauna. Bai jima sosai ba ya saka ta kira masa Hajja suka yi sallama yana godiya sannan ya tafi.

Didi ta ce, "Hajja bara na je gida na kashe kayan wuta na dawo." Hajja ta amsa mata sannan ta fita. Ba jimawa ta dawo gidan bayan ta kulle gidan ta dawo falon Hajja ta zauna amma gabaɗaya bata jin daɗi.

Sallamar Bashir ta ji daga gate ɗin Hajja, ta tashi da hanzari ta je ta ce, "Bashir ya ake ciki?." Ya kalli Didi ya ce, "Didi Ina ya bincikawa, na dawo Goje ya ce min kina gidan nan shine nazo na ji lafiya. Ko akwai wanda ya shiga gidan?."

"Babu kowa. Hajja ta ce na dawo nan na kwana ne saboda gidan babu kowa."

"Haba Didi, muna nan fa, wallahi ko kuɗa bazai taɓa ki da niyar cutarwa ba." Didi ta ce, "Gwara dai na zauna a nan ɗin Bashir. Don Allah duk abinda ake ciki ka yi min waya." Bashir ya amsa sannan ta dawo gida wajan Hajja gabaɗaya bata da nutsuwa.

Hajja ta ce, "Salma kai ta ɗakin Nayla ta huta." Salma ta raka Didi ɗakin Nayla da yake shirye tsaf sai khamshin turarenta yake yi. Murmushi tayi tunawa da Nayla, ta zauna a gefen gadon tana kallon kan mudubin Nayla da yake ajjiye da kayan

kwalliya kamar a gidan take rayuwa. Murmushi tayi ta kalli Salma da ta kawo mata abinci ta ce, "Salma ni fa ba baƙuwa bace, ki daina hidima haka."

Salma tayi dariya ta ce, "na sani Didi, hutar dake nayi." Didi ta ce, "na gode. Ɗakin ƙanwata Nayla sai ƙhamshi, ga kayan kwalliya kamar tana ciki."

Salma tayi dariya ta ce, "Aljanar kwalliya kenan." Didi tayi murmushi kawai bata ce komai ba Salma ta fita ita kuma ta ɗauki abincin ta fito ta zauna kusa da Hajja tana ci suna yɗar hira kaɗan.

Washe gari.

Abuja.

"Daddy Ina aka kai Faruk? Daddy a dokance baka da right ɗin da zaka saka a kulle shi ba tare da ya yi wani laifi ba. Yana da damar da zai kai ka ƙara court kuma dole a yi maka hukuncin aikata haka" Sai kuma ta daidaita murya ta ce, "Dad Ina yake? Don Allah ka faɗa min inda aka kai shi" ta faɗa tana zamewa a wajan tana kallon mahaifin na ta.

Shi tausayi take bashi sosai, gabaɗaya ta fita daga hankalinta ta koma wani iri kamar ba Narma yɗar gayu mai aji ba. Kallon Mum ya yi da take kallon sa kafin ya sake kallon Narma ya ce, "Narma ki nutsu." Narma cikin kuka ta ce, "bazan iya nutsuwa ba Dad, bazan iya nutsuwa ba Ina so na ganshi. Ina kewarsa, don Allah Dad kar ka cutar dashi. In aurena dashi ne baka so zan haƙura dashi amma kar ka yi masa komai don Allah Daddy, bashi da laifin komai ni ce na fara son sa."

Sen ya kalle ta ya ce, "na ce ki nutsu ko?." Zama tayi tana share hawaye ya kalle ta ya ce, "Ranar monday zaki jinginar da duk abinda ki ke yi zaki tafi London." Da sauri ta ɗago kai ta kalle shi murya na rawa ta ce, "Daddy London..? Me zan yi a can?."

"Ina so ki je ki huta hankali ki ya dawo jikinki daga baya za a san abinda za ayi."

"Dad i can't go anywhere without knowing where Faruk is. Where you have take to him?. Dad wallahi bai yi deserving wannan hukuncin ba, it's his fault for falling in love with me?. Kuma Daddy kai ka yi min alƙawari zaka bani duk wanda nake so, na kuma kawo maka shi ga sakamakon da ya biyo baya."

Dad kallon ta ya ke yi kamar bata cikin hankalinta, sai magana take yi mara kan gado kamar ba ita ba. Sai ya yi shiru bai ce mata komai ba. Narma ta ce, "don Allah Dad ka taimake ni ka bar Faruk ya tafi, ka ƙyale shi na yarda na haƙuta dashi bazan sake cewa Ina sonsa ba." Mum ta kalli Dad sai ta miƙe kawai ta bar wajan jim kaɗan sai gata ta dawo. Ba jimawa sosai sai ga wani saurayi ya shigo Mum ta taso ta riƙe Narma ya yi mata allurar bacci.

Mum ta kalli Dad ta ce, "ni na kira shi, na lura Narma ba ta cikin hankalinta. Ya gama lalata min tunanin yarinyata, ya gama cutar da ita. Na rantse da Allah na tsane shi bana sonsa, bana so ya rayu a cikin duniyar nan." Dad ya kalli Narma da tayi bacci a wajan ya kalli Mum ya ce, "sai a hankali zata dawo daidai, ita da ganin sa kuma har abada" yana gama faɗa ya fita dan ya zama dole ya canja shiri akan Omar.

Narma bacci tayi na sama da awa bakwai, dan tun safe take bacci har bayan sallar la'asar sannan ta farka da weaknesses joints. Daƙyar ta iya wanka ta fito tana kallon kanta a madubi, key ɗin mota ta ɗauka bayan ta shirya ta fita daga gida.

Kai tsaye wajan ɗan sanda da ya zo ya kama Omar ta je ta ce tana so ta ga Omar. Da kamar bazai kai ta ba amma ya ga ta dage sai ya saka aka raka ta inda aka ajjiye Omar.

Can ƙauyen Abuja ne, cikin wata unguwa da bata taɓa zuwa ba, aka buɗe mata wani wulaƙantaccen gida ta shiga ana biye da bayanta. Kallon gidan take yi tana hawaye, wai Omar ɗin ta ne a cikin nan ba tare da ya yi laifin komai ba.

Da ta shiga waje mai kyau aka ajjiye ta, inda masu azabtar dashi ɗin suke nan suka bata ta zauna. Bouncers ɗin da suke gidan kaɗai abin tsoro ne, Narma sai kallo su take yi domin kana ganin su ka san basu da imani, in ka shiga hannun su sai sun karya ka. Ita kam ta kasa zama sai zagaye take yi, tana ji an buɗe ƙofa da sauri ta kalli wajan. Ajiyar zuciya ta sauke ganin Omar da kayan jikinsa da suka zo amma kayan sun yi baƙi, duk da ba ɓaki sosai ba amma sun yi duhu. Fuskarsa babu walwala ko kaɗan, sannan wahala ta bayyana ƙarara akan fuskarsa. Da gudu Narma ta taho inda yake zata rungume shi ya motsa ya ɗan ja baya kaɗan sai ta kalle shi tana kuka.

Zubewa tayi a wajan ta ce, "im sorry Faruk! I'm sorry!!" Ta faɗa tana kuka sosai tana durƙushe a gaban sa. Bai ce komai ba bai ma kalle ta ba idanunsa a rufe babu abinda yake addabar zuciyarsa kamar ɓacin rai, babu abinda yake damunsa kamar halin da Didi take ciki. Zaman inda yake da wahalar da ake bashi baya damuwan sa kamar barin Didi da ya yi a gida ita kaɗai. Ya san tana can tana kuka, ya san tana can hankalinta a tashe saboda rashin ganinsa. Wannan tunanin yafi halin da yake ciki ƙuna da raɗaɗi a zuciyar sa.

Narma ta ce, "Na yi maka alqawari zan yi duk yadda zan yi wajan ganin ka bar wajan nan, zan yi iyakar iyawata wajan tabbatar da Dad ya ƙyaleka. Ni lawyer ce, zan yi duk abinda zan yi saboda kai Faruk." Sam kalaman ta basa kwantar masa da hankali dan gabaɗaya ma baya so yaji koda maganarta, ba wai dan ya tsane ta ko dan yana jin haushinta ba, sai da tsantsar baƙin cikin da yake zuciyarsa.

Narma ta sake cewa, "kayi magana Faruk, ka ce wani abun ko zan ji daɗi." Sai a lokacin ya sauke shanyayyun idanunsa a kanta, haɗa ido suka yi ya kalle ta na sakan biyar kafin ya janye idanunsa. Tabbas ta rame kana ganinta ka san tana cikin damuwa. Damuwarta bata dame shi ba, inda zai iya yi mata magana da ya yi magana akan Didi, amma baya tunanin ko waye yazo a wannan lokaci zai iya buɗe bakinsa ya yi magana, shirun shine alkhairi a gare shi.

Omar da kansa ya juya ya koma inda aka ajjiye shi, Narma na kiransa amma ya yi mata banza ko juyowa bai yi ba. Bashi da nutsuwar da zai iya kallon ta har ya yi mata magana shiyasa bai ce komai ba.

Narma da hawaye shaɓe-shaɓe ta fito ta shiga mota ta fizgi ta da ƙarfi zuwa gida. Tana tafiya tana kuka har ta je gida tana shiga falo ta zube a jikin Mum tana kuka mai sauti. Hankalin Mum ya tashi dan ita take nema tun bayan fitarta ta ce, "Narma Ina kika je? Kin san baki da lafiya kika fita ke kaɗai?. Me ya same ki ke kuka haka?."

"Mum naje na ga Faruk, Mum gabaɗaya an canja min Faruk ɗina, Mum Dad ya saka ana azabtar min dashi. Mum abinda nake ji a zuciyata ji nake kamar na kashe kaina. Kinga bouncers ɗin da Dad ya ajjiye suna dukan Omar, kinga irin azabar da ake yi masa? Kashe kaina kawai zan yi!."

Hankalin Mum ya tashi da kalaman Narma, da hanzari ta dannawa Sen waya Allah ya taimaka bai yi nisa ba ya ƙaraso gidan. A lokacim Narma take cewa, "Mum Ina

sonsa, Ina ƙaunarsa. Mum in Dady bai fitar dashi daga gidan da ya saka aka ajjiye ba ni zan yi da kaina, in aka hana ni zan yiwa kaina illa Mum, zan iya kashe kaina akan Faruk Mum...!" Ta ƙarasa faɗa tana jan sunan Mum ɗin tana kuka.

Sen ya ji ta ya ƙaraso ya tasar da ita tsaye ya rungume ta sai kuka take yi yana rarrashinta. Surutai take tayi masa barkatai akan Omar yana ta rarrashi yana shafa bayanta, sai da ya ga ta ɗan yi sanyi sannan ya kalle ta ya ce, "je ki ɗaki ki huta." Zata yi magana ya ce, "kar ki ce komai Daughter, je ki" ba musu ta tafi zuwa ɗaki tana share hawaye.

Mun ta kalli Dad a ƙufule ta ce, "Tunda har ka san zata iya binciko inda yake har taje ta ganshi meye amfanin barinsa nan? Meyasa baka kai shi inda baza ta iya zuwa ba?." Dad ya ce, "shiyasa zan tura ta London."

"Saboda shi sai ta bar Nigeria? Kenan shi ya yi riba akan ta ko me?."

"Saboda ta samu peace of mind. Shi kuma zan ji dashi" ya faɗa yana hawa sama ya bar Mum a wajan. Dole ya san abinda zai yi akan Omar kafin yarsa ta rasa hankalinta akansa.

Kaduna.

Nayla na zaune sun gama magana da Twiny a waya sai ta kira Salma, tana ɗauka ta ce, "Sis ya ki ke? Ya Hajja?." Salma ta ce, "lafiya lau Nayla, ya Mama da Abiy?."

"Kowa yana nan lafiya lau. Kin ga alert?."

"Eh naga kuɗi ya zo, na ce Nayla kuɗin wa ta saka min." Nayla ta ce, "Kuɗinki ne, first salaryna ya sauka."

Salma tayi dariya ta ce, "godiya nake ma'aikaciya." Murmushin yaƙe Nayla tayi kafin Salma ta ce, "ya ki ke? Ina fatan yanzu babu damuwa ko?." Murmushi ta yi kawai bata ce komai ba dan maganar da suka gama da Jidda kenan. Salma ta ce, "Nayla don Allah ki kwantar da hankalinki, in kina tayar da hankali Abiy bazai ji daɗi ba. Yanzu kin samu magana dashi ɗin?."

Nayla ta ce, "Salma na faɗa muku ni bana so ya san Ina sonsa, gwara ku taya ni addu'a kawai Allah ya kawo min ƙarshen ko meye. Bana jin zan iya furta masa kalmar so gaskiya."

"Amma Nayla cutar da kan ki ke ke yi. Ni ki faɗa min inda take a faɗin Kano naje na same shi nayi masa magana, sai cutuwa ki ke yi a kansa, ba ke kika sakawa kan ki ba Allah ne, meye aibu dan an faɗa masa?." Nayla ta murmusa ta ce, "Salma sanin waye bashi da wani mahimmaci, koda yana sona ma aure na dashi bazai yu ba. Na tabbatar Abiy bazai aura min shi ba."

Da mamaki Salma ta ce, "kafiri ne?." Nayla ta ce, "musulmi ne yana sallah kamar kowa, kawai dai aurena dashi na san bazai taɓa yuwa ba. Balle kuma ni bazan faɗi suna ba, kuma sannan bazan ce Ina sonsa ba." Salma tayi shiru kafin ta ce, "Nayla kar ki cutar da kan ki, ni na san Abiy indai kina sonsa shima zai so shi Nayla." Nayla bata ce komai ba Salma ta ce, "kin yi shiru."

"To me zan ce miki Salma? Asalin gaskiyata nake faɗa miki Salma, na san Ina sonsa, Ina ƙaunarsa amma bazan iya furta masa ba, kuma bazan iya faɗa muku sunansa ba koda zan mutu. Ƙarƙari in na mutu ku ce soyayya ce ta kashe ni keda Jidda. Tabbas in na bar duniya a yanzu da tasirin soyayyarsa a yin ajalina."

Salma ta sake karya murya zata yi magana Nayla ta katse ta ta ce, "Ya Didi? Tana lafiya?." Salma jin ta kawar da maganar sai ta ce, "Allah ya kawo miki mafita, in alkhairi ne a gare ki Allah ya zaɓa miki shi yɗar uwa."

Ta amsa da amin kafin Salma ta ce, "Didi tana gida, ɗazu dai ta fita daga nan, da yake a nan ta kwana." Nayla ta ce, "ta kwana a gidan Hajja? Lafiya dai ko?."

"Ba ƙalau ba dai. Taƙadirin ƙaninta ne mana, ɗan kuka mai jawa uwarsa jifa." Gaban Nayla ya faɗi matuƙa ta ce, "Me ya faru?."

Salma ta ce, "Wai yɗar Senator Sagir yake so dan tsabar bashi da hankali, to ko ni zauna gari banza babana ba Senator ba yazo ya ce yana sona ba sai na saka an yi masa abinda har ya mutu bazai manta dashi ba?. Ke ko bani ba, ko wacce bata kai ni rufin asiri ba ya ce yana so sai mun haɗu mun hana ta sonsa saboda ba mijin da za a so bane. Wai ƙafa ya ɗauka yaje har Abuja gidan Kano centaral Senator wai yana son yɗarsa Narma. Ki ji fa Nayla, Barr Nass fa wacce ki ke gani a social media yaje neman aure dan tsabar ƙarfin hali irin nasa. Tsabar wiwin da yake sha ta taɓa

masa ƙwaƙwalwa harda kwasar gajojin yɗan daban yaransa suka tafi wai neman aure. Ai kam Sen ya yi ram dashi, ya saka an ɗaure shi yana neman hanyar da zai kai shi prison, kuma ya ce sai ya yi life in prison."

Dum dum dum dum! Haka ƙirjin Nayla yake bugawa, ta zazzaro idanu waje kamar Salma ɗin tana ganinta. Duk da a.c da take ɗakin gumi ya gama wanke mata jiki saboda tashin hankali. An kama Omar? Omar ɗin ta da ake zancen zai yi life in prison? Omar fa masoyinta.

Salma ta katse mata tunaninta hanyar cewa, "Shine fa hankalin baiwar Allah ya tashi, ta shigo tana kuka abin tausayi. Allah ya haɗa ka da ɗan uwa irin Omar ma ko ƙaddara, haka kawai ya saka hankalin baiwar Allah ya tashi. Hajja har Daddy ta yiwa magana ya ce zai san yadda za ayi, za a yiwa Sen ɗin magana ko zai fito dashi. Gashi an ce bashi da kirki ko kusa, baya ɗaga ƙafa akan komai daƙyar ya amince ya bada Omar. Ke ni fa a wajena Omar ya cancanci fiye da haka, tsabar raini da tsaurin ido ya ɗauki ƙafa ya je har gida wai yɗarsa yake so? Ni ban ga laifinsa ba."

Nayla bata iya cewa komai ba domin ƙwaƙwalwarta tafi hutun rabin lokaci. Salma bata damu da shirun ba ta kuma cewa, "jiya da daddare Hajja ta saka ta dawo nan ta kwana saboda gidan babu kowa, kuma kin san yɗan daba yɗan uwasa masu jin haushinsa zasu iya shigowa su cutar da Didi. Inda mutumin kirki ne ma sai ka tauyasa masa, gwara ma haka."

Nayla hawaye ya gama wanke mata fuska, hawaye na tausayin masoyinta, hawaye na tausayin abin ƙaunarta, hawaye na tausayin halin da yake ciki a wannan lokaci. Hango fuskarsa take yi tana tunanin yadda ya koma a yanzu. Gabaɗaya nutsuwarta ta bar gangar jikinta.

Daƙyar ta iya buɗe baki ta ce, "Allah ya kyauta" daga haka ta yanke wayar ta toshe bakinta da hannunta fashe da kuka mai sauti. Mama tana tsaye daga bakin ƙofar duk hirarta da Salma taji, girgiza kai take yi domin wannan soyayyar da Nayla ta fara babban makami ne a gareta, tunda gashi har taji tana cewa mahaifinta bazai amince ba, lallai tsuntsu ya faɗo daga sama gashashshe.

Shigowa ɗakin tayi tana kallon Nayla, Nayla tana ganin ta manta halin da take ciki ta miƙe a guje ta faɗa jikinta tana kuka. Mama tana shafa bayanta a hankali cikin rarrashi ta ce, "yi shiru kar ki damu, kwantar da hankalinki."

Kuka Nayla take sosai na tausayi Omar da Didi, jikinta har rawa yake yi saboda tashin hankali da tsananin bugawar zuciya. Mama ta ɗago ta daga jikinta ta kalle ta ta ce, "Nayla ko baki faɗa min ba idanunki sun faɗa min soyayya ce ta saka ki a wannan yanayi, kar ki damu kar kuma ki tsorata ni uwa ce a gare ki, zan shige miki gaba wajan samun duk abinda ki ke so a wajan mahaifinki. Haka ne hasashena?."

Nayla ta yi shiru ta sunkuyar da kai sai hawaye da yake zarya a kan fuskarta. Mama ta sake janta jikinta ta ce, "kar ki damu ki nutsu, Ina tare dake a ko yaushe. Na kuma yi miki alqawari zaki auri wanda ki ke so ko waye shi, kar ki damu da faɗa min waye shi a yanzu, ki bari sai lokacin da zuciyarki ta aminta da ki faɗa min. Ni kuma a lokacin zan jajirce kamar ko wacce uwa na samar miki da farin ciki. Zan sadaukar da komai wajan ganin mallaki wanda ki ke so, zan iya yin komai dan tabbatar da cikar burin ki Nayla."

Nayla kwanciya tayi a jikin Mama tana kuka tana ji wani ɓangare na zuciyarta na tabbatar mata da abinda Maman ta faɗa. Ido ta a kulle cikin tausayi da soyayyar Omar..

KRB2P003

Arewabooks@nanahaleema11.

Mama sai da ta bar Nayla tayi kukan ta sosai sannan ta ɗago ta daga jikinta ta ƙarasa da ita kan gado ta zaunar da ita, ta tashi ta kawo mata ruwa a glass cup ta sha ta zauna a gefenta tare da riƙe hannunta tana kallon ta. Nayla sai sauke ajiyar zuciya take yi irin ta wacce ta sha kuka ta gaji. A tausashe Mama ta ce, "ki nutsu, Ina tare da ke a akan duk abinda ki ke so. Mahaifiyarki ni ta barwa amanarki, bazan taɓa bari wani abun ya cutar dake ba."

Nayla ƙarfin guiwa maganar Mama take ƙara mata hakan ya saka ta ɗaga kai Mama ta ce, "Sanar dani yaushe kika fara sonsa? Sannan a Ina yake?." Nayla ta rausayar da kai ta ce, "Mama don Allah bana so Abiy ya sani."

"Bazan sanar dashi ba Nayla, ai wannan sirrin uwa da yarta ne." Nayla ta sauke numfashi ta ce, "A Kano yake da zama Mama, kuma ni ma ban san lokacin da na fara sonsa ba."

Mama ta ce, "ya sunansa?." Nayla ta kalli Mama sai bata ce komai ba. Mama ta ce, "shikenan ba sai kin faɗa min waye ba, amma meyasa ki ke cewa Abiy bazai amince ki auren shi ba? Yana da wani hali mara kyau ne ko kuwa ba musulmi bane ba?." Nayla a sanyaye ta ce, "Musulmi ne Mama, kawai dai...." Sai tayi shiru bata ce komai ba. Mama ta ce, "Ina jinki, kawai dai me?."

Nayla ta kalli Mama ta ce, "don Allah Mama mu bar maganar nan kawai." Mama tayi murmushi ta ce, "shikenan Nayla. Ki daina saka damuwarsa a zuciyarki komai zai zama labari kin ji ko?." Nayla ta ɗaga kai Mama ta ce, "Dama nazo na sanar dake Abiy ya ce zaki yi baƙo yau, sai ki shirya tarbar zuwansa."

Nayla ta amsa a sanyaye Mama ta dafata ta ce, "kar ki damu, zaki auri wanda ki ke so in sha Allah." Murmushin yaƙe kawai tayi dan ko amin din ma bata ce ba. To in ta ce amin ta wacce hanya auren zai zo? Na farko dai Omar bai ma san tana sonsa ba, na biyu yanzu haka Omar yana kulle babu ranar fitowarsa, na uku koda yana nan ita dai baza ta ce tana sonsa ba, na huɗu Abiy bazai amince ta auren shi ba. Duk da Abiy baya damuwa da lallai sai mai kuɗi za a aura, amma yana son good background da kuma good manners wanda ta tabbatar da Omar ya rasa. To akan me zata ce amin? Gwara tayi shiru kawai kar ta faɗa da bakin mala'iku.

Mama ta ce, "ki yi ƙoƙari ki dinga sakewa in ba haka ba Abiy zai takura ki akan rashin da sakewar nan taki." Kai ta ɗaga kawai Mama ta fita ita kuma ta koma da baya tana ajiyar zuciya. _Ko ya Omar yake yanzu? Wanne hali yake ciki?. Allah sarki Omar ya haɗu da sharrin so, son maso wani kenan, ni ina nan ina haukan sonsa shi yana can ya sadaukar da ƙuruciyarsa akan wata. Ko da yake abinda nake ji shima shi yake ji a zuciyarsa akan wata, amma ni bazan iya furta Ina sonsa ba, gwara na mutu....eh gwara na mutu kawai na huta. Bayan a gabana yake yiwa wacce take son sa faɗa a waya...? Hmmm ga wulaƙancin da Didi ta faɗa min ya yi mata a gabanta, me ya kaini cewa ina son Omar?. Gwara nayi shiru kawai na auri wanda suke sona._ tunanin da take yi kawai a zuciyarta kenan ita kaɗai cikin yanayi na damuwa da bugawar zuciya.

Sai bayan sallar i'sha sannan aka turo tazo baƙon ta yazo. Daƙyar ta samu ƙarfin guiwar motsawa daga inda take ta miƙe ta canja kaya zuwa doguwar riga ta slik mai kyau da santsi. Ɗinkin bubu ne, amma wacce ake yayi, wacce ake ɗan ɗaureta daga ciki. Tayi mata kyau sosai ta saka hular kayan sannan ta yaga mayafi ta fito zuwa falon.

Yau ma dai baƙuwar fuska ta gamu da ita, daman Abiy ya ce mata mutum huɗe ne har Abbas, ta zauna da mutum biyu ga na ukun, na huɗun kuma Abbas ne daman ta sani. Kamar sauran bata haɗe rai kuma bata kore shi ba, sun gaisa da girmamawa ya gabatar da kansa itama ta gabatar da kanta, sun ɗan tattauna kafin ya yi mata sallama ya tafi.

Kamar ko yaushe yau ma dai Abiy na zaune a falo ta dawo, shi da Yaya J ne da kuma Mama. Da sallama ta shigo kamar baza ta zauna ba sai kuma Abiy ya kira ta dole ta dawo ta zauna gabanta na faɗuwa matuƙa. Abiy ya kalle ta ya ce, "Mamana kun gaisa da Lamin ɗin?." Nayla ta ɗaga kai ta ce, "Eh Abiy, ya tafi ma."

Abiy ya ce, "To daga kansa zan dakatar da duk mai zuwa neman aurenki. A cikin Omar, Lamin, Abbas da Hashim ki ɗauki guda ɗaya a cikin su. Dukkan su na amince da iyayen su, aikin su, ilimin su, halayen su da sauran su. Sannan ko wanne ɗan babban gida ne sun fito daga gidan mutunci da tarbiyya. Babu ɗaya a cikin su da yake shan koda taba balle a kai ga batun maye ko wani abun. Babu wanda na bawa damar zuwa wajanki a cikin su har sai da nayi bincike a kansu sannan na bari suka zauna dake. Kun tattauna da ko wanne a cikin su, to ki zaɓi guda ɗaya da ki ke jin zaki iya zaman aure dashi. A cikin guda huɗu ai na san baza ki rasa wanda ya kwanta miki a rai ba, In kuma ɗan uwanki Abbas kika ɗauka duk ɗaya ne."

Nayla gabaɗaya kalaman Abiy tarwatsa mata zuciya suke yi, dan gabaɗaya abinda yake lissafowa samarinta suna da shi ita kuma hange ta ke yi Omar bashi da ko ɗaya. Gashi Abiy ya jefa ta a tsaka mai wuya, ta ya ake tunanin zata iya ɗaukar mutum ɗaya a cikin su da sunan tana so? To wa take son ɗin a cikin su...?ita ko kamannin su ma bata tunanin zata iya hange a idanunta balle tayi batun so, ko waya suka kirata bata jimawa take sallama dasu ta kwanta. So ɗaya take yiwa mutum ɗaya tak a duniya kuma shine Omar Tiger, ta kuma tabbatar son bashi da wani amfani tunda ba auren sa zata yi ba.

Abiy ya katse ta ya ce, "kina ji ko?." Nayla ta girgiza kai ta ce, "in sha Allah Abiy. Ka taya ni da addu'ar neman zaɓin Allah." Abiy ya murmusa ya ce, "Allah ya tabbatar da alkhairi a rayuwar ku baki ɗaya." Aka amsa da amin ta tashi ta shiga ciki.

Abbas ta gani yana yi mata waya ta taɓe baki dan baza ta ɗauka ba, ita a cikin samarin nata ma zata iya auren kowa amma ban da Abbas, sam tsarin Abbas bai mata ba, ita maza masu gym ɗin nan ba burge ta suke yi ba. Omar ne kawai mai irin wannan jikin da taji ya burgeta amma shi kam Abbas ko kaɗan bata son halittar jikinsa. A cikin samarin na ta ma gwara Omar, zata iya ɗaukarsa ba dan ya cancanta a wajanta ba, sai dan saboda sunan masoyinta da yake dashi kuma yana da sanyi bashi da yanayi saɓanin nata Omar ɗin. Da wannan tunane-tunanen ta shirya ta kwanta tana tunanin halin da masoyin ta yake ciki a Abuja.

Bayan Kwana biyu.

Abuja.

Yadda Narma take kuka sai ka ɗauka mutuwa aka yi mata, ta rame sosai ta yi wani iri da ita kamar ba ita ce Narma yʻar gayu mai ji da ƙwalisa ba. Soyayya ta sakata birkicewa, ta koma kamar wata mai taɓin hankali saboda surutan da take yi ita kaɗi. Wannan dalilin ya saka iyayenta suka sake gasgata asiri Omar ya yi mata.

"Mum ni bana son barin Nigeria, in naje England me zan yi a can?. Ni ku barni na zauna a nan babu inda zan je" ta faɗa tana kuka tana riƙe da Mom da take riƙe da ita itama. Mum a tausashe ta ce, "zaki je can ne ki samu hutu Narma, ba zama zaki yi a can gabaɗaya ba, zaki huta ne na ɗan lokaci sannan ki dawo kin gane?."

"A'a Mum, ni a barni na zauna a nan bana so na tafi na bar Faruk a gidan da Dad ya kai shi, ban yi masa adalci ba in na tafi tunda ni ce na gayyato shi. Don Allah ku bani dama na fitar dashi sai na tafi."

Dad ya ce, "Narma! Ki yi abinda aka ce kawai." Narma ta ce, "Dad bashi da laifi fa, ni ce nace Ina sonsa har ya amince dani, kuma ni na gayyace shi nan ya amsa gayyata ta yazo. Sai da ya maimaita min babu matsala na ce masa babu saboda na

yarda da alqawarin da kayi min, ban ɗauka zaka yi disappointing ɗina ba Dad. Na ɗauka kana son duk abinda nake so, na ɗauka zaka bani abinda nake so ko meye shi, amma ka kasa....ka kasa bani farin ciki Dad...ka kasa cika min burina..." ta faɗa tana kuka sosai. Dad cikin tsawa ya ce, "Narma ya isa! Kar na sake ji kin ce nayi disappointing ɗin ki

Narma ta ce, "inda falon sama zai yi magana zai bada shaida, kai ka ce ko waye kana maraba dashi, kai kace kana maraba da shi matsayin sirikinka, da yazo dan ya gaishe ka ga abinda ka yi masa. Ina sonsa, ku barni na zauna a nan in ba haka ko na je can bazan ji daɗin zaman ba."

Dad a fusace ya ce, "sai kin tafi! sai kin je England in ki yi duk abinda zaki yi. Last warning zan miki yanzu, kar na sake ji kin furta na karya miki alqawari, kar na sake ji kin ce kina sonsa kin gane!?." Kallon Dad ɗin take yi dan bata saba jin tsawa daga wajan iyayenta ba hakan ya bata mamaki ta ce, "Dad you shouted me?."

Mum ta katse Sen ta ce, "Dear stop please, ka daina sake tsorata ta don Allah. Ka bari mu ji da yanayin da take ciki mana." Shiru ya yi bai ce komai ba ta kalli Mum ta ce, "Mum zaki saka a fito dashi? Dad ya saka ana ta wahalar dashi. Zaki bari na aure shi?."

"Babu maganar aure tsakaninki dashi, in akwai a zuciyarki ya kamata ki goge dan ba abu ne da zai yu ba" Dad ya faɗa yana nuna ta da yatsa dan ta fara fusata shi. Zata yi magana ya katse ta ya ce, "kar ki ce min komai, zaku yi missing flight ku wuce ku tafi" ya faɗa yana hawa sama. Narma tana kuka Mum ta riƙe ta har bakin mota, ta shiga itama sai da ta kai su airport tana jajjadawa Najwa kula da ita, sai da taga tashin jirginsu sannan ta dawo.

Kai tsaye ɗakin Dad ta shiga ta same shi ta ce, "ya zama dole a saka Tiger ya karya asirin da ya yiwa Narma, sannan ya zama dole a samu abinda zai ɗauke mata hankali a London." Dad ya kalle ta ya ce, "na san abinda zan yi akan maganar Tiger. Maganar Narma a London kuma Ina tunanin nan da kwanaki biyu na tura mata Ashraf."

Mum da mamaki ta ce, "Ka tura mata Ashraf for what?." Dad ya ce, "Auren masa ita zan yi." Mum ta wara idanu waje ta ce, "aure fa? Auren Narma ne zai kasnace a

haka?." Dad ya ce, "kina da wata hanyar ne bayan wannan? Ashraf shine boyfriend ɗinta, shi ta so kafin asirin Tiger ya kamata, in aka ɗaura auren su ya bita London zai ɗauke mata kewar Omar har ta manta dashi. Ki daina tunanin a yadda auren zai zo, ki duba yanayin da yɗarki take ciki. Ba lallai sai duniya ta san anyi auren ba, in aka ɗaura auren daga baya in ta dawo daidai sai ayi biki mai girma. Amma a yanzu ba maganar biki ake yi ba, magana ake ta ceto Narma."

Mum tayi ajiyar zuciya ta ce, "Dear Don Allah ka tabbatar da Tiger baya numfashi a duniya, ka tabbatar da ƙasa ta rufe idanunsa. Duk ta silarsa wannan abubuwa suke faruwa, don Allah a ɓatar dashi a daina jin labarinsa, hakan shine kawai zai saka na huce daga raɗaɗin abinda ya yiwa Narma." Sen ya taso ya rungume ta ya ce, "kar ki damu Dear, na san abinda zan yi akansa. Labari da tarihin Omar zai shafe a duniya gabaɗaya, don't worry."

"Saboda shi Narma ta tafi London ba dan tana so ba, saboda shi ana ƙoƙarin yi mata irin wannan auren. Ji nake kamar na kamo shi na harbe." Bayan ta yake shafawa cikin rarrashi amma shi kansa abin ya tsaya masa a zuciya, zai kuma zan abinda zai yi.

Kano.

Didi tun tana jiran tsammani daga Hajja har ta gaji, ba labarin ceto mata ƙaninta gashi har an yi kwanaki goma da kama Omar. Duk ta damu ta koma wani iri yɗan unguwa kaf an fahimci Omar baya nan, duk da haka babu wanda ya yi gigin yiwa Didi wani abun a san duk inda ya je tabbas ai dawo.

A ranar Bashir ya ce mata zai je Abuja ya duba prison ko an kai Omar ɗin can. Sai dai ya je ɗin ya faɗi sunan Omar matsayin wanda yazo yiwa ziyara, kaf sunayaen mutanen da suke ciki babu mai suna irin na Omar. Gabaɗaya ya damu shima a haka ya dawo Kano a ranar duk ya galabaita.

A gidan Hajja ya same ta da daddare ko abinci ta kasa ci tana jiran dawowarsa. Tana jin sallamar da ta miƙe tana kallon sa har ya shigo yana kallon ta shima. Hajja ta ce, "Bashir ka ga Omar ɗin?." Bash ya girgiza kai ya ce, "Ban gan shi ba, ko mai irin sunan sa an tabbatar da baya cikin prison ɗin."

"Innalillahi wa'inna ilahir raji'un! Shikenan sun kashe min Omar, Hajja sun kashe min shi" ta faɗa cikin kuka sosai. Hajja ta riƙeta cikin tausayi ta ce, "Haba Aisha! bai kamata ki yi wannan tunanin ba, in sha Allah Omar yana nan da ransa kuma zai dawo gare ki in sha Allah."

Didi tana kuka ta ce, "Hajja in ba basu kashe shi ba yana ina? Meyasa ba a same shi a can ba?" Ta faɗa tana sake fashewa da kuka cikin rashin mafita. Sai kuma ta kalli Bashir a firgice ta ce, "Zaka iya raka ni Abujan gobe? Ina so naje gaban Senator da kaina na bashi haƙuri akan abinda Omar ya yi masa. Zaka raka ni mu je tare?."

Hajja ta kalle ta tana jinjina girman ƙaunar da take yiwa Omar tace, "wa kika sani a Abujan da zakije? Sannan kema in ya yi miki wani abun fa?." Didi ta ce, "Hajja gwara na je, gwara naje Hajja bazan iya zama babu Omar ba. Ban san halin da yake ciki ba, ko zai yanka ni gwara naje na bashi haƙuri."

Tausayi ta bawa Hajja ta dinga rarrashinta amma ta kafe akan ita fa sai ta je Abuja. Hajja ganin ta kafe ya saka ta ce, "Shikenan Allah ya kaimu goben, zan saka a kai ki da motata sannan ku tafi Bashir ɗin." Didi ta ce, "Na gode Hajja." Hajja ta ce, "ya isa, ki daina wannan kukan shine bana so."

Hajja ta kalli Salma ta ce, "Ko zaki raka ta Abuja gobe?." Salma ganin Didi ba ita take kallo ba sai ta wara ido ta ce, "Zan je wajan Daddy gobe." Hajja ta kalle ta kawai dan daman ta san baza ta je ba, dama dai Nayla ce. Ita kuwa Salma ƙunƙuni take yi tana cewa, "Haka kawai na je nima ayi ram dani, wallahi bazan je ba ita dai taje tunda ɗan uwanta ne. Haka kawai babu dangin iya babu na Baba ga rashin mutuncin da yake yiwa mutane, naje na bada haƙurin a karɓo shi ƙarshe ya dawo yana yi min wulaƙanci. Bazan je ba wallahi."

Ranar daƙyar Didi ta iya yin bacci,asubar fari suka buga sammako suka ɗauki hanyar Abuja da fatan dacewa da kuma nasara a kan abinda zai kai su Abujan.

Kaduna.

Nayla ta damu sosai akan Omar, tana ƙoƙarin dannewa ne kawai saboda Mama tace ta dinga daurewa saboda Abiy, amma Allah kaɗai ta san meye a zuciyarta da kuma abinda take ji akan Omar da rashinsa da aka ce ba a yi ba. Ta fara neman hanyar da zata bi wajan ganin ta dawo da Omar, ta rasa inda zaje ta samu damar da za a iya yiwa Sen magana ya sakar mata masoyinta. Tana nan tana shiri akan tunkarar Ogan su na wajan aiki da maganar Sen ko Allah zai saka a dace.

Video call Nayla da Salma suke yi suna hira, hirar dai rabi rarrashin Nayla take yi akan abinda yake zuciyarta. Nayla ta ce, "Salma ya batun Didi kuwa? Omar ɗin ya dawo?." Salma ta yi ƙaramin ta ce, "ke wai kullum sai kin tambaye ni batun wani Omar? Ina ruwanki da dawowarsa ne?." Nayla ta daure ta ce, "Ina damuwa ne saboda Didi kawai malama."

Salma ta yi tsaki ta ce, "Har yau dai babu labari, Daddy bai san kowa da yake da alqala mai kyau da Senator ba. Allah sarki kin san me?." Nayla da ta ke ta shirin tafiya aiki ta ce, "Sai kin faɗa."

"Didi ta ɗauki hanyar zuwa Abuja dan ta bawa Sen haƙuri. Wallahi ni itace take bani tausayi ba shi ba. Ban ɗauka haka take tsananin ƙaunar Omar ba sai yanzu, gabaɗaya ta firgice in kika ganta sai ta baki tausayi. Tana son ƙanin nan nata, gashi Allah ya haɗata da ƙaddara, dan ɗan uwa irinsa ai ƙaddara ce." A sanyaye Nayla ta ce, "ita da wa ta tafi?."

"Ita da yaron sa Bashir sai Hajja da ta saka Sayyadi ya kai su."

"Allah sarki, Allah ya sa tayi nasarar zuwa, Allah yasa su dawo tare."

"Amin. Ke ni bana so ma ya fito wallahi, haka kawai yake bani haushi." Nayla sai taji ranta ya ɓaci sosai da kalaman Salma akan Omar, ta harare ta tare da yin tsaki ta ce, "Sai ki ta ji ai, bani da lokacinki" ta faɗa tana datse kiran tana jin zuciyar ta bugawa sosai. Tabbas ya kamata tayi wani abun akan Omar.

A haka ta gama shiri ta fito zuwa falo ta tarar Abiy ma bai fita ba. Ganin sa a falo sai suka gaisa ya ke cewa, "ya zaki yi da bikin yayarki Shayida ta Kano?." Nayla ta ce, "Zan je."

"Aikin fa?." Nayla ta kalli Abiy jin abinda ya ce sai ta ce, "Abiy ai na lokaci ɗaya ne, zan ɗauki excuse ." Abiy ya ce, "har yaushe kika fara aikin da zaki fara ɗaukar excuse? fara ɗaukar excuse ya yi wuri Mamana."

"To Abiy haka za ayi bikin Yaya Shayida babu ni?" Ta faɗa tana hawaye daman a wuya take, kukan take son yi. Abiy ganin tana kuka aya yi tsaki ya ce, "to meye abin kukan? Kwana biyu kin zama shagwaɓaɓɓiya, da anyi magana sai kuka."

Ta share ido dan a zahiri ne kawai take kukan son zuwa bikin Shayida Kano, amma a baɗini Omar ne a zuciyarta. Abiy ya ce, "akwai abinda zai kai ni Kano ni zan riga su Maman ku yin gaba, babarki ma ta ce ranar laraba zata tafi, in sun tafi ranar laraba ɗin ai Jawad yana nan, sai ku zauna tare in ya so ranar Friday sai ki tafi kema."

Nayla ji tayi kamar an sakata aljanna saboda farin ciki, ta kasa ɓoyewa ta ce, "To Abiy Allah ya kaimu, na gode sosai."

"To maza tafi aiki." Hanyar fita tayi tana murna ya ce, "kin yi breakfast?." Nayla ta ce, "nayi takeaway sai naje can."

"Okay, Allah ya kiyaye" ta amsa da amin ta fita tana murya. Ko babu komai zata je Kano, duk da dai Omar ɗin baya nan amma zata je ko gidan su ne ta kalla ta ji daɗi, kuma tayi alƙawarin zata yi duk yadda zata yi wajan ganin Omar ya dawo.

Fan's Waye zai ci wasan ne? Nayla ce ko kuma Narma?. Waye zai yi silar dawowar Omar? Nayla ce ko kuma Narma ko kuma Didi ce?.

KRB2P004

Arewabooks@nanahaleema11

Su Didi sun isa Abuja sha biyu na rana, Bashir yana yiwa driver Hajja kwatancen estate ɗin da zasu shiga wancan lokacin. Suna zuwa gate na estate ɗin suka ganshi a kulle ga manyan jami'an tsaro a wajan da alama ba a shiga. Didi ta kalli Bashir ta ce, "ba a shiga ne?." Bashir ya ce, "Gaskiya mu ma saboda Damisa ne a lokacin mu ka shiga, amma yanzu ban san ta ya zamu shiga ba." Tk ya ce, "muje muyi magana dasu mana."

Didi ta ce, "A'a karku je su yi mu ku wani abun fa." Tk ya ce, "kar ki damu babbar Yaya, Bash mu je" suka faɗa suna fita zuwa wajan su. Sun jima suna magana kafin su dawo su kalli Didi Bashir ya ce, "sun ce ba a shiga dole sai da izini." Didi ta yi

ajiyar zuciya ta ce, "kawai dai munyi wahalar banza za su ce." Kallon gidan da aka nuna mata na Sen ta ke yi don shine na biyu layin, jinjina girma da kyaun da take yi a zuciyarta.

Didi ta ce, "Bashir ku shigo mu san abinda zamu yi, gashi mu ba wani muka sani a garin nan ba balle mu je mu huta." Driver Hajja ya ce, "Akwai gidan da Hajja ta ce na kai ku ku huta a can, ku zo mu je in yaso in anjima sai mu sake dawowa nan ɗin." Shiga motar suka yi ya bar unguwar dasu zuwa gidan da Hajja ta ce su je.

Gida ne babba mai apartment guda biyar, ya faka motar ya fito suka shiga ciki yana cewa, "Gidan Hajja ne da take bayarwa haya, ɗaya daga cikin gidajen da mahaifiyar Nayla ta rasu ta bari Hajja ta gada, shine take karɓar kuɗin haya. Wannan ɓangaren babu kowa ta ce na kawo ku nan a huta in yaso gobe sai mu koma Kano."

Didi murmushi take yi a bayyane ta ce, "Allah ya sakawa Hajja da alkhairi, ya biya ta da aljanna. In ba ita ba waye zai yi min haka?." Suka amsa da amin suna shiga ciki. Ƙofar farko ya nunawa Bashir da Tk ya ce, "ga ɗaki a nan sai mu zauna a ciki, ita sai ta shiga ciki." Da to suka amsa suka shiga ciki itama ta shiga.

Falon harda kujeru sai dai ya ɗan yi ƙura, bata damu ba ta zauna sai ga wuta haske gauwaye ina. Sayyadi ne ya shigo da sallama ya shigo ya kunna mata a.c sannan ya kalle ta ya ce, "yanzu za a kawo abinci." Ita dai Didi murmushi take kawai cikin jin daɗi. Ƙaunar Hajja da iyalanta take ji a zuciyarta, girma da darajar na sake mamaye mata zuciya. A nan suka ci abinci suka ɗan huta, ita dai tana kwance ne kawai amma burinta kawai ta ga Sen ta nemi alfarma ko zai amince.

Sai dare sannan suka koma wajan suka tarar an canja masu tsaron wajan ba na ɗazu bane, suka sake yi musu magana amma basu bada dama ba Didi ta ja ta tsaya a wajan ta ce babu inda zata je sai ta ga Senator. Sun hana su tsayawa a wajan gate ɗin, sai can baya suka koma kamar almajirai.

Motar Sen ce take fitowa daga gidan ba tare da jiniya ko jami'an tsaro ba, ya hangi su Didi a tsaye tunda a baya yake zaune amma bai san su waye ba, suka wuce su dan ya ɗauka almajirai ne. Bashir ya kalle ta ya ce, "shine ya wuce a cikin motar nan." Didi ta ce, "mu jira dawowarsa to."

Haka suka ta zaman jiransa sama da awa uku sannan motar ta dawo ta sake wuce su ta tsaya a wajan masu gadin wajan Sen ya sauke glass daga baya da yake zaune ya ce, "su waye waɗancan can a tsaye? Meyasa ku ke barin mutane a tsaye a bakin gate ɗin nan?." Ɗaya daga ciki ya ce, "Sorry Sir! Sir kai suke nema, tun da rana suka zo. Na gansu a lokacin da nazo wajan Jibson."

"Ni suke nema kuma? Ina sadaka ne a gidana?."

"Haka dai suka ce kai suke nema." Sen ya juya ya kalli bayan sa ya hango Didi a tsaye tana kallon motar.

Kallon su ya yi ya ce, "kira ɗaya daga cikin su." Cikin ɗaga murya ya yafito Tk, da hanzari Tk ya ƙaraso Sen ya kalle shi ya ce, "su waye ku?." Tk ya ce, "mu yan uwan Damisa ne, mun zo muna son ganin ka, tare da yayar sa muke." Sen ya ce, "waye haka?." Da mamaki Tk yake kallon sa amma sai ya ce, "Tiger na Kano."

Wani irin kallo Sen ya yi masa na baku da hankali ya ce, "gani na ɗin me ku ka zo yi?." Zai yi magana ya kalli masu tsoron wajan ya ce, "a tabbatar duk bar wajan nan yanzun nan, in na leƙo naga ɗaya a cikin su ranku ne zai ɓaci" yana faɗa ya ɗaga glass ɗin motar aka ja motar zuwa ciki.

Nan da nan aka fara yi musu tsawa su bar wajan babu shiri suka bar wajan zuwa inda suka ajjiye motar. Jingina Didi tayi da motar ta rufe ido kawai bata ce komai ba. Kallon gidan ta sake yi ta yi ajiyar zuciya cikin damuwa mai yawa. Ga gidan tana kallo amma babu yadda zata yi, bata da damar shiga balle ta yi magana da Senator ko zai taimaka mata.

Senator da ɓacin rai ya fita daga motar ya shiga ciki, a sama ya samu Mum a zaune ya kalle ta ya ce, "kin san su waye a wajan estate ɗin nan?." Mum ta ce, "su waye?."

"Wai yan uwan Tiger ne suka zo son ganina." Mum ta ce, "yan uwansa? Kenan daman da sanin su yazo nan neman aure?."

Dad ya ce, "bara na yi waya gabaɗaya a kama su." Mum ta ce, "A'a Dear, kar ka saka a kama su."

"Meyasa?" Ya tambaya yana kallon ta. Mum ta ce, "ka shigo dasu, ka shigo dasu mu yi musu warning, sannan mu saka su je su karya asiri da Tiger ya yiwa yarmu." Dad ya kalle ta da mamaki ya ce, "hakan ya yi?."

"Hakan ya yi mana, ki shigo dasu muyi amfani dasu a karya asirin da ya yi mata. Babbar dama muka samu da zamu tura su gida su je su karya asirin ko dan hankalin Narma ya dawo jikinta."Waya Dad ya ɗauka ya kira masu gadin ya yi musu magana yana kashewa.

Su Didi suna tsaye aka ƙaraso inda suke, su sun ɗauka ma laifi suka yi. Bashir ya ce, "ya dai? Nan ma korar mu za a yi ne? Na ga nan kan titi ne ko?." Kallon su ya yi ya ce, "ku ku zauna a nan, ke mu je Sen yana kiran ki." Bashir ya kalli Didi da ta zabura zata bisu ya ce, "Didi bai kamata ki je ke kaɗai ba." Didi ta ce, "kar ku damu, bara naje na dawo." Tare suka tafi zuwa gidan aka raka ta har bakin falon gidan sannan ya dawo wanda ya rakata.

Da sallama Didi ta shiga amma bata ga kowa ba, falon shiru sai sanyi da ƙhamshi da yake tashi a cikin sa. Didi bata tsaya ƙare masa kallo ba dan ba abinda tazo yi ba kenan. Tana tsaye a falon aka turo aka shiga da ita ciki, a wani falon ta same su a zaune su biyu suna kallon mai shigowa. A sanyaye Didi take shiga, ganin su kawai ya sanyaya mata jiki,

ba kamar kallon wulaƙancin da suke binta dashi duk sai ta sare guiwar ta tayi sanyi sosai.

A kan carpet ta zauna a sanyaye ta ce, "Ina yini." Mum ta ce, "ba gaisuwarki muka kira ki mu ji ba, ke ce Yayar ta sa?." Didi ta ɗaga kai alamun Dad ya ce, "Ina iyayen ku?." Didi ta ce, "sun jima da rasuwa."

"Na sani, na san hiv ce ta kashe babar ku, sannan baban ku ya mutu ta sanadin shan taba har huhunsa ya lalace."

Didi ta sunkuyar da kai idonta yana cikowa da hawaye. Dad ya yi tsaki ya ce, "ɗan uwanki ya yiwa yata asiri mai ƙarfi kin san da hakan?." Didi ta girgiza kai ta ce, "Ban sani ba." Dad ya ce, "to na faɗa miki yanzu, ya yi mata asirin da ta kusa fita daga hankalinta. Dalilin da ya saka nace ki zo shine, ki je duk inda ki ka san ya binne asirin nan ki tona shi a karya, in ba haka baza ki sake ganin sa ba har abada."

Hawaye ya sakko daga idanun Didi, ta yi sauri ta share a sanyaye ta ce, "don Allah ku yi haƙuri ku barshi ya dawo gida, nayi alƙawarin bazai sake kallon koda hoton yʻarku ba balle har wata magana ta shiga tsakanin su. Omar yana jin maganta sosai, in na ce ya yi zai yi, haka in nace ya bari zai bari. don Allah, don Annabi ka yi haƙuri ka sassautawa Omar. Maraya ne bashi da uwa bashi da uba, nima shi kaɗai ne dani, don Allah ka taimaka min."

Mum ta ce, "ya san shi marayan ne ya yiwa yʻar mu asirin da shiga wani hali mara daɗi? Ya san da bashi da kowa ya kawo kansa gidan nan cikin gadara da nuna iko?. A wajan mu bai wuce sauro ba, yadda zamu kashe sauro mu kwana lafiya haka zamu kashe shi ba tare da kowa ya sani ba. Matuƙar kina son sake ganinsa a duniya dole ki san yadda zaki yi a karya asirin nan, in ba haka ba wallahi sai mun ɓatar da shi a duniya, sai ya bar rayuwa a duniya, ke dashi sai dai a lahira wallahi!."

Didi murya na rawa ta ce, "wallahi bai yi mata komai ba, wallahi bai yi mata asiri ba. Itace ta fara cewa tana sonsa, ita ce tazo har gida ta....." Cikin tsawa mai ƙarfi Dad ya ce, "ki mana shiru! Jahila mara hankali. Mu za ki kalla kina cewa ba asiri ya yi mata ba? To me ya yi mata? Ko kina so ki ce soyayyarsa ce zata iya shiga zuciyar yʻarmu?. Waye shi da yʻar mu zata so shi? Na ce waye shi!?."

Didi ta sunkuyar da kai tana hawayen baƙin ciki da damuwa. Mum ta ce, "wai har tana ƙoƙarin faɗa mana ita taje har gida ta ce tana sonsa, to in ba asiri ya yi mata ba taya haka zai faru?. Dear ka san abinda zaka yi wannan matar ta bar falon nan kafin raina ya ɓaci na saka a yi mata dukan tsiya." Ya kalli Didi ya ce, "kina jina? Ki tabbatar da kin saka ya karya asirin da ya yi mata, in ba haka ba kema bazan bar ki ba wallahi, sai na saka miki baƙin ciki a zuciyarki." Didi murya na rawa matuƙa ta ce, "to a ina zan ganshi balle ya karya asirin?."

Mum ta kalli Dad ta ce, "in dai yana kusa a haɗata dashi su yi magana, ya tabbatar ya karya asirin in ba haka ba wallahi bazai fita ba." Dad ya kalle ta ya ce, "Ina zuwa" ya faɗa yana ɗaukar waya yana dannawa kafin ya kara a kunne ya yi magana. Babu wanda ya sake yi mata magana har wani ya shigo falon da girmamawa. Dad ya kalle shi ya ce, "gata nan, ku je tare." Mum ta miƙe tsaye ta ce, "nima zan je."

Dad ya ce, "me zaki je ki yi?."

"Ina so nayi magana dashi ne."

"Akan me?."

"Ni dai ina so naje nayi magana dashi." Dad ya miƙe shima ya ce, "mu je tare gabaɗaga." Mum shiga ciki kawai tayi ta ɗauko mayafi suka shiga bayan wata mota, ita kuma Didi suka ce ta shiga motar Escort ɗin Dad. Didi a motar ta yiwa Bashir text ta faɗa masa.

Tafiya suka yi mai ɗan nisa kafin su ƙaraso wani babban waje aka yi parking da motar suka fito suka shiga. A wani babban waje suka zauna Didi dai tana tsaye bata iya zama ba buri take ta ga Omar. Kallon inda aka buɗe ƙofa tayi ta ga Omar ɗinta ya shigo cikin yanayi mara daɗin gani.

Kayan jikinsa gabadaya sun canja kala fuskarsa ta cika da gashi haka kansa ya taru da gashi, da ganin yadda yake tafiya ka san ya wahala ko yana kan wahala, idanunsa sai lumshewa suke yi saboda wahalar da take ɗawainiya da gangar jikisa. Kai kana ganin sa ka san bayan wahala ma akwai yunwa a tare dashi, ya canja gabaɗaya kamar ba shi ba.

Kayan jikinsa sun yage kaɗan musamman rigar jikinsa, ana iya hango fatar jikinsa da ta koma wata kala ga shatin ciwo da alama dai duka ake masa da bulalai bama bulala ba. Kuka Didi ta fashe dashi ta ƙarasa inda yake ta ce, "Omar!." Jin muryar Didi sai ya ɗaga idanunsa da suka yi masa nauyi ya kalle ta, a iya laɓɓansa ta ga ya furta sunanta hakan ya saka ta rungume shi tana kuka sosai.

Ɗagowa tayi tana kallon sa ganin yadda ya dake kamar ba dashi ne yake cikin wannan yanayi ba, fuskarsa har ɗan washewa tayi saboda ganin rabin ransa. Muryarsa a ɗan dashe kaɗan ya ce, "Didi me ki ka zo yi nan? Kina lafiya? Babu abinda ya same ki?" Ya faɗa yana kallon fuskarta.

"Omar haka ka koma?." Murmushin ƙarfin hali ya yi mata ya lumshe ido ya buɗe ya ce, "Ina lafiya kar ki damu. Waye ya kawo ki nan? Ina fatan ba ke kaɗai ba ce ba ko?. Babu abinda yake damun ki?."

Mum ta miƙe tana hararar Omar bayan ta sauke facemask ɗin da ta saka a hanci ta ce, "bazan iya zama mai yawa tare dashi ba, gabaɗaya dashi da wajan abin ƙyama ne" ta faɗa tana yatsine fuska tana kawar da kai. Ta kalli Dad ta ce, "Dear ka yi abinda ya kawo mu kawai." Kallon Omar Senator ya yi ya ce, "ga Yayarka nan tazo

bada haƙuri dan a fitar da kai, ka faɗa mata inda ka binne asirin da ka yiwa Narma ta je ta tona shi a karya, daga nan sai nayi tunani in zan iya yafe maka."

Kallon sa yake yi dan saboda shi ya dake kamar yana lafoya duk da abinda yake ji a jikinsa. Murmushin rainin hankali yayi ya ce, "yʼarka ai bata kai matsayin da zan yi mata asiri ba." Mum ta kalle shi ta ce, "ai ba jayayya aka zo yi da kai ba, ga Yayarka nan in baka karya asirin nan ba wallahi akanta komai zai ƙare. Na lura itace weekneess point ɗinka, to wallahi duk azabtar da kai ɗin da ake yi ita sai mun ninka mata."

Didi ya kalla da yaji ta riƙe hannunsa alamun kar yace komai, yaga ta marairaice tana hawaye sai ya ce, "Didi baki ji abinda suke faɗa ba ne? Ni wanne asiri na yiwa yʼatsu? Har ta kai matsayin da zan yi mata asiri ne?. Wallahi bata kai ba, irin ta dubu basu isa nayi musu asiri dan su soni ba. Sai dai in yʼarsu ce tayi min asiri amma ba dai ni nayi mata ba."

Kulle ido tayi ta buɗe jin ya riga dai ya faɗi abinda bata so ya faɗa ɗin ta kalli Sen ta ce, "Kuyi haƙuri don Allah, tun farko na faɗa daman babu abinda ya yi mata, amma tunda kun dage a kan hakan zan koma duk yadda zan yi zan yi wajan an karya asirin."

"Didi ban san ki da ƙarya ba, dan kare ni kar ki faɗi abinda bazai faru ba. Babu asirin da na yi musu balle a karya shi. Ba yʼarsu ba, ko su ɗin ne da kansu basu isa nayi musu asiri ba wallahi, zuciyar Omar ta wuce wannan mataki, babu wata halitta da zan iya yiwa asiri a duniya. Yʼarsu ɗin banza da wofi, wacce ita da har ni Omar zan yi mata asiri?."

Mum ta fusata sosai ta kalli Dad ta ce, "ka ga rainin da ka jawo mana, anya escort ɗin na suna akin su kuwa? Tunda har yake tsaye akan ƙafarsa wallahi bai sha wahala ba" ta juyo ta kalli Didi ta ce, "kince yana jin maganar ki gashi kema ya nuna mana jahilcin nasa bai bar ki ba. Ki ja masa kunne a tabbatar an karya asirin nan in ba haka ba wallahi zaku yi dana sani gabaɗayan ku."

Didi zata yi magana Omar ya rigata ya ce, "Jahili shine wanda bai san abinda yake yi ba, ni na san abinda nake yi kuma ban yi dana sanin zuwa gidan ku a matsayin mai neman auren yʼarku ba. Ina alfahari da hakan ko babu komai zan shiga cikin

tarihin rayuwarku, har abada baza ku manta da mai suna Omar yazo har falo ya ce yana son ƴarku ba. Jahilin da ku ka raina shine soyayyarsa ta hargitsa ƴarku har kuke tunanin an yi mata asiri. Ƙarfin tasirin Omar kenan ku ka gani, ƴar da kuke ji da ita zuciyarta ta gama narkewa a soyayyar wanda ku ka raina ku ke kallon sa ƙasƙantacce. Sai dai a yanzu ta makara, lokacinta ya wuce, domin in Omar ya yi gaba baya juyawa baya, Omar in ya tsallaka baya sake tsallakowa, Omar in ya tafi baya dawowa. Ku bata haƙuri, ba wai na ƙita bane kawai akwai abinda ya fita mahimmaci a gabana yanzu. Ku yi mata addu'a Allah ya bata ikon jure rashina. Na san zaku sha matuƙar wahala kafin ta jure, dan nima tasha wahala kafin na fara ko da ɗaukar kiran wayarta."

Sen ya fusata da jin kalaman Omar, ransa ya ɓaci sosai ya ce, "ƙarya ka ke yi, ƴata ta wuce ta fara soyayya da irin ka wallahi, sai dai aikin asiri. Kuma wallahi ka yi gaggawar sanar da ƴar uwarka inda ka ɓoye asirin, in ba haka ba kana gab da aikata aikin dana sani." Zai yi magana Didi ta riga shi ta ce, "Ku yi haƙuri don Allah, ku bani shi mu tafi zamu tattauna dashi zan yi iya ƙoƙarina wajan ganin an karya asirin."

Omar ya kalle ta da mamaki ya ce, "ki daina faɗar wannan maganar fa, babu abinda na aikata kin sani. Ita tazo har gida ta zube a gabanki tana roƙonki ki saka na sota, na ji tausayinta saboda raunin da take tare dashi har naji a raina zan iya taimaka mata na saurarenta..." ya faɗa yana kallon su Mum da suke kallon sa.

Ya sake kallon Didi ya ce, "Dan na taimaka mata na bata aron kaɗan daga cikin lokacina sai ya zama nayi mata asiri?. Didi kar ki damu dani, ai ba yau na fara shan wahala ba, ba yau aka fara dukana ba. Wannan kaɗan ne ba mai yawa ba, kar ki da wannan komai zai wuce. Amma na ƙara ilimi, na kuma ƙara sanin meye duniya, na kuma gasgata zancen da ki ke yawan faɗa min a kullum. Ko a nan zan gama rayuwata zan tabbatar miki da Omar ɗin da kika sani a baya yana nan, hatta shi Senator bazai manta da Tiger yana da rai ba."

Mum ta kalli Senator cikin ɓacin rai bata sake cewa komai ba ta fice shima bai yi magana ba ya fita. Omar ya yi murmushi dan so yake ya cusa musu haushi a zuciyarsu kuma ya yi, ya kalli Didi ya ce, "kar ki damu, babu abinda zai same ni zan kuma fito na dawo na zauna tare dake in sha Allah. Ki je kawai."

"Wahalar da kai suke yi ko Omar? Naga nan bai yi kama da gidan yari ba, Ina ne nan?."

"Ai daman ba prison suka kai ni ba, wani gida suka fara kaini kafin su kawo ni nan. Duk ƙarfin mulkin da suke ji dashi basu isa su kaini prison ba tare da laifi ba, in nayi laifin ma sai dai kotu ta tura ni prison ba dai su ba. Amma zasu iya yi min sharri in suka ga dama, ban san meyasa basu aikata ba har yanzu. Ki kwantar da hankalinki Omar ɗinki zai dawo." Hawaye ya share mata da hannayensa da suka yi duhu ga farce ya taru.

Didi kuka take yi sosai ta ce, "Duk yadda zanyi dan ganin na kuɓutar da kai zan yi Omar."

"Kar ki wahalar da kan ki Didi, ki kwantar da hankalin ki. Tare da wa ku ka zo?."

"Bashir da Tukur, Hajja ce ta bada mota aka kawo mu. Omar murmushin ƙarfin hali ya yi ya ce, "shikenan ki je kawai." Didi ta ce, "Bana so na barka a nan Omar." Ƙarfin hali yake yi kawai yana yi mata magana saboda kar ya sakata a damuwa. Daƙyar ya ce, "Ki je Didi." Fita tayi tana kallon sa shima a lokacin suka koma ta inda suka fito.

Didi da ta fito bata ga motar da suka zo ba hankalinta ya tashi gashi bata san gari ba, ta fito bakin titi ga taxi nan tana yawo amma bata san Ina zata ce zata je ba. Allah ya taimake ta da waya a tare da ita ta kira Bashir ta faɗa masa, ta tura masa location ta whatsapp yadda zasu fi ganewa. Da yake driver Hajja ya san Abuja ba jimawa ya ƙaraso suka ɗauki Didi zuwa inda suka sauka.

KRB2P005

Arewabooks@nanahaleema11.

Didi bata ɓoyewa su Bashir abinda ake ciki ba ta faɗa musu yadda suka yi dasu, gabaɗaya ta canja yanayin damuwa ta sake mamaye ta ba kamar in ta tuna halin da ta ga ƙanin nata sai zuciyarta karye ta fashe da kukan tausayinsa. Washe gari da wuri suka ɗauki hanyar Kano, da suka shiga cikin gari kai tsaye gidan Hajja suka shiga suka same ta a zaune da hijjabi ga kuma babban mutum a kan carpet a zaune yana gaisheta da matuƙar girmamawa.

A sanyaye Didi ta shiga falon Hajja ta bita da kallo haka Salma ma da take zaune. Abiy ya kalli wacce ta shigo, Didi ganin Abiy a zaune sai Didi ta gaishe shi a sanyaye

ya amsa Hajja ta ce, “Aisha ce, Aisha maƙociyarmu, Yayar Omar.” Nan da nan fuskar Abiy ta washe zuwa fara’a ya ce, “Allah sarki, na gane ta yanzu. Ina Omar ɗin? Yana nan lafiya?.”

Hajja ta ce, “ba lafiya ba gaskiya, wata matsala ce ta saka har aka kama Omar ɗin a Abuja.” Abiy ya ce, “Subahanallah! A Abuja kuma aka kama shi?.” Hajja ta ce, “ƙwarai kuwa, hanyar da za a fito dashi ma muke so saboda bashi da laifin komai aka kama shi.” Abiy ya girgiza kai zai yi magana aka kira shi a waya ya kalli wayar ganin kiran mai mahimmaci ne sai ya kalli Hajja ya ce, “Hajja zan koma ana kirana, Amma zan saka a bincika maganar Omar ɗin in sha Allah.”

Hajja ta ce, “Allah ya yi albarka, na gode sosai Allah ya saka da alkhairi.” Da amin ya amsa ya ajjiye mata kuɗi kamar ko yaushe, ya bawa Salma da Didi kafin ya tashi ya fita.

Kawai sai Didi ta fashe da kuka mai sauti Hajja ta riƙota ta ce, “Don Allah ki bar kuka ki huta tukunna sai mu yi magana. Jikinki ma ya yi zafi sosai Aisha da alama zazzaɓi yana damunki.” Salma ta ce, “Da gajiya ma a zazzaɓin da yake damunta Hajja, ta yi wanka ta sha magani ta kwanta zata ji daɗi.” Hajja ta ce, “kin ji abinda likita ta ce, don Allah ki yi shiru ki daina wannan kukan. Ba ki ji mahaifin Nayla ya ce zai san abinda zai yi ba? Na san zai yi, kuma daƙyar in bai san shi Sanata ɗin ba.”

“Hajja bazai amince ba, baza su bar Omar ba Hajja. Sun ce ya yiwa ɣarsu asiri shiyasa take sonsa har ta fita daga hayyacinta. Wallahi Hajja Omar bai nata komai ba, har gida tazo tana yi min kuka na saka Omar ya sota. Kuskuren Omar da ya bari ya fara sonta, kuskuren Omaar da ya je ne gidan Sen. Hajja kin ga yadda suka mayar min da Omaar? Kin ga yadda ya koma Hajja….?” Ta faɗa tana jan kalmar ƙarshe tana kuka sosai.

Hajja ta ce, “ki yi haƙuri komai zai wuce in sha Allah, ki daina tayar da hankalin ki kin ji.” Didi ta ce, “shi yake jawowa kan shi Hajja, a gaban su a jiya baki ji irin maganar da ya dinga yi ba, sam Omar baya riƙe maraicinsa, baya tuna matsayin da yake dashi. Na rasa wanne rashin tsoro ne haka da Omar bashi dashi, lamarinsa yana bani tsoro sosai. Kina ganinsa Hajja kin san yana cikin azaba, amma ya dake yana faɗa musu maganganu masu ciwo.” Hajja ta ce, “ni maganar ce bana so ki yi, ki je ki yi wanka ki huta kin ji?.” Ba dan ta so ba Hajja ta saka ta shan tea sannan tayi wanka ta sha magani ta kwanta ba dan tana jin bacci ba. Haka Didi ta kwana da

zazzaɓi mai zafin gaske, sai da Salma ta yi mata allura sannan ta iya bacci a safiyar ranar jum’a.

Nayla ta shigo garin Kano a ranar ana gab da shiga masallaci domin yin sallar juma’a, gidan su na Kano wanda su Abiy suka sauka ta wuce ta ajjiye kayanta tayi wanka ko hutawa bata yi ba ta fito falo. Da Mama ta haɗu ita da Jidda a zaune ta kalli Mama ta ce, “Mama zan je gidan Hajja sai zuwa dare zan dawo tunda event ɗin yau sai dare.” Mama ta ce, “Baki huta ba fa Nayla, zuwan ki kenan kuma ki tafi gidan Hajja?.”

“Bana so lokacin masallaci ya yi a rufe hanya ban tafi bane shiyasa.”

“Baza ki yi makeup ɗin ba?.”

“Bazan yi ba gaskiya.” Twiny ta ce, “bara nazo na raka ki gidan Hajjan.”

A motar Twiny suka tafi gidan Hajja lokacin ana ta sallah a masallaci. Bata ɗauka zata tarar da Hajja ba dan tasan zuwa sallah duk sati da ita ake yi a masallaci, amma sai ta tarar tana nan ta tasa Didi a gaba tana ta rarrashinta. Shigar su falon ya saka Salma ta ce, “A’a Nayla, saukar yaushe?.” Duk sai suka kalle ta har Hajja, Hajja ta bita da kallo ganin ta yi wani iri itama kamar ba ita ba.

Fuskar Hajja ta washe ganin jikarta ta da kuma ɣar uwarta. Ta ce, “Hauwa’u da Jidda, sannan ku da zuwa.” Twiny tayi dariya ta ce, “Hajiya Hajja, barka da rana.” Hajja ta amsa fuska a sake tana tambayarta Maman ta Jidda ta amsa da kowa yana lafiya. Da Didi suka gaisa ganin bata da lafiya sai tayi mata sannu. Didi ta kalli Nayla ta ce, “ƙanwata Nayla ya kika tsaya?.”

Nayla ta ce, “Hajja Didi bata da lafiya haka shine ba a faɗa min ba?.” Hajja ta ce, “kema ai baki da lafiyar, kalli yadda ki ka koma.” Share batun Hajja tayi ta dawo kusa da Didi ta ce, “Didi sannu, me ya same ki haka?.” Didi tayi murmushi ta ce, “Zazzaɓi ne kawai Nayla, bayan shi babu komai.”

“Sannu Didi, Allah ya baki lafiya. Gabaɗaya kin rame.”

“Amin Nayla. Kema kin rame, na faɗa miki ki daina cewa zaki rage ƙiba, baki fa ƙibar kirki ki ce zaki rage? wallahi kin fi kyau da jikinki.” Nayla tayi ajiyar zuciya kafin ta kalli Hajja da take kallon ta sai tayi murmushi ta ce,”Hajiya Hajjata, na yi kewarki.”

Hajja ta ce, “nima nayi kewarki Nayla. Amma me yake damunki haka?.” Nayla ta ce, “Hajja na fara aiki fa, in na fita tun safe sai yamma nake dawowa, kin san ba wani abincin kirki na iya ci a waje ba shiyasa na koma haka.” Hajja ta tace, “Mahaifinki ya faɗa min ai zancen aurenki ake yi, yanzu haka ya baki lokaci ki fitar da gwani. Ni na san a cikin gwanayen naki babu Abbas ko?.” Gabanta ya faɗi sosai ta kalli Hajja bayan ta ɓoye damuwarta ta ce, “Hajja ni na barwa Allah zaɓi, duk wanda ya zaɓa min shine daidai da rayuwata. In Yaya Abbas ne Ina maraba dashi.”

Hajja ta ce, “Gaskiya ne. Allah ya zaɓa abinda yafi alkhairi. Ni daman so nake ki yi auren ai, an gama karatu aikin me za a tsaya yi? Me kika nema kika rasa?.” Nayla tayi murmushi kawai kafin ta kalli Didi da take kallon ta. Didi ta ce, “Ashe ƙanwar tawa ta kusa aure babu labari.” Murmushi tayi kawai bata ce komai ba kafin ta ce, “Yau baki yi abincin sadaka bane?.” Didi ta ce, “bani da lafiyar yi ne, da Omar ma yana nan sai ya yi ni bani da wannan ƙarfin gabaɗaya” tana faɗar haka sai hawaye ya sakko mata.

Nayla daman zancen Omar ɗin take so ayi sai ta ce, “Didi meye na kuka?.” Didi ta ce, “Nayla baki san an kama Omar ba?.” Nayla tayi ajiyar zuciya ta kalli Salma kafin ta kalli Didi ta ce, “Salma ta bani labari.”

“To na je har Abuja naga halin da yake ciki Nayla, Omar yana cikin wahala da azabtarwa, dauriya da rashin son sani a damuwa ne ya saka shi ya dake har yake yi min magana kamar ko yaushe. Suna cutar min da Omar kawai dan suna taƙama da mulki baza a iya ja dasu ba, in ba dan haka ba meye laifin Omar? Me ya yi da za a kama shi a ɗaure ba tare da ya yi laifin komai ba?. Laifin Omar ɗaya da yaje gidan, amma da ya je ai ba kisan kai ya je yi ba, ba kuma wani laifi ya aikata musu ba. Kawai saboda bai kai matsayin da suke kai ba, a gare su ƙasƙanci ne yarsu ta so Omar. Yanzu zancen asiri suke yi, sun ce asiri ya yi mata take sonsa, ko nazo na karya asirin ko kuma bazan sake ganinsa ba har abada!…..Kashe Omar suke son yi, kashe shi suke son yi kawai!” Ta faɗa da rauni tana hawaye mai taɓa zuciya.

Nayla kuka take yi sosai wanda ya bawa kowa mamaki, sun santa da tausayi sosai kuma tsaf labarin zai iya saka ta kuka. Amma yadda take kuka da zuciyarta da gangar jikinta zaka tabbatar da ba iya kukan tausayi take yi ba akwai wani abun a cikin zuciyarta. Hajja a sanyaye ta ce, “Aisha na ce ki yi haƙuri komai zai zo ƙarshe in sha Allah.” Didi ta ce, “Hajja wallahi mahaifiyar Narma so take a kashe Omaar, yanayin kalamanta kashe shi suke son yi kawai. Sun san in sun kashe shi sun kashe banza tunda bashi da gata, bashi da wani gatan da za a neme shi shiyasa.”

Hajja ta ce, “su Baba Adamu dasu Kawu duk babu wanda zai samu hanyar magana da Sanata?.” Didi ta ce, “Tunda har Daddyn Salma bai samu ba bana tunanin zasu samu. Kuma ni ko faɗa musu ma ban yi ba, ban saba kai damuwata gare su ba na saba ni da Omaar mu ke warware ko meye in ya tunkaro mu. Ban sani ba ko sun ji a gari amma ni ban sanar musu da komai ba.” Hajja ta ce, “ai ya kamata ace sun sani Aisha, iyayen Omar ne fa, ya kamata a sanar dasu ko da addu’a su taya mu.”

Didi ta ce, “Hajja yanzu bana cikin wannan nutsuwar, hankalina baya jikina wallahi.”

Nayla dai kuka take yi har sautin nata kukan yafi na Didi fita, Didi ta kalle ta cikin rauni tace, “ki bar Kuka Nayla, ni ban faɗa miki dan ki yi kuka ba. Ki share hawayenki.” Nayla ta kalli Didi cikin muryar kuka ta ce, “Didi ki yi haƙuri in sha Allah zan yi ko meye ganin na dawo dashi, zan yi duk abinda zanyi dan ganin ya bar hannunsu.”

Didi ta murmusa cikin tsokana da son kawar da damuwa ta ce, “na ɗauka zaki barshi a can kawai, kin manta tsorataki yake yi?.” Nayla bata yi murmushi ba sai ma hawayen da ya sake sakkowa daga idonta ta ce, “Didi ba maganar wasa nake yi ba, zan yi ko meye ganin na dawo da shi.”

Didi tayi murmushi ta ce, “to Nayla. Na gode sosai Allah ya bar zumunci.” Idanu Nayla ta goge ta kulle idanun nata, ita kaɗai ta san raɗaɗin da take ji akan rashin Omar, ita kaɗai ta san azabar da zuciyarta take mata akan Omar. Dole ta san abinda zata yi ta fito da Omar, ko meye shi kuwa zata aikata in dai zai dawo. Zata iya sadaukar da komai dan Omar ya dawo, zata iya rasa komai indai Omar zai fito ta amince.

Ganin tayi shiru sai kowa ya yi shiru Salma da Jidda dai kallon Nayla kawai suke yi cikin tuhuma. Nayla sai ta miƙe ta shiga ɗaki tayi alwala tayi sallar azahar kafin ta dawo falon. Abinci ta tarar suna ci, Hajja ta kalle ta tace, “baza ki ci abincin ba?.” Nayla ta ce, “bana jin yunwa, kaina ciwo yake yi.” Jidda ta ce, “dole kan ki ya yi ciwo, kin zo daga Kaduna ko hutawa baki yi ba kina taho nan, ga kukan da ki ka yi gashi ko abinci baki ci ba, ai dole ki yi ciwon kai.” Hajja ta ce, “Hauwa’u me yasa haka?.”

Kallon Jidda ta yi tace, “Twiny mu je gida” ta faɗa tana ɗaukar mayafinta da yake wajan. Jidda ta ce, “ki ka ce sai anjima zamu tafi.”

“Na fasa, mu tafi yanzu. Salma zaki je bikin ko baza ki ba?.”

“Zan je mana.” Nayla ta ce, “ku zo mu tafi, Hajja sai gobe” abinda ta ce kenan ta fita da hanzari bayan ta ɗauki key ɗin motar Jidda ta fita dashi.

A mazaunin driver ta zauna ganin haka sai suka shiga motar ta ja motar da ƙarfin gaske suka tafi. Gudu take yi sosai ga yanayin gari na juma’a a cushe garin yake da mutane amma haka take gudu kamar zasu bar gari burinta kawai ta je gida. Jidda da take a zaune a gaba ta kalle ta ta ce, “Twiny wai lafiyar ki kuwa? Wannan gudun da ki ke yi na meye?.”

Bata yi magana ba Salma da take baya ta ce, “malama magana ake miki ki rage gudu Ina zamu je? Sai gudu ki ke yi kamar zaki tashi sama.” Daidai nan suka ƙaraso gate ɗin gidan ta dinga danna horn dashi ƙarfi, mai gadi ya buɗe da gaggawa ta shiga da motar ganin motar Abiy tana nan ko parking daidai bata yi ba ta fita daga motar da sauri.

Jidda ta kalli Salma ta ce, “lafiyar ta kuwa?.” Salma tayi tsaki ta ce, “ƙiris ya rage bata saka mun baƙunci lahira ba, ko aure ban yi ba zata kashe ni.” Jidda tayi dariya suka shiga cikin gidan.

A zaune suka same ta a gaban Abiy da yake waya suma suka zauna saboda ya kammala. Kashe wayar ya yi ya kalli Nayla ya ce, "Mamana lafiya ki ke kuwa? Meye ya same ki haka fuskarki tayi ja haka?." Nayla ta ce, "Abiy ai ka san Didi ko?." Abiy ya ce, "Wacece Didi kuma?."

"Maƙociyar Hajja Yayar...." Kafin ta ƙarasa ya ce, "Oh Yayar ɗan daban nan ko? Na gane ta, da Aisha na santa ni ba wani Didi ba. Mutuwa tayi?."

Nayla gaban taya buga dum jin da sunan da Abiy ya kira Omar dashi, amma bata nuna ba ta ce, "da ranta." Abiy ya ce, "to lafiya ki ka shigo a firgice haka?." Jidda ta ce, "Haka ta dinga gudu damu a titi Abiy, gari ya cushe mutane an dawo daga masallacin juma'a amma bata daina ba, ƙiris ya rage bamu yi hatsari ba." Abiy ya kalli Jidda ya ce, "Wai daman ba Jawad ne ya shigo da mota a guje ba itace?."

"Wallahi itace" ta bashi amsa tana kallon Nayla.

Ya kalli Nayla a nutse ya ce, "Me ya faru haka?." Nayla ta ce, "Tausayin Didi nake ji Abiy, an kama mata ƙaninta sai kuka take yi har da zazzaɓi. Don Allah Abiy ka taimaka a fito dashi don Allah." Abiy ya bita da kallo cikim mamaki ya ce, "akan wannan ne kika kusa kashe kanki da yɾan uwanki?."

"Na kasa sarrafa kaina ne kawai Abiy, bana jin daɗi a zuciyata, Didi tana sona, nima ina son abinda take so." Abiy ya kalle ta a nutse ya ce, "mun yi maganar da Hajja jiya sai dai ba a bani labari duka ba aka kira ni a waya. Waye ya saka aka kama shi ɗin sannan me ya yi?."

Shiru tayi bata amsa ba ya ce, "ke nake saurare, me ya yi aka kama shi har kike so na fito dashi?. Ko wani ya kashe?." Ta girgiza kai alamun a'a ya ce, "to faɗi." Nayla ta ce, "Dama ya je gidan Sen Sagir Sani ne, shine ya saka aka kama shi."

"Me ya je yi gidan? Sata ko kuma kisan kai?." Salma ce ta bawa Abiy labarin abinda ya faru kaf har zuwan Didi wajansa. Abiy ya girgiza kai cikin mamakin ƙarfin halin Omar ya ce, "Barr Narma ya je yace yana so? Kuma yana da hankali?." Salma ta ce, "gashi nan dai akwai Abiy."

Abiy ya ce, "gaskiya dai gashi nan dai kawai, dan in har yana da hankali to tabbas shaye-shayen su na ɓata gari ya taɓa masa ƙwaƙwalwa. In ba haka ba ya ɗauki ƙafa ya je ya ce yana son yɾar Sen Sagir? Ya san waye Sen Sagir kuwa?." Suka yi shiru Abiy ya ce, "To ai ko zauna gari banza wanda bashi da komai ya je ya ce masa yana son yɾarsa dole ya ɗauki mataki balle Sen. Kuma dole ya ce asiri ya yiwa mata take sonsa. Meye abin so a tare dashi har da zata fita hankalinta haka?." Nayla dai wani irin sanyi jikinta ya yi da jin kalaman Abiy, zuciyarta na bugawa, guiwarta kamar ana dukanta saboda sagewar da tayi.

Abiy ya numfasa ya ce, "well, ya taimaki Nayla a lokacin da take buƙatar taimako, ya kuɓutar da ita daga masu sharrin fyaɗe. Ya cancanci na taimaka masa a fito dashi tunda ba wani laifi ya aikata ba. Na san Sen Sagir sosai, abokina ne sosai tare muka yi ABU Zaria. Kuma ni ne class captain a lokacin, bara mu ga" ya faɗa yana ɗaukar waya yana dubawa.

A speaker Abiy ya saka kiran daga can ɓangaren Sen yana ɗauka ya ce, "Class Captain....!." Abiy ya murmusa ya ce, “ni ɗauka baka da number ta ai.” Sen yayi dariya ya ce, “Haba ni na isa nace bani da number ka?.”

“Ka isa mana Sem, ai ka kai matsayin da ba number kowa zaka ajiiye ba.”

“Ai kai kana cikin mutane na farko a wayata.” Abiy yayi murmushi suka gaisa cikin wasa da dariya na yɑn makaranta kafin Abiy ya ce, “kwanaki nazo Abuja na karɓi offer ta yɑr wajena Nayla, naso nazo wajan ka sai kuma na sha’afa wallahi.”

Sanata ya ce, “gaskiya baka kyauta ba, duk da dai nima kwanaki na shiga Zaria naso na kira ka wallahi dare ya yi min. “

“Haka ne, komai sai Allah ya yi.”

“A wacce ma’aikata ta samu aikin?.”

“FIRS.”

“Haba Captain, me zata yi da wannan ƙaramin aikin da salary sa bai wuce 400k per month ba? Ga aiki a nan Abuja da zata samu kuɗi me zata yi da 400k kamar wata almajira?.” Abiy ya yi dariya kafin ya yi magana Sen ya ce, “ka turo ta Abuja akwai aikin da zan bata, 900k ne per month banda allowances da suke shigowa. Shima dai tayi manage kawai.”

Abiy ya yi dariya ya ce, “Senator! Ai ba dan salary take aiki ba, hakan burinta ne shiyasa kawai na bari tana yi.” Sen ya ce, “Sai ta cika burinta da abu mai kyau ba wannan ba, ka rasa aikin da zaka bata sai wannan ƙaramin aikin? Me zata yi da kuɗin da bai wuce albashin house maids ɗin gidansu ba?...Ka turo min ita kawai, zan cika mata burinta da aiki mai kyau, in kana tunanin baka so ta zauna ita kaɗai a guest house sai ta zauna a gidana wajan Narma da Najwa.”

Abiy ya ce, “A’a, barta a Kaduna kusa dani ya fi. Nayla me zata yi da kuɗi tana yarinya ƙarama?. Tana da shop fa.” Senator ya yi dariya ya ce, “Najwa ba ma Narma ko Nabil ba, itace take kula da ɓangare guda na companyna, kuma tana aiki sannan itama tana da shops. Ai yaran yanzu sai da kuɗi Captain, haka duniyar ta zama.”

Abiy ya ce, “kana Abuja ne?.” Sen ya ce, “A’a ina Kano, nazo ɗaurin aure yɑr sarkin Kano da za a yi gobe.” Abiy ya ce, “nima Ina Kano ɗin, gobe zan kuma shiga ɗaurin

auren in sha Allah.” Sen ya ce, “to ya kamata mu haɗu gabaɗayan mu, dan yawancin yɼan class ɗinmu duk suna nan goben.” Abiy ya ce, “Allah ya kaimu goben, sai mu haɗu gabaɗaya yi zumunci a samu lada.” Sen ya amsa yana dariya kafin su yi sallama Abiy ya kashe wayar.

Kallon Nayla ya yi da ta sunkuyar da kai ya ce, “Gobe zan yi masa maganar Omar ɗin, in sha Allah zai dawo.” Nayla farin ciki take ji a zuciyarta har hakan ya bayyana akan fuskarta, ta ce, “to Abiy na gode.” Abiy ya kalle ta a nutse ya ce, “ga murmushi nan kina yi, da alama dai shima kina shiri dashi sosai ko?” Ya tambaya da niyar bugun cikinta.

Sunkuyar da kai tayi ta ce, “A’a Abiy, ko magana bamu taɓa yi ba, ni saboda Yayarsa kawai nake so ya fito.” Abiy ya girgiza kai ya ce, “ko dan taimaka miki da ya yi a shekarun baya ai ya cancanci ki so ya fito. Kar ki damu komai ya ƙare.” Nayla ta yi dariya tana kallon Mama da ta zuba mata ido tana kallon ta.

Da sauri ta tashi ta shiga ɗaki Salma da Jidda suka bita. Murmushi suka samu tana yi a bayyane tana cewa, “zan zama silar fitowar Omar in sha Allah, in sha Allah zai fito. Wayyo daɗi, Allah na gode maka.” Jidda ta kalli Salma da suke kallon Nayla da mamaki, Jidda ta girgiza kai tana gasgata abinda take zargi a zuciyarta. Jidda ta ce, “Twiny ko dai Omar shine wanda ki ke so?!.”

Arewabooks@nanahaleema11.

Nayla gabanta ya faɗi sosai, ta jiyo a firgice tana kallon su dan tambayar tazo mata babu zato babu tsammani. Duk sun tsare ta da ido suna jira su ji abinda zata ce. Kallon kallo ake a tsakanin ta su, suna jiran amsarta ita kuma duk ta firgice. Salma ta ce, "tambayar ki mu ke yi Nayla, Omar ƙanin Didi shine wanda ki ke so ɗin?." Tayi ƙoƙarin dakewa da son ɓoye damuwarta ta ce, "Wacce irin magana ce wannnan? Ni ba haka bane ba."

Jidda ta ce, "to meyasa muryarki take cracking? Meyasa ki ka ji tsoron tambayar da muka yi miki?. Sannan meyasa hankalinki ya tashi a kan ance yana cikin wahala?, gudu kika dinga yi da mota sai da kika zo ki ka samu Abiy sannan hankalinki ya kwanta. Ki faɗa mana shine wanda ki ke so ɗin?. Duk alamomin soyayya ya

bayyana a yanayin ki, yadda ki ka zaƙe a kansa ya saka muna zargin shine wanda soyayyarsa take wahalar dake, ki amsa mana Nayla."

"Eh shine!" Ta faɗa a sanyaye tana zubewa a kan gado tana sake fashewa da kuka. A tare suka wara idanu Jidda ta ƙarasa inda Nayla take dan Salma tayi suman tsaye. Jidda ta zauna kusa ta da ita ta ce, "Twiny da gaske shi ki ke so?." Kai ta ɗaga tana kuka ta ce, "Shine Twiny. Ban san ya akayi hakan ta faru ba, na san dai tsoronsa nake ji amma ban ya akayi na fara sonsa ba. Nayi kuka, na yi addu'a amma na kasa cire shi daga zuciyata. Bai san ina yi ba, tunda shi Abuja ya je neman aure a gidan su wata bani ba, amma duk da haka bana jin haushinsa Twiny."

A kan kafaɗar Jidda ta ɗora kanta tana kuka sosai Jidda tana shafa kanta dan bata san ne zata ce mata ba. Salma daƙyar ta iya motsawa tazo wajan da suke ta zauna a ɗaya gefen ya zama sun saka Nayla a tsakiya kenan. Salma ta ce, "Nayla wai Omar ɗin Didi ki ke so?."

Bata iya bata amsa ba sai numfashi da take saukewa a jikin Jidda. Salma ta ce, "Innalillahi! Mun shiga uku." Nayla ta ɗago daga jikin Jidda idanunta sun jiƙe da hawaye ta ce, "shiyasa naƙi faɗa muku saboda faɗar babu amfani Salma. Babu ribar da zan samu da soyayyarsa, wahalar da ni kawai take yi wataƙila tayi ajalina. Wallahi duk samarin da Abiy yake basu damar ganina na kasa kallon kowa da fuskar so, shi kaɗai nake so, shi kaɗai zuciyata take da burin aure, shi kaɗai nake ji a raina in ban aura ba kamar bazan iya zaman aure da kowa ba, na kuma san bazan taɓa mallakarsa ba har abada."

Jidda a sanyaye ta ce, "Meyasa ki ka ce haka?." Tayi murmushi ta ce, "baki ji me Abiy ya ce bane? Ko zauna gari banza yaje yace yana neman aure a gidansa baza a bashi ba balle gidan Sen. Dame Sen ya fi Abiy Twiny? Mulki kawai ya fi Abiy, amma duk abinda ya mallaka a duniya Abiy ma ya mallaka. Kinga kenan harda gidan mu a cikin gidajen da baza'a bashi aure ba, ni daman na san aurena dashi bazai yu ba shiyasa ban sakawa zuciyata zan aure shi ba. Kuma shi bai ma san ina sonsa ba."

Salma tayi ajiyar zuciya ta ce, "gaskiya ne zancen ki Nayla, auren Omar bana hango yuwarsa a rayuwarki. Gwara mu faɗa miki gaskiya kar mu cuce ki mu yaudari zuciyarki da kalamai na ƙarya dan mu kwantar miki da hankali. Omar ba irin wanda ya cancanci a bashi aure bane, sam ba tsarin auren ki bane."

"Na sani Salma. In ba dan ɗabi'arsa ba ni zan iya zama dashi, ban damu da bashi da kuɗi ko bashi da wani abu ba. To ɗabi'a sa baza ta taɓa sakawa Abiy ya amince ba, Inda Abiy zai amince ni zan iya zama dashi a haka, koda zai dinga bani tsoro kamar yadda yake yi ko yaushe na shirya Salma...." ta sake faɗa a sanyaye hawaye na sakkowa. Jidda ta kalle ta da kulawa ta ce, "kuma kin ce bai ma san kina sonsa ba ko?."

"Bai sani ba, kuma bana fatan ya sani ɗin. Domin Didi ta faɗar min kalar wulaƙancin da ya yiwa Narma a lokacin da ta je gidan su ta ce tana sonsa. Daƙyar ta iya samun kansa har ya amince mata, jin kunnena naji yana waya yana yi mata faɗa kamar ba wacce yake so ba. Wataƙila soyayyarsa kashe ni zata yi, dan wallahil azim ina matuƙar son Omar, Ina matuƙar ƙaunarsa, ina yi masa ƙaunar da ban taɓa yiwa wata halitta a duniya ba sai shi. Matuƙar dauriya nake yi, juriya da haƙuri da jajircewa nake yi nake iya sarrafa zuciyata akansa. Amma haƙuri na ya fara ƙarewa, gab nake da karaya..." ta faɗa tana kuka sosai.

Salma ta rungume ta tana kuka itama cikin tausayin yar uwarta. Jidda a bayan Nayla ta ɗora hanunta cikin tausayin Nayla, dan yanda Naylan take yin maganar zai baka tabbacin daga zuciyarta maganar take fitowa. Sun jima a haka ko wacce na kuka kafin Nayla ta tsayar da kukan ta ce, "Abiy ya bani lokaci na fitar da wanda nake so a cikin mutune huɗu. Wallahi bana son su duka, bana tunanin zan iya zaman aure da ɗaya daga cikin su, ko na zauna zuciyata tana ga Omar ba ga wanda na aura ba. Ya zanyi? Ku faɗa min abinda zan yi na daina sonsa don Allah!" Ta faɗa da rauni wanda ya saka su Jidda sake fashewa da kuka.

Duka kuka suke yi daƙyar Salma ta iya dakatawa ta ce, "Addu'a zaki yi Nayla, addu'a zamu dage da yi Allah ya kawo mana mafita." Nayla ta ce, "Ina addu'a Salma, Ina yin addu'a babu dare babu rana. Wallahi zuwan mu umra ban san adadin addu'ar da nayi akan lamarin nan ba, kuka na ke yiwa Allah Ina faɗa masa ya cire min son Omar daga zuciyata amma soyayyar taƙi fita. In ina kuka a cikin sujjada ina faɗawa Allah damuwata sai na yi awa ɗaya a haka ban san nayi ba. In aka cigaba da haka zan mutu ne kawai, dan na san bazan same shi a matsayin miji ba mutuwar itace hutu a gare ni."

Jidda ta ce, "kar ki sare, ki cigaba da addu'a Allah zai miki magani Nayla. In kika roƙa yau Allah bai baki ba ki ƙara roƙa gobe, yana ji kuma yana gani, shi ya ƙaddara miki kuma shi ya nufe ki da fara son Omar. Allah ya san damuwarki amma yace ki

roƙe shi zai yaye miki, kar ki sare Nayla, kar guiwarki ta yi sanyi akan addu'a, ki cigaba kar ki tsaya. Ki yi haƙuri." Basu hanata kuka ba dan ya cancanci tayi kukan, zuciyarta ta yaudare ta da ta fara son wanda auren ta dashi bazai taɓa yuwa ba. Shiyasa suka barta tayi kukan son ranta ko dan taji daɗi a zuciyarta. Ai kam ta kwashe sama da mintina ashirin tana kuka, zuwa lokacin kanta ya yi nauyi zazzaɓi ya rufe ta ruf.

Salma ce ta kwantar da ita ta tashi ta samo towel a banɗaki ta jiƙa shi da ruwan sanyi tana goge mata fuska da wuyanta. Rarrashin ta suka dinga yi har ta daina kukan Salma ta takura mata ta sha magani suna zaune a gefenta. A hankali kuma sai tayi bacci su dai kallon ta suke yi cikin tausayi.

Salma da Jidda fita suka yi zuwa harabar gidan dan su tattauna abinda ya kamata su yi. Salma ta ce, "Zuciyar Nayla bata yi mata adalci ba da ta fara son Omar Jidda, gashi bai ma san tana yi ba, sannan ko ni bazan goyi bayan ta aure shi ba duk da son da take masa."

Jidda ta ce, "yanzu meye abin yi? Wanne abu ki ke ganin zamu yi da zai taimaka mata?. Tana cikin halin azabar so da raɗaɗi mai ciwo, ya ki ke ganin zamu yi?."

"Addu'a kawai zamu taya ta Jidda, to in ba addu'ar ba me zamu yi mata?. Zamu je mu samu Omar in ya fito mu ce masa Nayla na sonsa ne?. Ko zamu je mu samu Didi mu faɗa mata?."

Jidda ta ce, "Amma tana buƙatar ɗauki Salma." Salma ta ce, "shiyasa na ce addu'a itace mafita." Jidda ta yi ajiyar zuciya bata ce komai ba Salma ta ce, "ikon Allah, shi kuma farin jinin mata masu hankali da kyau Allah ya bashi. Ki dai duba Nayla da Narma, a cikin babu wacce tayi sa'ar aurensa, amma lokaci ɗaya duk sun birkice a kansa kamar wani mutumin kirki? Anya ma ba asirin ya yi musu ba kuwa?." Jidda tayi dariya ta ce, "Wanne asiri ana zaune lafiya?."

"Allah Jidda abin da mamaki, yʻan mata zuƙa-zuƙa kamar Nayla da Narma ace sun birkice akan sa? Yʻan mata masu asali, kyau, ga arzuƙi amma su rasa wa zasu fara so sai wani Omar....Omar ɗin ma na gidan Didi ɗan daba wanda ko sana'a bashi da ita?. Allah lamarin nan abin dubawa ne, dan ni zuciyata ta fara amincewa da batun sanata akan asirin nan wallahi. Kuma da alama wanda sunan su fara daga N ne suke faɗawa tarkonsa, wataƙila wani malamin ne ya bashi sa a akan Nayla da

Narma. Aniyarsa ta bishi, in sha Allah Nayla tafi ƙarfinsa." Ita dai Jidda dariya kawai take yi jin kalaman Salma na asiri.

Sai yamma Nayla ta farka a lokacin har sun shirya tafiya bikin Shayida, ta bisu da kallo ta ce, "har kun shirya?." Jidda ta ce, "ya ciwon kan?."

"Ya yi sauƙi sosai."

"To ki tashi ki yi sallah da wanka mu tafi."

"Anya zan iya zuwa Twiny? Ku je kawai basai naje ba." Salma ta ce, "A'a tashi ki shirya sai kin je, ganin mutane zai iya rage miki damuwa." Ta dole suka saka ta wanka ta shirya suka fita zuwa wajan bikin gabaɗaya.

KRB2007

Arewabooks@nanahaleema11

Washe gari bayan sallar azahar Abiy da Senator da wasu manyan mutane su shida gabaɗaya suna zaune a wani babban falo na alfarma suna hira da nishaɗi ana tuna rayuwar makaranta. Su huɗu a ciki duk yan siyasa ne, Abiy da wani ne kawai ba sa harkar siyasa.

Ana cikin hira Abiy ya kalli Senator ya ce, "Senator daman akwai maganar da zamu yi da kai." Sen ya ce, "Ina ji." Abiy ya ce, "Akwai wani yaro Omar da ka kama ya je Abuja gidan ka haka ne?."

Sen ya ɗaure fuska yanayin sa ya canja lokaci guda ya ce, "Haka ne." Abiy ya ce, "Ina neman alfarma ka taimaka ka bani shi." Sen ya kalli Abiy ya ce, "ka san abinda ya aikata min kuwa? Narma fa ya je har gida ya ce yana so yana kallo na ina kallon sa." Abiy ya ce, "na sani, naji labarin komai. Ya yi tsaurin ido sosai bai kuma kyauta ba, amma kaima matsayin ka na babban ɗan siyasa ajjiye a wani waje ana azabtar dashi hakan bai kamace ka ba."

Sen ya ce, "Babu yadda na iya ne, ina so a koya masa hankali shiyasa na aikata hakan. Na so na tura shi prison kawai na ƙyale shi ne."

"Amma abinda kayi a yanzu zai iya taɓa maka siyasarka, da zarar maganar ta fita shikenan za a dinga yaɗawa ana faɗar ƙarya da gaskiya. Ka fini sanin meye siyasa,

ka san yadda ƙaramin abu yake zama babba, ka san yadda ƙaramar magana take zama babba a gare ku."

Sen ya yi ajiyar zuciya ya kalli sauran ya basu labarin Omar kaf har zuwan Narma Kano da komai ya faɗa musu, kana ya ce, "in ban saka an killace shi an wulaƙanta shi ba ta ya zai fahimci ya yi kuskure?."

Mai girma gwamnan jahar Katsina kuma mahaifi ga Ashraf ya ce, "hakan ya yi, amma da ka sani baka saka ana wahalar da shi ba gaskiya, kai ka faɗa mana tasiri da ya yi maka a lokacin zaɓe, baka ganin zai zama tasiri nan gaba wajan lalata komai?." Senator ya yi shiru yana tunani kafin ya ce, "shiyasa zan san abinda zan yi a kai shi kotu a yanke masa hukuncin da bazai fito ba har abada."

"Wannan ba shawara ce mai kyau ba, kafi kowa sanin meye siyasa da yadda harkokinta suke gudana" Abiy ya faɗa yana kallon sa.

Senator ya ce, "asiri ya yi mata, in ba haka ba tana matuƙar son Ashraf, rana tsaka ta daina wai shi take so." Abiy ya yi dariya ya ce, "babu wani zancen asiri ni a ganina gaskiya, kawai tasirin soyayyar ne ba komai ba. Kuma yanzu ai komai ya wuce tunda ka tura ta london, a shawarata kawai ka aura mata Ashraf ɗin ya bita can su zauna a hankali zata manta dasahi."

Mahaifin Ashraf ya ce, "Abinda zan ce kenan, tunda ka ce ka tura ta London ayi auren au sai Ashraf ɗin ya bita can. Su samu good one year basa ƙasar nan, in suka dawo sai ayi biki tunda babu wanda ya san ma sun yi aure. Amma barin sa a kulle ana wahalar dashi zai iya taɓa ka nan gaba wallahi. In yan uwansa suka shiga gidajen yaɗa labarai suna cewa dan ya ce yana yarka ka yi masa haka ka yi tunanin maganar da zaka jawo." Wajan ya rabu biyu, Abiy da mahaifin Ashraf suna ganin riƙe omar bai kamata, ba sauran suna ganin hakan shine daidai.

Senator ya kalli Abiy ya ce, "A ina ka san shi?." Abiy ya ce, "Unguwar su a nan kakar Nayla take mahaifiyar Bilkisu matata da ta rasu. Shekaru kusan goma baya an taɓa yunƙurin yiwa Nayla fyaɗe, shine ya kuɓutar da ita har aka yi ƙoƙarin kai shi prison saboda ya zubarwa da yaron jini aka ce ya ɗauki doka a hannunsa, ni na san yadda akayi dai bai je prison ba. Yayarsa sun saba da Nayla sosai, halin da take ciki shine ya tashi hankalin Nayla tazo tana yi min kuka, kuma ko bata zo ba nayi niyar bin

maganar saboda na rama alkhairin da ya yi min da alkhairi. Ina neman alfarma ayi masa afuwa bazai sake wannan gangancin ba."

Sen ya yi ajiyar zuciya ya kalli Abiy ya ce, "kuma ka tabbatar itama ba asirin ya yi mata ba?." Abiy ya yi dariya mai sauti ya ce, "babu asirin da ya yiwa Narma ma balle Nayla ta shigo ciki, Babu abinda ya yi musu. Kuma ni dan ina bibiyar good background da good manners a aure ne, da ace yana dasu tsaf zan ce ka bawa Narma shi ɗin. Ai kana da arzuƙin da zaka iya sakawa ya tashi daga nobody to somebody."

Sen ya taɓe fuska ya ce, "Allah ya kiyaye, Jahili ne fa ko secondary school bai gama ba. Ina zai iya kaiwa a rayuwa babu ilimi?." Abiy ya ce , "ni dai ayi min alfarma a bani shi." Sen ya yi shiru yana tunani, bazai iya ƙin yiwa Abiy alfarma ba saboda mutuncin da yake tsakanin su. Amma in ya tuna wulaƙancin da Omar ya yi masa sai yaji bazai iya bada shi ba.

Senator ya ce, "Shikenan, za a ƙyale shi gobe. Amma saboda kai ne kawai babu yadda zan yi maka, amma wallahi da sai ya ƙare rayuwarsa haka." Abiy ya yi dariya ya ce, "godiya nake mai girma Senator kuma sirikin Gov, future Kano state gov in sha Allah." Dariya suka yi aka share zancen suka cigaba da hira har bayan sallar la'asar kafin kowa ya watse.

Kasancewar ranar ne dinner ɗin Shayida su Nayla suna gida su ukun a falo suna ta jan Nayla da hira amma ta kasa sakewa. Abiy ne ya shigo falon duk suka miƙe tsaye ya kalle su da murmushi suka gaishe shi ya amsa kafin ya kalli Nayla ya ce, "Mamana kina lafiya kuwa?." Nayla ta ce, "lafiya lau Abiy, ciwon kai ne tun na jiya har yanzu."

"Kwana biyu ciwon kai yana damunki sosai, ki je asibiti mana."

"Wallahi stress ne aiki na kawai Abiy, da nayi bacci na tashi sai na dawo daidai."

Abiy ya yi dariya ya ce, "kaga sabuwar ma'aikaciya." Tayi dariya Abiy ya zauna yana cewa, "ƙarfe nawa zaku tafi Kaduna gobe? Ni sai jibi monday zan dawo in sha Allah ." Nayla ta ce, "Duk lokacin ka ce Abiy."

"Saboda aikinki dole a koma gobe gaskiya, zamu gani zuwa azahar sai ku tafi in Allah ya kaimu."

Bata yi magana ba ya kalle ta ya ce, "Maganar ɗan daban yaron nan." Ai da sauri ta ɗago tana kallonsa a lokacin Mama tazo ta zauna a wajan. Abiy ya ce, "Mun yi magana da Senator..." ya faɗa yana duba waya wacce saƙon text ya shigo. Shiru ya yi bai yi magana ba yana duba wayar. Nayla ji take kamar ta ƙwace wayar daga hannunsa saboda ya kai ga faɗa mata abinda zai ce.

Abiy ya ajjiye wayar ya ce, "mun yi magana ya kuma amince zai ƙyale shi, gobe ma ya ce zai sake shi ya dawo gida in sha Allah." Wata irin ajiyar doguwar zuciya Nayla tayi, ta lumshe idanu tana jin wani irin daɗi na ratsa zuciyarta. Abiy ya bita da kallon mamaki ganin yadda farin ciki ya bayyana a tare da ita kamar itace Yayar ta sa. A hankali ta buɗe ido suka haɗa ido da Abiy da yake kallonta, da sauri ta sunkuyar da kai amma murmushi take yi. Abiy ya ce, "ko dai kema ƙanwarsa ce ne Nayla? Wannan ajiyar zuciya haka kamar Jawad aka kama za a saki?."

Murmushin yaƙe tayi ta ce, "Abiy kawai Ina murna ne in na tuna yadda Didi zata yi murna." Abiy ya zuba mata ido yana binta da kallon tuhuma kafin ya ce, "kin tabbata?." Sai taji tsoro ya shige ta da tunanin Allah yasa bai gane wani abun ba. Ta sake sunkuyar da kai tace, "Eh Abiy."

"To ya yi. Ki sanar mata gobe zai dawo in sha Allah." Da farin ciki ta amsa shi kuma ya tashi ya shiga ciki Mama ma tabi bayansa. Nayla na shiga ɗaki sai gata ta fito da key ɗin motar Mama, Salma da Jidda suka kalle ta kafin su magana ta ce, "Gidan Hajja zan je, in zaku je kuzo mu tafi." Salma ta karɓi key ɗin hannunta tace, "bani baza ki sake ƙoƙarin kashe mu ba." Bata ma ji ba tayi gaba burinta kawai taje ta faɗawa Didi. Salma ce ta ja motar suka tafi gidan Hajja.

Nayla na shiga ta tarar da Didi ita da AbdulHamid suna tsaye da alama sallama yake yi mata. A guje ta faɗa jikin Didi ta ce, "Didi Abiy ya yi magana da Senator ya tabbatar masa da gobe zai dawo, gobe zai dawo Didi" ta faɗa da murna sosai. Didi cikin farin ciki ta ce, "da gaske ki ke? Da gaske ki ke Nayla?."

"Da gaske nake Didi." Didi ta ce, "Alhamdulillah! Allah na gode maka, Allah na gode maka" ta faɗa tana sake rungume Nayla da take dara saboda murna.

"Na gode Nayla, na gode Allah ya saka miki da alkhairi Allah ya baki miji na gari." Ciki suka shiga dan Didi ta manta da AbdulHamid da yake wajan. Sai da suka shiga

falon Hajja Salma ta ce, "Amin Didi. Dan wallahi itace jiya ta samu Abiy tana kuka kamar zata mutu saboda a fito da Omar, yadda muka bar gidan nan jiya baki ga gudun da ta dinga yi damu a mota ba saboda kawai take ta samu Abiy. Cikin ikon Allah tana faɗawa masa ya kira shi a waya ya ɗauka, yau suka haɗu ya yi masa maganar ya kuma amince" Salma ta faɗa tana kallon Didin da ta san aikin Nayla ne yadda ko Omar ɗin ya fito ya san ita tayi masa hanya ya fito.

Didi ta sake riƙe Nayla tana godiya tana hawaye tana cewa, "na gode Nayla, Allah ya bani abinda zan saka miki Nayla. Na gode sosai." Hajja ta ce, "itama ai ta saka alkhairin da ya yi mata ne Aisha, kin manta abinda ya yi mata?." Didi ta ce, "ban manta ba Hajja, amma wannan taimakon da tayi min ai baza ki haɗa shi da wancan ba. Ta ceci rayuwata ta ceci ta Omar, bani da abinda zan saka mata saka addu'a."

Hajja tayi dariya dan ko ita ta ji daɗin labarin dawowar Omar. Didi ta ce, "Nayla mu je na yiwa Abiy godiya, mu je yanzu in yana gida." Hajja ta ce, "A'a Aisha, ki bari ya dawo sai ku je ku same shi tare." Didi ta ce, "Amma ya kamata na je yanzu kafin ya dawo ko?." Nayla ta ce, "to sai mu je in anjima, ko kuma ki yi masa waya."

A nan suka baje ana ta hira da nishaɗi Didi ji take kamar ta mayar da Nayla ciki saboda son da take yi mata. Sai bayan i'sha suka tafi saboda dinner da zasu je, tare da Didi aka je ta yiwa Abiy godiya ya ce babu komai. Drivern Hajja ne ya dawo da Didi su kuma suka fara shirin dinner. Ko a wajan dinner kowa ya lura da walwalar da Nayla take yi, su dai su Salma fatan samun sasssuci akan abinda yake damunta suke yi mata.

Washe gari ranar lahadi ƙarfe goma na safe ta fita daga gida zuwa gidan Hajja. Ta samu Didi ma bata nan ta shiga gida tana aikace-aikace Saboda dawowar Omaar. Salma ce ta shigo tana cewa, "shine ko ki jira ni kika taho bayan kin san Jidda tana gidan ta." Nayla ta ce, "to ba gashi kin zo ba. Matsa min naje gidan Didi." Salma ta ce, "ba da wuri Abiy ya ce zaku koma ba ne? Yana ta faɗa ya ce kin san zaku tafi Kaduna ki ka fito yawo."

"Kin ga Ina zuwa" ta faɗa tana fita ta shiga gidan Didi Salma na biye da ita.

Lokacin da suka shiga Didi share ɗakin Omar take yi, jin sallamar Nayla ya saka Didi ta ce, "Nayla gani nan, shigo." Nayla gabanta ya faɗi matuƙa, ta kalli Salma da take tsaye sai Salma tayi tsaki ta shiga ɗakin.

Nayla ta shiga ɗakin a sanyaye da sallama gabanta yana faɗuwa, ɗaki ne babba mai girma dan yafi na Didi girma. Babu tarkace a ɗakin babbar katifa ce mai girma da tudu, sai wardrobe mai guda shida a gefe, sai mirror mai irin wardrobe ɗin a gefe wanda abubuwan da suke kansa basu wuce guda biyar ba.

Didi ganin Nayla sai ta yi murmushi ta ce, "Nayla har kin fito?."

"Wallahi na fito Didi. Kin san fa yau zamu wuce Kaduna." Didi ta ce, "wallahi duk sanda ki ka zo bana so ki dinga zancen zaki koma Kaduna ɗin nan, bana jin daɗi ko kaɗan.." Nayla tayi dariya tana cigaba da kallon ɗakin da sai ƙhamshi turare yake yi mai sanyi.

Didi ta ce, "Ina gyara ɗakin mutumin naki, in ba haka ba in yazo da faɗa zamu fara kin san baya ƙaunar ƙura ko kaɗan. Zai iya zama wajan da aka zubar da kaya amma bazai iya zama a waje mai ƙura ba. Shiyasa yake gyara ɗakinsa ko yaushe, dan shi baya jin gyaran ɗaki." Salma ta girgiza kai ta ce, "Ga ɗakin nan tsaf dashi kamar ba na maza ba, har so nake na shigo dan naga ƙazantar da take ciki ashe ɗan gayu ne."

Didi ta yi dariya ta ce, "Ai baya shiri da waje kaca-kaca, kinga tsintsiyarsa a ajjiye ga dustbin"

Didi ta faɗa tana nunawa Salma amma Nayla ce ke gani. Salma ta ce, "shikenan ya huta, ko ya yi aure babu ruwansa da sai an gyara masa ɗaki."

Nayla sai murmushi take yi tana kallon ɗakin tana jin farin ciki a zuciyarta. Fita suka yi zuwa falon Didi bayan ta gama gyarawa har da fesa airfreshner. A falon suka zauna suna ta hira Nayla sai kallon ƙofa take yi amma babu alamun Omar ko kaɗan.

Duk ta damu ga rana tana yi lokacin tafiyar su yana gabatowa. Suna zaune har azahar tayi Omaar bai dawo ba, a lokacin kiran Abiy ya shigo wayarta tana ɗauka bai jima yana magana ba ya kashe, Nayla ta kalli Salma da Didi ta ce, "Didi zan je gida zan haɗa kayana zan wuce, sai dai na ce sai na dawo wani lokaci. Wataƙila ma sai bikinki" ta faɗa tana kallon Didi.

Didi ta ce, "tafiyar ta tashi?."

"Wallahi Abiy yace na zo zamu tafi."

"Na so kun haɗu da Omar kafin ki tafi gashi bai dawo ba har yanzu. Amma zamu zo Kaduna tare dashi mu sake yiwa Abiy godiya sha Allah." Nayla ta yi murmushi ya ce, "Allah ya kawo ku. Salma zo mu je" tare suka fito Didi tana ta yi mata godiya har sai da Nayla ya nuna bata so sannan ta daina suka shiga gidan Hajja. A harabar gidan Hajja ta kalli Salma ta ce, "Salma don Allah ki zauna da Didi in ya dawo ki yi min video ki tura min kin ji?."

Yadda tayi maganar sai ta bawa Salma tausayi a sanyaye ta ce, "in sha Allah zan yi miki, kar ki damu."

"Na gode yʻar uwa." Daga haka suka shiga wajan Hajja tayi mata sallama a gaggaucs saboda kiran Abiy da yake shigowa wayarta. Ta ɗauki motar da ta zo da ita ta bar unguwar zuciyarta duk babu daɗin rashin ganin masoyinta.

KRB2P008

Arewabooks@nanahaleema11.

Didi da Salma tun suna zaman jiran dawowa Omar har suka gaji da zama suka koma gidan Hajja. A can suke zaune har akayi sallar magriba babu alamun Omar. Didi a lokacin ta yi ajiyar zuciya a sanyaye ta ce, "wataƙila bai amince ya sake shi ba ne, wataƙila kuma Omar ɗin ne ya yi taurin kai ko ya faɗi wata magana mara daɗi." Hajja ta ce, "ki ta addu'a zai dawo, tunda Abdullahi ya ce zai dawo na tabbatar zai dawo kar ki damu."

"Assalamu alaikum!" aka faɗa a ciki ba tare da sallamar ta fito sosai ba tare da shigowa cikin falon. Gabaɗaya suka juya ga wanda ya shigo suna kallon sa.

Didi wara idanu tayi ganin Oamar ɗinta a tsaye yana kallonta, sai ta zabura ta miƙe ta ƙarasa inda yake ta riƙe hannunsa ta ce, "Omar kai ne?." Kai ya ɗaga mata ya ce, "eh Didi, ni ne." Ajiyar zuciya ta yi ta ce, "Alhamdu lillah! Allah na gode maka, Allah na gode maka da ka dawo min da Omar cikin ƙoshin lafiya."

Duk ta ruɗe tana addu'a kamar wacce bata cikin hankalinta, ganin hakan sai ya dafa kafaɗarta muryarsa a shaƙe ya ce, "Didi ki nutsu mana." Didi ta ce, "na kasa

nutsuwa Omar, na kasa. Farin cikin dawowarka ba zai bar ni na nutsuwa ba." Sai a sannan ya kalli Hajja da take kallonsa ya ce, "Ina yini."

Hajja ta ce, "daga nan? Baza ka shigo ka zauna ba?." Didi ta riƙo hannunsa zuwa cikin falon ya tako daƙyar dan baya jin daɗi gabaɗaya. Zama ya yi Hajja ta kalle shi ta ce, "Barka Omar, Ina fatan komai lafiya ko?." Kai ya ɗaga kawai bai ce komai ba dan maganar ma wahala take masa, ya kalli Didi da take kuka ya ce, "meye na kukan kuma Didi? Ba dai gani na dawo ba? In kina kuka bazan ji daɗi ba."

Saurin goge ido tayi ta ce, "na daina Omar, farin cikin ganin ka ne ya saka haka nake kuka amma na daina." Hajja ta yi murmushi tana kallon sa, abinda ya bata mamaki tsaf dashi baza ka ce ya fito daga wahala ba. Duk da ya rame sosai fuskar sa ta ɗan yi duhu amma shigarsa da yanayinsa gabaɗaya bai nuna haka ba. Yadda ta ce gashin fuskarsa ya taru yanzu duk an rage sai wanda ya saba bari abin ya bawa Hajja mamaki.

Didi ta kalle shi ta ce, "Ka yiwa Hajja godiya, ta silar Hajja da Nayla ka dawo gida yau. Mahaifin Nayla shine ya saka aka dawo da kai gida." Hajja ta katse ta ta ce, "Aisha ki bar shi ya huta tukunna, yana buƙatar hutu sosai. Ku je gida ya huta maganar ta biyo baya." Kamar jira yake ya miƙe dan daman bai so shigowa ba, kawai dan Bashir ya ce masa tana ciki ne ya saka shi ya shiga. Hajja ya kalla ya ce, "Sai da safe."

"Allah ya tashe mu lafiya Omar" ta faɗa da murmushi tana kallon sa.

Fita ya yi Didi ta dawo kusa da Hajja ta ce, "na gode Hajja, na gode Allah ya biya ki da aljanna. Duk ta dalilinki Omar ya fito, ta dalilinki ne Hajja. Allah ya sa aljanna ce makomarki." Hajja da Salma suka amsa da amin Hajja ta ce, "kar ki damu Aisha ai a riga an zama ɗaya, kallon jikata nake yi miki kamar Nayla da su Salma, Kar ki damu ki kwantar da hankalinki. Ki shiga kitchen ki ɗauki abinci a nan ki kai masa ya ci ya huta, in zai je ganin likita ma aje a duba shi ya dawo hankalinsa kamar da."

Didi ta ce, "to Hajja. Amma na so Nayla tana nan ya dawo, ban san dame zan sakawa Nayla abinda tayi min ba Hajja." Hajja tayi murmushi ta ce, "kin san bashi da uwa sai ke Aisha, ki tashi ki je ki bashi abinci ya huta sai mu yi magan." Da to ta amsa ta tashi taje ta ɗauki abinci a kitchen ɗin Hajja, ta ɗauki hijjabi da wayarta ta fita daga gidan cikin farin ciki.

Hajja tayi murmushi bayan ta fita ta ce, "Allah sarki Hauwa'u sarki tausayi, sai da ta san yadda tayi mahaifinta ya fito da Omaar. Allah ya biyata." Salma ta amsa da amin tana kallon video da ta yi a zuwan Omar tana tunanin ta tura mata ko ta share ta kawai. Kiran Nayla ne ya saka shigowa wayarta, daga tafiyarta zuwa yanzu sau goma sha bakwai kenan tana kiranta, Salma

tayi tsaki ta miƙe ta shiga ɗaki.

Didi da ta fita a tsaye a ƙofar gidan ta ga Omar shida mutane sa, da hanzari ta ƙarasa ta buɗe gidan ta manta a rufe gidan ya ke. Sai da ta ɗan jima da shiga sannan ya shigo falon tana kallon sa har ya ƙaraso. Ta ce, "ƙanina ga abinci kazo ka ci sai ka kwanta ka huta ko?." Omar ya zauna ya ce, "na ƙoshi Didi, na ci abinci magani kawai zan sha na kwanta."

"Sannu" ta furta a sanyaye tana kallon sa. Kawai ya ɗaga kawai bai ce komai ba.

Didi ta ce, "na ganka tsaf ba kamar lokacin da naje na same ka ba." Omar ya ce, "ban shigo cikin gari ba sai da na tabbatar na dawo nutsuwata. Da aka bani wayata sai na kira su Bash suka same ni a wajan gari, har asibiti mun je a ƙara min ruwa an kuma bani magani. Wannan dalilin ne ya saka na jima ban shigo ba sai yanzu." Didi ta ce, "gwara da ka yi hakan ko dan saboda yɗan gulma. Amma ka rame sosai Omar, kuma ka yi duhu." Bai ce komai ba ta sake kallon sa ta ce, "to ka sha maganin kafin kwanta sai ka fi jin daɗin bacci."

Kallon ta ya yi da kulawa ya ce, "kema kin rame Didi, baki da lafiya ne?."

"Lafiya lau nake Omaar, rashin ka ne kawai ya kawo hakan." Ɗan murmushi ya yi ya ce, "Sai ka ce in ina na nan ɗin ba faɗa muke yi ba." Didi ta yi yɗar dariya ta ce, "Ko doke-doke muke yi ƙarewar faɗa ba." Murmushi ya sake yi ya ce, "Kar ki damu yanzu na dawo ai."

Kafin ta yi magana ya ce, "an ce a gidan Hajja ki ke kwana ko?."

"Eh Omar, hana ni kwana anan tayi ta ce na koma gidan ta saboda mutane." Kai ya girgiza da yayi masa nauyi bai sake magana ba. Dauriya kawai yake yi yana magana saboda ita, amma kansa ciwo yake yi sosai.

Miƙewa ya yi sai ya yi kamar zai fadi ta zabura ta miƙe tana kallonsa, Omar ganin yadda ta zabura sai ya dake ya ce, "kar ki damu ba wani abun bane, kaina ne yake ciwo kaɗan." Har ɗaki sai da ta raka shi ta tabbatar yana cikin ƙoshin lafiya sannan ta fito ta shiga nata ɗakin tana tunanin dame ya kamata ta sakawa Nayla alkhairin da tayi mata?.

Washe gari.

Ya ji sauƙin jikinsa babu laifi ya daure bai kwanta ba saboda kar hankalin Didi ya tashi, hakan ya saka shi ya fito ya samu tana ta aikace-aikace kamar kullum. Tana ganinsa ta dakata ta ce, "ka fito? Ya jikin na ka?." Ɗan lumshe ido ya yi ya buɗe, da zai iya faɗa mata gaskiya da ya ce mata babu sauƙi dan ciwon kan bai rabu dashi ba, ga jikinsa gabaɗaya babu ƙarfi, ga ciwo da duk gaɓoɓin jikinsa suke masa. Amma da yake baya so ya sakata a damuwa sai ya ce, "na ji sauƙi. Kawai bana jin ƙarfi ne sosai."

Didi ta ce, "Sannu. Zauna na kawo maka shayi ka sha zaka ji daɗi." Zaman ya yi kamar yadda ta ce ta kawo masa shayi ya karɓa tana yi mata sannu. Zama tayi a nesa dashi tana kallon sa ta ce, "sannu Omar." Kai ya ɗan ɗaga kaɗan yana shan shayin a hankali ba dan yana jin daɗinsa ba sai dan saboda ita ɗin.

Shiru ya ratsa tsakani, tayi shiru shima ya yi shiru yana shan tea a hankali yana kallon wani wajan daban. Didi ta ce, "in ka warware ina so zamu je Kaduna gidan mahaifin Nayla mu yi masa godiya. Shi ne ya yi magana da Sen ya rabu da kai Omar, yarsa Nayla ce taje tana kuka ta ce don Allah ya yi wani abun ka fito." Omar ya kalle ta ya ce, "to" ya amsa a taƙaice dan baya son doguwar magana.

Ido ta ga ya lumshe ya ajjiye kofin hannunsa ta bishi da kallo kafin ta miƙe ta ƙyale shi a wajan tana cigaba da aikin da take yi.

••••••

England, london.

Tunda Narma da Najwa suka sauka a ƙasar England Najwa ta kasa gane kan Yayarta, domin kuwa ta koma wata iri babu walwala babu dariya babu zaman hira. Ko yaushe tana cikin ɗaki ta rufe kai ko tana kuka ko tana tunani. Gabaɗaya zaman bai yiwa Najwa daɗi ba saboda ba haka suka saba zaman ba, sun saba su ne yaje su je nan su je can, amma yanzu gabaɗaya ta canja.

Narma ta kasa sarrafa kanta akan son da take yiwa Omar, ta rame ta ɗan yi dogon wuya saboda tunani. Gangar jikinta ce kawai a England amma hankalinta da komai nata yana Nigeria.

Tana zaune cikin riga da wando masu laushi kanta babu ɗankwali ta zubawa waje ɗaya idanu. Ƙarar shigowar message taji kamar baza ta duba ba sai kuma ta duba taga daga WhatsApp ne ta buɗe tana karantawa. Ai da sauri ta kira voice call yana ɗauka ta ce, "Da gaske ka ke Dad ya saki Faruk?." Shiru tayi alamun ana bata amsa kafin ta ce, "Shikenan ina zuwa" ta faɗa hannu na rawa tana kashe wayar.

Farin ciki ya bayyana akan fuskarta a bayyane ta ce, "Dad ya saki Faruk, Faruk ya koma gida. Wayyo Allah daɗi, Allah na gode maka." Number Omar ta nemo babu wani tunani kawai ta kira voice call. Ringing ta dinga yi alamun ba a kunna data ba ta kashe wayar tare da cillar da ita gefe ta ce, "Ko ya yake? Ko yana tunanina kamar yadda nake tunaninsa?."

Najwa ce ta ƙaraso wajan ta ce, "Ya Narma ga ticket na siya mana zamu je emirate stadium kallon wasan arsenal da liverpool." Narma ta kalle ta ta ce, "Sai kin dawo, ni bazan je ba."

"Meyasa baza ki je ba? Kuma na ga Arsenal shine club ɗin da kike so, Meyasa baza ki zo mu je ba?."

"Najwa bana jin daɗi don Allah ki ƙyale ni, bazan iya zuwa ko ina ba."

Najwa bata sake magana ba ta koma ɗaki ta kira Mum, Mum tana ɗauka ta ce, "Mum Ya Narma tana gab da kashe kanta da tunani, tunda muka zo nan bata da wani aiki sai na tunani Mum. Kullum kuka, kullum cikin ganin hotonsa take tana magana ita kaɗai. Mum lamarin Ya Narma ya fara bani tsoro wallahi."

Mum ta ce, "kuma kina zama a inda take?."

"Mum bata bani wannan damar, yau ne fa take zaune a falo amma kullum tana cikin ɗaki ta kulle kanta. Har ticket na siya mana yanzu na zuwa kallon ball amma ta ce baza ta je ba, kuma Arsenal ne fav club ɗin da take supporting." Mum ta ce, "ki cigaba da jan ta da hira, in abin bata yu ba sai ku dawo kawai." Najwa ta ce, "daman ni na gaji da zaman nan wallahi" ta faɗa tana yanke wayar tana mita.

KRB2P009

Arewabooks@nanahaleema11

Nigeria, Abuja.

Lokacin da Mum ta yanke wayar Najwa kallon Sen tayi da yake jin duk abinda Najwa take cewa, cikin fusata Mum ta ce, "ana cikin wannan yanayi kuma wai ka saka aka sake shi, mu da muke so ya karya asirin da ya yi mata amma ka sake shi ya bar ma Abuja salin alin kamar wanda mu ke jin tsoro. Gaskiya Dear baka kyauta ba sam, baka kyauta min ba nida Narma, abinda ka yi bai kamata ace kayi shi ba. Ka san yadda muke ciki da Narma amma ka iya bari ya bar Abuja lafiya ba tare da wata damuwa ba, ka ga kenan ya yiwa banza."

Dad da yake jinta yana daga zaune ya ce, "Dear ki nutsu mu yi magana."

"Bazan taɓa iya nutsuwa ba wallahi, ya asirce min yarinya bata iya ganin kowa sai shi ka ce na nutsu?."

"Calm down please, ki zauna mu yi magana."

"Ina zancen yaɗata tana london ta kasa sukuni saboda asirin da aka yiwa mata kana ce min I should calm down!. Wallahi dear in wani abun ya samu Narma, in Narma ta samu ciwo ta wannan dalilin, in Narma ta yiwa kanta illa ta dalilin wannan asirin da ya yi mata ba tiger ba, wallahi ko lion ne sai na ga bayan sa! Wallahi sai na saka an raba shi da numfashinsa gabaɗaya!" Ta faɗa cikin ihu tana kallon Dad da yake kallon ta.

Dad ya miƙe tsaye ya riƙe ta cikin rarrashi ya ce, "ki nutsu mu yi magana mana." Mum ta ce, "bazan nutsu ba! Duk kai ka jawo wannan abin, na faɗa maka kar ka haɗa min yarinya da ɗan daba amma ka ƙi ji. Ga abinda hakan ya haifar nan muna gani ni da kai, kuma ana ƙoƙarin samun mafita akan kuskuren da ka yi ka sake tafka wani kuskuren ta hanyar sakin sa da ka yi. Anya kaima ba asirin ya yi maka ba?."

Dad ya ce, "Nayi hakan ne saboda tafiyar siyasar mu dear. Ke kin san matakin gov nake nema, kin san yana da tasiri sosai a ɓangaren zaɓen baya. Barinsa a hannunna in labarin ya fita hakan zai iya taɓa carrier ta, sannan shima zai iya sakawa ayi abinda bazan kai labari ba. Shiyasa ana sake shi."

Mum ta ce, "babu abinda zai iya, babu abinda ya isa ya hana babu abinda ya isa ya saka ayi. Waye shi? Waye shi nace!? Ka manta da waɗanda aka yi gwagwarmaya ne? Ka manta ta yadda aka yi ka zo wannan matakin ne?."

"Ya isa dear, Dear ya isa. Zai iya taka rawar gani wajan ganin ya kai ni ƙasa." Mum ta ce, "Shiyasa ai nace a gama dashi, shiyasa nace a raba shi da numfashinsa amma ka ƙi ji. Yanzu me ka ke so ayi? Haka zamu bar Narma kenan?."

Dad ya ce, "Aura mata Ashraf zamu yi a tura shi su zauna na ɗan lokaci, in yaso daga baya sai su dawo ayi biki. Hakan shine mafita kuma na tabbatar Ashraf zai yi iya bakin ƙoƙarinsa wajan ganin Narma ta dawo hankalinta saboda tana sonsa." Tsaki Mum ta yi ta ce, "wannan ba shawara ba ce, ka ƙyale ni da kaina zan ɗauki matakin da kai ka kasa ɗauka, zan yi masa abinda zai karya asirin koda ba ya so, na san abinda zan yi" ta faɗa tana fita daga ɗakin da yake ya bita da kallo yana ajiyar zuciya cikin ƙunar zuciya.

•••••••

Haka Omar ya yini a gida babu inda yaje saboda baya jin daɗi ko kaɗan. Didi ce take ta hidima dashi har dare a lokacin AbdilHamid yazo. Ya yi farin cikin dawowar Omar ko babu komai Didi zata nutsu su fuskanci abinda ya ke gaban su.

Washe gari ya tashi babu laifi ya ɗan ji ƙarfin jikinsa, da ya shiga falon ya same ta tana karatun alkur'ani, da sallama ya ƙarasa ya zauna sai kuma ya tashi ya shiga kitchen ya zuba tea ya dawo ya zauna yana sha a hankali. Sai da ta kai ƙarshen aya sannan ta rufe ta kalle shi ta ce, "ya jikin?."

"na ji sauƙi. Ya ku ka yi da AbdulHamid jiya?."

"Maganar gida ce. Ni wallahi ban san ma ya za a yi ba, ya ce zai zo da makullin gidan a je a gani dan asan abinda za a zuba. Sai kuma batun kawo lefe, shi na ce kawai maza su kai gidan Kawu."

Kai ya girgiza kafin ya ce, "Allah ya kaimu."

"Amin" ta amsa a taƙaice dan baza ta yi masa maganar hidimar biki da kayan ɗaki ba a yanzu saboda yanayin da yake ciki. Kira ne yake shigowa wayarsa ya kalla yaga Narma ce ya ɗauke kai ba tare da ya ɗauka ba yana kulle ido.

Didi ta ce, "ana yi maka waya." Bai buɗe ido ba balle ya amsa mata, a lokacin wayar ta sake shigowa nan ma bai ɗauka ba kuma bai katse ba. Didi ta kalle shi a sanyaye ta ce, "Narma ce take yi maka waya?." Buɗe ido ya yi ya kalle ta ya ce, "tun jiya take kira na, ni ban san me zance ba." Didi ta ce, "gwara kar ka ɗauka ɗin ya fi alkhairi. Ka cigaba da addu'a Allah ya cire maka ita daga zuciyar ka, ita kuma sonka da Allah ya ɗora mata ya canja mata da mafi alkhairi."

Bai amsa ba ya sake mayar da ido ya rufe, baya jin daɗi gabaɗaya a zuciyarsa sai yaji kamar bai kyauta mata ba. Ko babu komai ai tana sonsa kuma mai sonka yafi wanda ya ce baya sonka. Gashi abinda yake ji a kanta a baya duk ya sire masa, ya kasa gane dalilin da ya saka baya jin abinda ya ji dah a kanta. Duk da ya alaƙanta hakan da abinda ya faru amma bai kamata ace ya daina ji gabaɗaya ba, ya ɗauka wani abun zai rage ko ya ya yake amma babu ba. Ya ajjiye batunta a gefe, ya tsallake ta ya wuce gaba dan shi giwa ce baya waiwaye, in dai har ya wuce to ya wuce kenan har abada.

"Didi!." Jin yadda ya kira sunanta sai ta kalle shi a nutse ta ce, "Na'am." Zuba mata idanu ya yi ya ce, "dama hiv ta kashe mahaifiyar mu?." Didi ta runtse ido a sanyaye ta ce, "ƙarya ne wallahi, ƙarya ce kawai aka faɗa mana dan mu ji zafi a zuciyar mu amma ba haka abin yake ba. In da ace haka ne kaima ka san da labarin bai kai yanzu bamu sani ba. Da lokacin da muke gidan su Kawu mun san labarin, tunda har basu faɗa mana ba wallahi ba haka bane Omar."

Ajiyar zuciya ya yi yana tuna irin kalaman da Senator ya yi amfani dasu masu zafin gaske a gare shi, in ya tuna kalamansa akan iyayensa sai yaji kamar duniyar tana juya masa. Yafi jin zafin zagin iyayensa da ya yi fiye da komai, ya ji raɗaɗi da ƙunar zuci wacce bai taɓa ji ba a rayuwarsa. Buɗe ido ya yi ya kalli Didi ya ajjiye kofin

hannun sa ya ce, "Didi daman ashe kece ki ke ciyar dani a gidan nan? Na kasa yarda da gaske kece ki ke ɗaukar ɗawainiyata. Daman kallon da ake yi min kenan?."

Didi ta ce, "ba gaskiya ba ne Omar, ka tuna kana bani kuɗi a siyo abinda babu a gidan nan. Kaine ƙarfin yin abubuwa na gidan nan Omar bani ba, kar wannan maganar ta dame."

"Amma kafin na baki kuɗi a siya ke kin siya, saboda haka ki ke sana'a mai wahala domin ciyar dani. Tabbas abinda aka ce gaskiya ne, ban iya ɗaukar ɗawainiyar Yayata ba ta ya zan iya ɗaukar ta wata mace?."

Didi a sanyaye ta ce, "Wallahi ƙarya ne, in ma Senator ne ya faɗa maka haka ya faɗa dan ranka ya ɓaci kawai. Omar meye baka yi min? Duk kuɗin da ka samu a kaina yake ƙarewa, kana ɗinka min suttura ka hana kanka, ka bani kuɗi ka hana kanka amfani dasu. Don Allah kar wannan ya dame ka, ƙarya ce kawai da son ɓata maka rai."

Ajiyar zuciya ya sake yi idanunsa sun yi ja sosai ya ce, "ba a taɓa faɗa min kalaman da naji zafin su a duniya ba kamar abubuwan da ya faɗa a kanki da iyayen na, ba a taɓa yi min abinda naji zuciyata na rawa kamar abinda ya yi min ba. Ya kira ni jahili ya fi a irga, tabbas kuma na san bani da ilimi boko amma na addini ina da daidai nawa, ina da karatun addinin da bana tunanin shi yana dashi. Amma daman sai mai ilimi ne akwai yake zama wani a duniya?" Ya faɗa yana tsareta da idanunsa da suka koma jajaye.

Didi t ce, "A'a, Allah yana ɗaukaka duk wanda ya so a lokacin da ya so. Baka ji hausawa suna cewa dare ɗaya Allah kan yi bature ba? Wanda ba baturen ba ma dare ɗaya Allah yake yin sa. Haka arzuƙi, mutuwa, aure duk lokaci ne dasu, Omar in yanzu rabon ka ya kira ka rufe ido da buɗewa ya fi wahala akan ɗaukakar da zaka samu a lokacin da ka amsa KIRAN RABON ka. Shiyasa Allah ya ce tashi in taimaka maka, baza ka je kan titi babar mota taho ka kwanta ka ce Allah kare ni ba, baza ka ƙi karanta komai a yayin rubuta jarabawa ba ka shiga ɗakin jarabawa ka ce Allah zai yi min ba. Dole sai ka tashi sannan Allah zai taimaka maka."

Sunkuyar da kai ya yi kafin ya ɗago ya kalle ta ya ce, "Didi!." Ta kalle shi bata amsa ba ya ce, "Daga yau zan koma irin yadda ki ke so na zama, duk abinda nake yi

wanda ba mai kyau ba ki faɗa min ni kuma daga yanzu zan daina." Didi ta yi murmushin cikin farin ciki ta ce, "Da za kayi haka da ka nunawa masu son ganin ka ƙasƙanta cewa da Allah ka dogara, da zaka bawa maƙiya mamaki Omar."

"Ina jin ki."

"Omar gabaɗaya harkar daban nan zaka ajjiye ta a gefe, ka daina ɗaukar wuƙa kwata-kwata, sannan ka nutsu ka kama sana'a ka zama mutum kamar kowa. Daman ba shiga harkar mutane ka ke yi ba, ka cigaba da rayuwarka ka sake ƙarfafa addininka. Sallah, azumin nafila, sadaka, taimako ka ƙara akan yadda ka ke yi, aikin alkhairin ka ya danne na sharrinka Omar."

Ya kalle ta bayan ta gama ya ce, "iya abinda zan yi kenan?." Ta ɗaga kai ta ce, "shine kawai. Sai kuma ka koma makaranta, sannan ka shirya da dangin mu, ka bar komai ya wuce a cigaba da zumunci."

Hannu ya ɗaga ya girgiza yatsansa ya ce, "har abada na gama yin karatu, bazan sake yin makaranta ba, Har gwara ma karatun addini akwai makarantar da na gani ana yi online zan shiga kodan sake gyara lahirata. Sannan batun dangi ma ki cire shi ya koma gefe, har gwara makarantar akan dai batun waɗancan matsiyatan. Ki cire batun karatun boko dana dangi, amma abinda kika ce da farko zan yi."

Didi ta yi dariyar farin ciki ta ce, "Allah ya baka iko Omar, Allah ya taimake ka ya yi riƙo da hannunka, Allah ya kai ka matakin da baka yi tunanin zuwa ba, Allah ya sa ka taka matsayin da baka yi tunanin takawa ba, Allah ya kawo maka alkhairin da baka yi zaton samunsa ba a rayuwarka. Naji daɗin wannan canjin Omar, naji daɗi, Allah ya sa ka yi abinda ka ce."

Kallon ta yayi yana girgiza kai ya ce, "zan yi, tunda na ce ai kin san zan yi" ya faɗa yana ɗauke ido daga kanta yana wani tunani daban. Didi ta ce, "Har makarantar da kayi magana zaka yi?."

"Da ban faɗa ba kin san da ita ne?."

"A'a ban sani ba."

"To tunda ki ka ji na faɗa zan yi."

"Ka yi mana register nima zan shiga."

"To."

Didi sai murmushi take tana kallon sa shi kuma ba ita yake kallo ba, Miƙewa ya yi ya fita ta bishi da kallo kafin ta faɗi a wajan ta yi sujjada ta godiya ga Allah da ya nuna mata ranar da ta faɗi kuskurensa ya amsa har ya ce zai gyara. Duk da bai amince da batun gyara zumunci ba, amma tunda ya fara karɓar gyara ta san a hankali zai bar komai ya zama labari. Tabbas soyayyar Narma a wajansa tamkar kiran rabo ce.

KRB2P010

Arewabooks@nanahaleema11.

Da wannan farin cikin Didi ta yini tana ta aikin ta cikin zafin nama da karsashi. Wajan Hajja ma take so ta shiga ta bata labarin abinda ya faru amma so take yi ta gama sai ta shiga. Bayan sallar la'asar ya shigo da sallama ta amsa tana fitowa daga kitchen tana cewa, "Ina ka shiga? Ga abinci ka zo kaci." Omar ya zauna tare da ɗan kashingiɗa ya kalle ta ya ce, "na je unguwa ne."

Fitowa tayi ta zauna ta ce, "unguwar bata da suna?." Miƙewa zaune ya yi a kan kujerar ya ce, "zan faɗa miki."

"To abincin fa?."

"A'a bana jin yunwa yanzu." Didi ta ce, "zuwa jibi nake so mu je Kaduna gidan su Nayla mu yiwa mahaifinta godiya." Kallon Didin ya yi ya ce, "to" ya furta dan bai san me zai ce ba. Ya san dai bazata taɓa amincewa ba in ya ce bazai je ba shiyasa ya ce to.

Wayar ta ce take ƙara ta duba ta ce, "A'a wacce irin number ce wannan? Tun ɗazu ake kirana." Ɗauka tayi ta saka a speaker daga can ɓangaren aka ce, "Didi barka, Narma ce." Didi jin muryarta da suna ta sai gabanta ya faɗi ta kalli Omaar da ba ita yake kallo ba ta ce, "A'a Narma, barkan ki. Ina ta ganin kiran ashe kece ni ɗauka nake company ne duba da yanayin number." Narma ta ce, "ni ce. Ina kiran ki da layin ƙasar England ne shiyasa."

"Allah sarki, ya ki ke?."

"To gani dai kamar mai lafiya amma ba lafiya nake ba Didi."

Didi ta ce, "me ya faru kuma?." Narma ta ce, "Didi rabuwa da Faruk ba abu bane mai sauƙi a rayuwata ba, ban taɓa son wata halitta kamar yadda nake sonsa ba Didi. Har yanzu ban cire rai da samunsa ba."

Didi tayi ajiyar zuciya ta sake kallon Omar da ba ita yake kallo ba har lokacin amma ta tabbatar yana jin duk abinda ake faɗa, ta ce, "Narma addu'a zaki dinga yi itace maganar damuwarki, Allah ya kawo mafita ya yaye miki abinda yake damunki. Kin san duk abinda ya faru ba sai na faɗa miki ba, auren ki da Omar bazai yu ba, kafin ma aje ga maganar aure tarayyar ku ma baza taɓa yuwa ba. Tun farko na faɗa miki amma baki fahimta ba, yanzu gashi komai ya lalace. Kar ki sare ki ta addu'a, in kina da rabon auren sarabon zai kira ki a lokacin da zaki amsa bama ki san kin amsa ba."

Narma tayi murmushi ta ce, "haka nake ji a jikina Didi, jikina yana bani zan zama matarsa in sha Allah" sai muryarta ta fara rawa ta ce, "basu san wahalar da na sha kafin na samu ya saurare ni ba, na samu kansa daƙyar amma Dad ya lalata komai bayan ya yi min alqawarin bani duk abinda nake so."

"Ki yi hakuri" Didi ta faɗa a sanyaye cikin tausayinta. Narma tayi murmushin yaƙe ta ce, "babu komai Didi. Ya Faruk ya dawo gida? Ina fatan Lafiya?. Na Kira shi yafi a irga baya ɗaukar wayata, Ina so naji lafiya ya dawo amma laifin su Dad ya shafe ni. Ni me nayi masa Didi? Ban cancanci ya saurare ni ba?."

Jin ta fara kuka sai Didi ta tausasa murya ta ce, "Ba haka bane ba Narma, yana ƙoƙarin kiyaye abinda iyayenki suka ce ne shiyasa, amma ba wai dan yana ganin laifinki ba."

"To ko sau ɗaya ya ɗauki wayata ya yi min magana, na kira shi sau babu adadi amma baya ɗauka kuma san ya san ni ce. In ba laifina yake gani ba meyasa bazai ɗauka ba? Meyasa bazai saurare ni ba?."

Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "haƙuri dai zan ce ki yi Narma, ki ta addu'a." Narma tayi ajiyar zuciya ta ce, "shikenan Didi zan yi. Ya dawo lafiya?." Sai ta sake bata tausayi matuƙa a sanyaye ta ta ce, "ya dawo lafiya lau Narma."

"Don Allah ki gaishe min da shi in yazo, sannan ki roƙar min shi ko sau ɗaya ne ya amsa kiran wayata, Ina cikin tsananin azaba da raɗaɗin zuciya, ni kaɗai na san abinda nake ji a zuciyata Didi, ni kaɗai na san zafin da zuciayata take min akan

rashinsa. Ko sau ɗaya ne ya ɗauki wayata Didi zan ji daɗin hakan, koda bazai yi min magana ba saukar numfashinsa ya ishe ni."

Didi gabaɗaya jikinta ya gama yin sanyi ta sake kallon Omar har lokacin ba ita yake kallo ba amma shi kansa ta san yaji a jikinsa. Ta ce, "zan faɗa masa in sha Allah, ki cigaba da addu'a kin ji?."

"Zan yi in sha Allah. Sai anjima" ta faɗa tana yanke wayar Didi ta ajjiye wayar a gefe tana sauke numfashi.

Shiru bai ce komai ba itama bata ce ba, tausayin Narma ya gama mamaye mata zuciya, in ba soyayya ba wai Narma ce take wannan kalamai akan Omar ɗinta, in banda soyayya ina ruwan biri da gada? In ban da soyayya mai ya kai akuya gaida kura har raminta?. Kallon sa ta yi ta ce, "Omar Narma tana sonka, Allah sarki kaɗai ya san azabar da zuciyar take yi mata. Kaima na san kana sonta har yanzu, bamu san abinda Allah ya ɓoye ba baza mu yanke hukunci ba."

Kulle ido ya yi ya buɗe cikin mutuwar jiki amma ya dake bai nunwa Didi ba ya kalle ta ya ce, "babu wanda ya san abinda Allah ya ɓoye kam, amma bana tunanin aure ta gaskiya. Ke kin san in na wuce bana dawowa."

"Daman bai kamata ka yi wannan tunanin ba duba da abinda ya faru, amma in Allah ya rubuta ƙaddara babu wanda ya isa ya canja ta." Ajiyar zuciya ya yi ya kalle ta ya ce, "shagon aikin takalmi nake so zan buɗd" ya faɗa dan kawar da zancen Narma kar ta saka jikinsa ya yi sanyi saboda tausayinta.

Didi a sanyaye ta ce, "Da gaske?."

"Da gaske nake, Ina tattara kuɗin ne saboda hidimar aurenki da kuma buɗe shagon. Amma a yanzu haka fitar da nayi akwai wani machine na aikin takalmin dana bayar za a siyo mana shi daga lagos. Bana so abin ya ɗauki lokaci ne da wuri nake so a fara in sha Allah." Didi tayi murmushi ta ce, "Allah ya tabbatar da alkhairi, Allah ya sa albarka a neman da za a fara."

"Amin."

"Amma Omar ba da kuɗin ɣan siyasar nan zaka gina halak ɗinka ba ko?." Ya kalle ta ya ce, "ban gane ba."

Didi ta ce, "Ina magana akan kuɗin da irin su Senator suke baku dan a zubar da jini a wajan zaɓe ko a tayar da hayaniya, ba dasu zaka fara sana'ar ba ko?." Ya zuba mata ido yana kallon ta kana ya ce, "Didi daman an taɓa biyana na kashe wani ne ko na zubar masa da jini?." Ganin yadda ya kafe ta da ido yana kallo sai ta ji daɗi a ranta, hakan da ya yi ya bata tabbacin ba irin kuɗin da take tunani bane, kallon da yake mata kuma na rashin jin daɗin maganar ta ne.

Didi ta ce, "Ni ban ce an taɓa baka ba, kawai ina nusar da kai da ka gina halak ɗin ka da tsarkakan kuɗi, kar ka gina halak da kuɗin haram babu abinda zaka ɗauka a ciki." Ya ce, "ki daina yi min wannan tunanin bana jin daɗi, na san abinda nake yi. Ba a taɓa bani kuɗi dan na cutar da wani na karɓa ba, ko shi Senator ki je ki tambaye shi ban taɓa karɓar aikin tayar da hayaniya bama balle kisan kai. Tunda na wuce lokacin da nake ji da iskancina ban yi kisa ba bana tunanin akwai wata halitta da zata iya biyana dan na kashe rai. Ki daina min irin haka ban so."

Didi ta yi murmushi ta ce, "To Allah ya baka haƙuri."

"Da haƙurin ya mutu sadakar nawa ki ka bayar?" Ya faɗa yana hararta alamun ya ji haushi. Didi ta yi dariya ta ce, "Tunda dai na bada haƙuri ai sai ya wuce ba sai an faɗa min magana ba."

Ajiyar zuciya ya yi ya ce, "Ya kamata a fara siyayyar kayan aurenki ko?."

"Eh haka ne, lokaci yana ta zuwa kamar wasa. Zan sanar da kai abubuwa da ya kamata." Kai ya ɗaga kawai bai ce komai ba yana kallon wani wajan daban. Tashi ya yi ya fita ita kuma a gaggauce ta gama abinda zata yi ta fita zuwa gidan Hajja.

Hajja tana ganinta ta fara murmushi ta ce, "Aisha ke ce tafe?."

"Hajja ni ce, Ina tare da labari mai daɗi da nake so na faɗa miki." Hajja ta ce, "Ina jinki."

"Hajja Omar dai ya fara nutsuwa, Omar ne jiya yake yi min zancen na faɗa masa duk abinda yake yi mara kyau zai daina. Na faɗa masa ya kuma ce in sha Allah na ɗauka ya daina ɗin. Yanzu da ya dawo maganar yana so ya buɗe shago na aikin takalmi yake min, har ya bada kudin siyan injin aikin takalmi."

Hajja tayi murmushi ta ce, "Alhamdu lillah! Wannan labari ne mai daɗin gaske Aysha. Fahimtar kuskure sa da ya yi har yake so ya gyara babbar riba ce a rayuwarsa. Kin ga abinda nake faɗa miki ko? Na kan ce miki Omar daƙyar in ba mace ce zata yi silar nutsuwarsa ba, sai gashi ta dalilin mace abubuwa zasu canja."

Didi ta ce, "kuma na fahimci a gidan su Narma ne aka faɗa masa maganar da yake ji a zuciyarsa zai canja, ya ɗan faɗa min wasu daga ciki kaɗan amma bai faɗa min duka ba, na kuma lura maganar tana damunsa a zuciyarsa."

Hajja ta ce, "kiran rabo da kiran canjin ƙaddararsa ne ya saka shi amsawa Narma. Kar ki yi mamaki in aka ce Allah ya shigo da Narma rayuwarsa ne kawai dan ya je gidan su a faɗa masa maganar da zata farkar dashi daga dogon baccin da yake yi, kar yi mamaki in aka ce Allah ya yi haka ne kawai saboda Omaar ya nutsu ya zama mutum kamar kowa. Wataƙila amfanin Narma kenan a rayuwarsa, ta shigo rayuwarsa ta zama silar da ya je inda aka faɗa masa abinda ya saka yake ji a zuciyarsa zai canja, ya amsa kiran rabonsa ta dalilinta, wataƙila ta fita kenan bazata sake dawowa ba har abada. Wataƙila kuma zata dawo nan gaba ta kasance matsayin matarsa. Ikon Allah ai girma gare shi, sai abu ya faru zaka tabbatar da in Allah ya yi nufin shiriya a lokaci ɗaya komai zai faru ayi a gama. Kai dai ka kasance cikin addu'a ko yaushe, duk ƙanƙantar addu'a bata faɗuwa a ƙasa wallahi."

Didi tana murmushi ta ce, "haka ne wallahi Hajja, Omar ya amsa kiran rabonsa ta silar Narma." Hajja ta ce, "wataƙila matarsa tana gefe zata shigo rayuwarsa ta wata fuskar, wataƙila kuma Narma ɗin ce matarsa, duk abinda iyayenta zasu yi sai dai su yi su gama amma sai ta aure shi. Allah ai ba abin wasa ba ne ba, in Allah ya rubuta babu wanda ya isa ya canja, In kuwa kaga ya canja to daman haka abin yake a cikin ƙaddararsa." Didi ta ce, "Wallahi Hajja na yi farin ciki, daɗi nake ji sosai zuciyata wallahi."

Hajja ta dafata ta ce, "zaki fi kowa jin daɗin canjin Omar a yanzu, ke kaɗai ce uwa, uba, yaya, ƙawa, ƙanwa a gare shi. Allah ya baki lada Aisha, ya jiƙan iyayen ku, ya ɗorar da zumunci da ƙaunar da ku ke yiwa junan ku har aljanna."

"Amin Hajja. Amma yarinyar nan Narma tana bani tausayi, yanzu ta kira ni tana kuka kina ji kin san ba ƙaramin so take yiwa Omaar ba. Abin har mamaki yake bani, ta rasa wanda zata yiwa wannan soyayyar mai zafi sai Omar, dole iyayenta su ce asiri ya yi mata."

Hajja ta yi dariya kaɗan ta ce, "ita Narma ƙaddararta kenan soyayyar Omar, in Allah ya rubuta matarsa ce kamar yadda na faɗa miki iyayenta basu isa su hana ba, duk matsayin da take dashi zasu manta su bashi aurenta. In kuma ba matarsa bace Allah zai sassauta mata abinda take ji tayi aure ta huta. Babu mamaki a cikin ikon Allah Aisha, bayan Narma sai ki ga Allah ya sake kawo wata da zata sake haukacewa akan soyayyarsa. Komai yana da sila, hatta mutuwa tana da sila, shi Omar silar soyayyar da Narma take masa ne ya saka ya amsa mata har yaje gidan su, ashe zuwa gidan na su shine silar canjawasa."

Didi ta yi ajiyar zuciya ta ce, "Allah ya sa mu dace, Allah ya tabbatar dashi akan tafarkin halak."

"Amin Aisha." Didi ta kalli Salma da take ta murmushi ta ce, "Salma zaki raka mu Kaduna jibi in sha Allah, zamu je mu yiwa Abiy godiya har cikin gida." Salma ta ce, "gidan su Nayla?" Ta faɗa tana wara idanu. Didi ta ce, "can zamu je, amma kar ki faɗa mata Ina so mu bata mamaki. Ki dai san yadda zaki yi ki tabbatar da Abiy yana nan zamu je a ranar mu dawo."

Salma ta yi dariya ta ce, "in sha Allah. Allah ya kaimu." Ta amsa da amin Hajja ta ce, "Allah ya kaimu."

"Amin Hajja. Me ki ka san yana so da zamu siya daga nan mu kai masa?." Hajja ya ce, "kar ki takura kan ki Aisha, iya zuwan da zaki yi ya wadatar." Didi ta ce, "A'a Hajja, ai ya wuce na je gidan haka babu tsarabar Kano. Me zan tafi dashi?."

Salma ta ce, "yana son gurasar Kano, musamman ta gidan gurasa na nan baya, zaki iya yi masa ita kaɗai ta isa. Dan indai Nayla tazo Hajja tana bayarwa a kai masa. Didi ta ce, "na gode Salma, zan saka a yi sabuwa wacce zamu karɓa da safe sai mu tafi." Hajja ta ce, "Allah ya kaimu, sai ku je Sayyadi ya kai ku." Didi ta ce, "To Hajja, na gode Allah ya ƙara girma." Suka amsa da amin kafin ta ce, "Hajja sai magana ta gaba."

Hajja ta ce, "ina jinki." Didi ta ce, "magana ce akan kayan ɗaki da za a siya, Baba Adamu ya kira ni ya tabbatar min da shi ne zai yi komai na aurena, hatta cokali baya so na siya shi ne zai siya da kansa. Kawai abinda yake so na bashi makullin gidan zai zuba duk abinda ya kamata ace an zuba."

Hajja da fara'a ta ce, "kai amma ya kyauta, Allah ya bar zumunci." Didi ta ce, "amin Hajja. Babbar matsalar itace Omar, in yaji Baba Adamu ne zai yi komai wallahi bazai bari ba, in kuwa ya haƙura ya bari to sai raina na dana Baba Adamu ya ɓaci. Yanzun nan kafin na fito maganar kayan yake min sai na ce masa zamu yi magana, na rasa ta yadda zan faɗa masa saƙon Baba Adamu shima kuma Baban baya so Omar ya sani saboda tijarar Omaar. Ya dinga faɗa kenan yana cewa an faɗa musu bashi da kuɗin da zai yi min komai ne, kai lefe ma da nace an kai gidan kawu ya yi min shiru ne amma zai nuna min yaji haushi nan gaba."

Hajja tayi dariya ta ce, "Omar kenan, Omar mazan fama, Omar carbin ƙwai, ya ci sunan nasa damisa kamar yadda ake faɗa masa." Didi ta ce, "wallahi na rasa abinda zan yi, ga makullin ya aiko min dashi amma na masa faɗawa Omar saboda saƙon Baba. Shiyasa nazo na same ki don Allah ki kira shi ki ce masa kece kika ɗauki nauyin abinda Baba zai yi, yana ganin girmanki sosai, ke kaɗai ce kaf duniya zan ce kin yi bazai musa ba, duk da zai yi magana amma ƙarama ce shikenan ya wuce. In na ce Baba Adamu ne ranar sai kowa ji kan mu dashi."

Hajja ta ce, "shikenan kin kawo dabara. Ki bawa kawun na ki makullin ni ki turo min shi in anjima. Kar ki damu ai an wuce wannan matsalar." Didi tayi murmushi ta ce, "Na gode Hajja. Kin kasancewa uwa a gare ni kuma kakata, bani da mai share min hawaye a duniya sai ke ɗin kawai. Allah ya shirya miki zuri'arki gaba da baya." Hajja ta yi murmushi ta ce, "Amin. Aisha ai an zama ɗaya kar ki damu." Didi tana ta murmushi suka ɗan cigaba da hira kafin ta tashi ta koma gida.

Washe gari da safe take sanar masa da Hajja na son ganinsa, ya ɗan yi jimm yana kallon ta kafin ya ce, "lafiya take son ganina?." Didi ta ce, "Omar

ya za a yi na sani? Ta ce min kawai na ce kaje." Ya ɗan ɗauke ido daga kallon ta ya ce, "to in na fita yanzu zan shiga." Bata sake kula shi ba kar tayi magana ya gano sai tayi shiru ta cigaba da aikin ta.

Kamar yadda ya ce da ya fita kam gidan Hajjan ya shiga da sallama, mai aikin Hajja ta amsa ta ce ya shiga ciki Hajjan tana ciki. Hajja ita kaɗai a zaune tana lazumi, ta amsa sallamar ya zauna sai ta ajjiye carbin suka gaisa ta ce, "Ummaru daman na ce kazo ne akan batun kayan ɗakin Aisha na aure. Na karɓi makullin gidan da Aisha zata zauna a hannunta, ni nake so nayi mata komai na ɗaki a matsayina na uwa a gare ku. Shiyasa na ce ta turo min kai na faɗa maka da kaina kar ka ji hakan a bakin ta bai maka daɗi ba."

"Ina kallon ku matsayin jikokina ne, Aisha ta ɗauke ni kamar uwa tana faɗa min duk damuwarta. Ana zaman mutunci da amana shiyasa zan sauke haƙƙin da yake kaina matsayin uwa a gare ta. Ina fatan hakan bazai ɓata maka rai ba." Shiru ya yi bai amsa ba Hajja ta ce, "Ummaru baka ce komai ba." Ya kalle ta ya ce, "babu abinda zan ce, tunda an yanke hukunci shikenan." Hajja tayi dariya kaɗan ta ce, "an yanke kam, sanar da kai yanzu ma nayi ba neman shawara ba."

"Shikenan, an gode Allah ya saka da alkhari" ya furta a kasalance dan bai ji daɗi ba. Hajja tana lura da yanayinsa tana girmama ƙarfin hali irin na Omar, da gaskiyar Aisha da ta faɗa masa asalin su waye suka yi da babu zaman lafiya.

Sallama ya yi mata ya fita ya koma wajan Didi ya shiga har cikin ɗakinta ya samu tana mopping a lokacin. Kallon sama da ƙasa ya yi ya ce, "Daman abinda aka tsara kenan shiyasa baki faɗa min dalilin kiran ba?." Didi ta ce, "Shiyasa na ce ta faɗa maka da kanta."

"Ai wallahi tunda naga kin kasa kallona kafin na fita na san akwai munafurcin da kika haɗa, da farko nayi tunanin akan waɗancan makiran ne ashe sabuwar gulma ki ka samo hanyar ƙullawa." Didi tana jinsa bata ce komai ba sai ma dariya da yake so ya bata.

Omar ya fusata ya ce, "Ni fa bana son shishshigi a cikin lamarin rayuwata, an ce mata bani da kuɗi da zan iya yi miki ne da za a yi miki a waje?. Ba dangin iya babu na baba a ce itace tayi miki kayan ɗakin auren ki haka daidai ne?. Salon nan gaba azo na yi min gori ace kayan ɗakin Yayata ma maƙota ne suka yi mata saboda na gaza?."

Didi ta kalle shi ta ce, "Omar kyautatawa ce fa ba wani abu ba." A fusace ya ce, "Allah ya tsinewa kyautatawar!." Didi ta yi shiru jin abinda ya ce. A kausashe ya ce, "in kyautatawar ce a yi ta wani ɓangare mana lallai sai ta kayan ɗaki? Yanzu kaf unguwar nan sai a san itace tayi ko dan a faɗa, ni kuma a cigaba da yi min kallon mara amfani tunda ni Allah ya ɗorawa yi miki ba wasu a waje ba."

Shiru tayi masa bata tanka ba kar ta tanka ta sake tsokano shi, ta san halin kayanta tsaf shiyasa take gujewa abinda zata sake tunzura shi. Shirun da tayi ma bai saka ya yi shiru ba ya ce, "wai komai na kayan ɗaki ita zata yi ko a matsayin ta na wa

oho?. Nuna min ake yi ni bani da kuɗin da zan yi kenan? ko ke kika ce mata bani da kuɗin da zan yi miki ita tayi miki?."

Didi a sanyaye ta ce, "ni bamu yi haka da ita ba, abinda ta faɗa maka shi ta faɗa min." Omar ya yi ƙaramin tsaki yana binta da harara ya ce, "To meyasa baki ce mata zan miki ba? Meyasa kika amince har ki ka ce ta faɗa min da kanta?. Kenan kina tunanin bazan iya ba ko?." Didi ta yi ajiyar zuciya ta ce, "Nidai ban ce ba."

"Mtsw! Na rantse da Allah ba dan Ina ganin girmanta baza'a karɓi kayan nan ba, to babu yadda zan yi mata ne amma da sai ta bar kayanta ai ba roƙa muka yi ba." Shiru Didi ta sake yi masa ta cigaba da aikin ta bata ce komai ba ya sake yin tsaki ya ce, "Abin haushi." Ita dai bata ce masa komai ba tana mamaki hali irin na Omar a zuciyarta, tabbas da ace ya san Baba Adamu ne ya yi ba Hajja ba da sai an yi yaƙin duniya na uku saboda bala'i da masifar da zai dinga zazzagawa kowa.

Juyawa ya yi ya fita ta bishi da kallo ta ce, "Na kuɓuta. Alhaji Omar manya, Allah ya shirya ka ya taimake ka a rayuwarka" ta faɗa tana cigaba da aikinta tana dariya da tunanin irin kalar tizajarar da zai yi mata in ya san asalin su waye zasu yi kayan ɗakin.

Haka ya wuni rai a ɓace, ko kula ta ma bai yi saboda baya son maganar, gani yake kamar an raina masa hankali ne da za a ce wata a waje ce zata yi kayan ɗakin yayarsa ba shi ba. Ita kuma tana sane ta share shi, tana yin magana zai sake yin sama ƙarshe ma ya ce zai je ya samu hajja ya ce gaskiya bai yarda ba shiyasa ta yi masa banza.

Washe gari ƙarfe bawai na safe ta buga masa ƙofa, da yake bacci yake yi a lokacin sai ya taso yana cewa, "Didi kin san ƙofar a buɗe take amma sai ki ta buga min ƙofa kin san na tsani a buga min ƙofa amma sai kin yi, lafiya?." Didi ta ce, "na san a buɗe take ai, shigowa ne bazan yi ba. Ka tashi ka yi wanka ƙarfe takwas zamu wuce." Ya kalle ta ya ce, "Zuwa Ina?." Hararsa ta yi ta ce, "ban sani ba, ka koma ka kwanta in ka manta" ta faɗa tana wucewa ta ƙyale shi. Ƙaramin tsaki ya yi, dan kawai ya san mahimmacin alkhairi ne da bazai je ba wallahi.

Wanka ya yi ya shirya cikin ƙananun kaya a lokacin Didi ta fito daga falo shi kuma ya fito ta kalle shi ta ce, "Omar don girman Allah ka koma ka saka manyan kaya, ba

dan ni ba, don Allah ka saka manyan kaya har hula ka saka." Bata barshi yayi magana ba ta dinga magiya dole ya koma tunda ba son magiya yake yi ba, ba jimawa ya dawo da shadda kalar blue mai haske har hula ya saka kamar yadda ta ce.

Murmushi tayi tana kallon sa ta ce, "Ko kai fa. Ka ci abinci sai mu wuce." Shayi kawai ya sha aka kawowa Didi saƙon gurasar da ta bayar ayi, duk yana kallo ta juye a babban bokitin roba sabo dal da ta siya. Kallon sa ta yi ta ce, "ranka ya daɗe in in ka gama sai mu tafi ko?."

"Ki jira na je na samo mai motar da zai kai mu ko?."

"Ai da driver Hajja zamu tafi." A kaikaice ya kalle ta ya ce, "Hajja dai?." Didi ta ce, "eh Omar, ita tace zata saka ya kaimu bazan ce mata a'a ba."

"Daman ai komai baza ki iya ce mata a'a ba tunda ga wacce ta haife ki, wallahi da na san haka ne bazan je ba."

"Shiyasa ban faɗa maka ba, mu je" ta faɗa tana fita ta bar shi kar tayi wani abun ya ce ya fasa.

Ransa a ɓace ya fito zuwa ƙofar gidan ya kulle gidan ya tarar da driver Hajja ya fito da motar ga Salma a tsaye a jikin motar da alama tare zasu je. Ƙaramin tsaki ya yi lokacin su Bashir suka zo wajan ya tsaya yana yi musu magana, Didi ta shiga motar shima bai jima ba ya ƙaraso ya shiga gaba su kuma daman baya suka shiga, motar ya yiwa key bayan sun gaisa da Omar da Didi suka ɗauki hanyar Kaduna ransa duk a ɓace.

KRB2P0011

Arewabooks@nanahaleema11.

Sha ɗaya da mintina na safe suka shiga Kaduna, da yake gidan su Nayla ba baƙo bane a wajan driver Hajja ba ɓata lokaci suka isa har ƙkofar gidan ya tsaya yana danna horn. Didi kallon gidan ta ke yi tana girgiza kai, domin gidan yana da matuƙar girma da kyau. Duk da bashi da ƙyale-ƙyale daga waje amma kana gani ka san gidan babban mutum ne ba gidan yaro matashi ba. Ko iya masu gadin da suke zaune a gate ɗin sun kai su biyar ko wanne da uniform kalar blue a jikinsa.

Ganin driver Hajja ya saka aka buɗe musu gate na farko a nan suka ajjiye motar. Bayan ya faka Salma ta ce, "Mu je ciki" ta faɗa tana fitowa tana ɗan jijjiga hannunta dan ta gaji da zaman. Omar dai bai fito ba yana zaune Didi ta kalle shi ta ce, "ka fito mana." Ya kalle ta ya ce, "Sai na shiga gidan mutane babu izini? Ku je dai." Didi ta saki baki tana kallon sa ta ce, "ikon Allah! Sabon salo."

Salma tayi dariya ta ce, "Didi mu je zai shigo daga baya." Didi tabi bayan Salma suka sake shiga wani gate ɗin a nan wani mahaukacin parking space yake mai bala'in girma wanda aka tanadi rumfuna daga can gefe na ajjiye mota.

Didi kallon gidan take tana girmama girmansa da kuma ƙarfin kirki irin na Nayla. Wanda ya fito daga wannan gida ba kowa ne zai yi mutunci har ya kalli na ƙasa dashi ba. Ciki suke shiga Didi ta ga sai tafiya suke yi kafin a buɗe wata babbar ƙofa su shiga sai gasu a wani babban falo mai bala'in kyau.

Babu kowa a falon sai mai aiki tana kunna turaren wuta Salma ta kalle ta ta ce, "Ina Mama da Nayla?." Ta ce, "Mama tana ciki, Nayla kuma tana sama bata sakko ba gabaɗaya." Mama ce ta fito tana cewa, "waye yake nema na?." Ganin Salma sai tayi murmushi ta ce, "A'a Salma, ke ce tafe?." Salma tayi dariya ta ce, "Ni ce Mama." Zama suka yi har Didi suka gaisa da fara'a kamar ta san Didi kafin Salma ta ce, "Didi ce Mama, na san kina jin labarinta a bakin Nayla." Sai Mama ta sake yin dariya ta ce, "ƙwarai kuwa in jin labarin Didi maƙociyar Hajja ko?." Salma ta amsa ta ce, "itace. Ta zo wajan Abiy ne."

Mama ta ce, "ai kuwa yana falon sa kuma fita zai yi, maza jeki ki rakata dan na ji yana cewa cikin Zaria zai shiga, kuma ya kai yamma ko dare bai dawo ba." Salma ta miƙe tana cewa, "Nayla fa?." Mama ta ce, "tana sama yau ko sakkowa ma bata yi ba, bata jin daɗi shiyasa ko aiki bata je ba. Jeki zan tasota sai tazo ta same ki." Tare suka fita da Didi da Salma. A harabar gidan wani ɓangaren daban suka shiga, Salma ta buɗe ƙofar da ta san nan ne falon Abiy na waje.

Ai kuwa yana zaune shi kaɗai da alama ya gama cin abinci suka shiga falon da sallama, Jawad ne ya fito daga kitchen ɗin falon da ruwa a hannunsa ya ajjiyewa Abiy a gaban sa. Abiy ya amsa sallamar sai ya murmusa ya ce, "A'a Salma, ke ce tafe?." Salma ta ƙarasa ta zauna a kan carpet ta gaishe shi ya amsa yana tambayarta Hajja da Daddy ta ce duk suna lafiya lau. Da Didi suka gaisa lokaci ɗaya

ya gane ta, Salma ta ce, "Abiy Didi ce." Abiy ya ce, "Aisha dai, Ai na gane ta." Didi tayi murmushi tana sunkuyar da kai.

Salma ta ce, "ta ce na rakota wajan ka shiyasa muka taho yau. Tare mu ke da Omar ƙaninta ma yana waje a tsaye." Abiy ya ce, "yana waje a tsaye? Kun yi wannan doguwar tafiya a barshi a waje? Jawad jeka ku shigo tare." Jawad ya tashi ya fita ba jimawa suka dawo tare da Omar harda driver Hajja. Gaisawa suka yi da Drivern kafin ya tashi ya fita Omar ya gaishe da Abiy cikin yanayin sa na kadaran kadahan.

Abiy da murmushi yana kallon sa ya ce, "Lafiya lau Omar, ya hanya?."

"Alhamdu lillah" ya amsa a taƙaice dan jinsa yake a takure. Wani irin girma yake ji Abiy ya yi masa a jikinsa da zuciyarsa, shiyasa gabaɗaya ya kasa sakewa ya kuma kasa haɗa ido da Abiy.

Didi ta ce, "Abiy mun zo mu yi godiyar alkhairin da aka yi mana, Allah ya saka da alkhairi ya biya ka da aljanna. Babu abinda zamu saka maka dashi sai addu'a. Ga Omar ya dawo cikin alfarmarka, Allah ya sa a fi haka, Allah ya kare ka, Allah ya shirya maka zuri'arka, Allah ya ƙara maka lafiya da tsahon rai mai amfani." Abiy yana ta murmushi cikin jin daɗin addu'arta ya ce, "Amin ya rabbi. Tun daga Kano har Kaduna ku ka taho?."

Didi ta ce, "ai ya zama dole ne, dole mu zo mu yi godiya."

"Har gida kin je kin yi min godiya a lokacin, sai da ku ka sake ɗauko hanya ku ka zo?." Didi ta yi murmushi Abiy ya ce, "Babu komai ai yiwa kaine. Kuma kafin na taimaki Omar ai shi ya taimake ni, na rama alkhairi da alkhairi ne kawai."

Omar wani iri yake ji a jikinsa, ba saba yiwa mutane godiya ya yi ba balle ya san irin addu'ar da zai musu, duk sai ya rasa abinda zai ce yake jin bakin sa kamar an ɗaure tamau. Gashi yana ji a jikinsa ya kamata yayi magana amma ya rasa me zai ce. Zai yi magana kenan Nayla ta shigo falon ba tare da ta lura da Didi ko Omar ba, a shagwaɓe ta shigo ta san Abiy yana nan dan kawai Mama ta ce mata Abiy na kiranta bata san su waye a ba.

"Abiy" ta faɗa tana ƙarasowa inda yake. Ya kalle ta ya ce, "Mamana kin tashi? Tun ɗazu aka ce bacci ki ke yi, ya zazzaɓin?" Ya faɗa yana riƙo hannunta ya zaunar da ita kan kujera yana taɓa wuyanta. Abiy ya ce, "har yanzu jikinki da zafi. Mamana baki da lafiya gaskiya yana da kyau ki ga likita, gabaɗaya kin rame sai yawan ciwo a kai akai-akai. Zan yi magana da likitan da zaki gani ki je gobe ya duba ki a san abinda yake damunki. Jiya Maman ki ta ce min harda ciwon ƙirji ko?." Kai ta ɗaga alamun eh har lokacin idanunta a lumshe yake kafin ya ce, "Jawad gobe zai kai ki wajan likita, na lura kece bakya son zuwa."

"Hajiya Nayla" Salma ta furta tana kallon ta. Da sauri ta buɗe ido tana kallon mutanen da suke zaune a falon. Dam! Gabanta ya buga haɗa ido da suka yi da Omar da yake zaune daga gefe ya ɗago kenan suka haɗa ido. Wara idanu tayi ta kalli Abiy ta sake kallon su Salma ta ce, "Salma, Didi?." Didi tayi murmushi ta ce, "Na'am Nayla." Sai kuwa tayi ihu ta tashi a guje ta koma kusa da Didi ta ce, "Didi yaushe ku ka zo? Shine ba a faɗa min ba?. Wai ko mafarki nake yi ne?."

Didi ta ce, "ba mafarki ki ke yi ba Nayla, ni ce yau a Kaduna." Nayla ta ce, "ikon Allah. Kuma Mama bata faɗa min ba fa, ta ce min kawai Abiy yana nemana, ashe ku ne kuka zo. Sannu da zuwa."

"Yauwa Nayla, ya jikin na ki?."

"Da sauƙi" ta faɗa tana sauke da ido ƙasa farin ciki yana mamaye zuciya ta ganin masoyin ta a zaune a falon gidan su.

Abiy da yake kallon ta yana murmushi ya ce, "ki tashi ki je ki saka a haɗa musu breakfast sun yi tafiya mai nisa." Mama ce ta shigo falon da sallama ta ƙaraso ta zauna suka sake gaisawa da Didi shi dai Omar bai iya kallon ta ba sun gaisa kawai dan in akwai abinda ya tsana bai wuce gaisuwa ba.

Abiy ya kalli Mama ya ce, "wannan shine wanda ya taɓa taimakon Nayla a Kano shekarun baya....Kin tuna?." Mama ta ce, "Allah sarki na gane shi." Didi ta bawa Mama abinda ta taho musu dashi Abiy ya ce, "harda wahala? Ku da ku ka yi tafiya mai nisa har sai an yi tsaraba?." Didi murmushi ta ke yi ta ce, "Babu komai Abiy." Abiy ya ce, "mun gode sosai, Allah ya bar zumunci."

Didi ta amsa da amin tana murmushi, ta ji daɗin yadda Abiy ya karɓe su wallahi, ta kuma fuskanci gadon kirki Nayla tayi daga wajansa. Mama ta kalli Nayla da ta

kwantar da kanta a kafaɗar Didi tana kallon Omar ta gefen idanu ta ce, "Nayla ki je ki saka a haɗa musu abinci su ci ko?." Nayla ta ɗago a sanyaye ta ce, "To Mama." Abiy ya ce, "Mamana jikin ne?." Ta girgiza kai ta ce, "A'a Abiy, murnar ganin Didi ce kawai."

"To maza ki je a haɗa musu abinci, sun yi doguwar tafiya."

Bata miƙe ba gani take in ta tafi bazata cigaba da kallon Omar ba, shi kam ko kallon inda take ma bai yi ba balle ya yi magana. Abiy ya ce, "amma dai sai gobe zaku koma?." Didi ta wara idanuta ce, "A'a, anjima kaɗan zamu koma in sha Allah." Abiy ya ce, "Toh, ai na ɗauka zaku kwana ku huta gajiya ai. Shikenan ni daga nan zance ya kiyaye hanya, zan shiga Zaria bazan dawo na zame ku ba gaskiya. Allah ya kiyaye hanya na gode da girmamawa." Omar ne ya buɗe baki kamar mai koyan magana ya ce, "Amin. Mun gode sosai, Allah ya ƙara girma."

Lumshe ido Nayla tayi jin kalaman Omaar idanunta suna cika da hawaye saboda tsantsar bugawar da zuciyarta take yi. Salma na lura da ita haka Mama duk motsin ta akan idanunta take yi. Abiy ya ce, "amin Omar, Na gode sosai. Mamana ki raka su falo su huta." Nayla ta amsa ta miƙe ta ce, "Didi ku zo mu je" ta faɗa a sanyaye. Didi ta miƙe Salma ma ta miƙe Abiy ya ce, "Omar ku je tare, Jawad raka shi zai fi sakewa." Jawad ya amsa yana miƙewa shima suka shiga ciki.

Ƙaramin falon baƙi aka shigar dasu mai kyau madaidaici. Nayla ta kunna a.c bayan ta kunna hasken falon ta fita daga falon ita da Salma. A kitchen Salma take ce mata, "Nayla don Allah ki nutsu, sai rawar jiki ki ke yi kina bayyana feeling ɗinki a fili." Sai kawai ta rungume Salma ta fashe da kuka tana cewa, "Salma Omar ne a gidan mu, Omar ne a zaune shaida Abina suna magana. Salma na kasa tantance adadin farin cikin da nake ji, ji nake kamar zuciyata zata buga saboda murna Salma. Omar ɗina yana nan lafiya, Allah na gode maka, Allah na gode maka" ta faɗa cikin kuka sosai.

Salma ta ce, "to ki yi haƙuri ki bar kuka mu kai musu abincin in ya so sai mu yi magana." Nayla ta ɗago daga jikin Salma tana share hawaye ta ce, "Salma ki yi addu'a Allah kar ya ɗora miki soyayya irin wacce ya ɗora min, akwai azaba ba kaɗan ba Salma. Na kasa yin lafiya cikin kwanakin nan kuma duk saboda tunaninsa." Tausayi ta bawa Salma matuƙa, idon Salma ya kawo ruwa amma bata yi kuka ba ta daure ta yi mata shiru bata tanka mata ba.

A haka suka zuba abincin a flaks, doya ce da ƙwai da sauce sai dankalin turawa soyayaye da kuma soyayyen ƙwai. Ga farfesun naman rago da aka yi shi mai ruwa, sai shayi da manyan slice bread da gwangwanin madara da na milo da sugar.

A kan table suka ajjiye sannan Salma ta koma ta kawo ruwa da lemo masu shegen sanyi ta ajjiye. Didi ta kalli Nayla da take tsaye kana ganin ta ka san tayi kuka ta ce, "Nayla jikin ne?." Nayla ta kalli Didi ta ce, "A'a Didi, kaina ne yake ciwo shiyasa."

"Sannu, Allah ya ƙara lafiya. Ki je asibiti a duba ki." Kai kawai ta ɗaga dan ƙirjinta ya yi mata mugun nauyi, ga Omar dai tana kallonsa amma kewarsa take ji kamar ta je ta rungume shi haka take ji.

Shi kuwa Omar yana jin su amma baya ɗagowa waya yake dubawa ba tare da yana yin wani abun a wayar ba. Fitar Salma da Nayla ya saka Didi ta ce, "kai kuwa Omar ko sannu ai ka ce mata ko? Itace silar fitowar ka daga hannun Sen na faɗa maka. Ko ya jiki ai ya kamata ka ce mata zata ji daɗi." Shiru ya yi bai ce komai ba, gabaɗaya a takure yake jin kansa cikin jin nauyi wanda bai san dalilin faɗuwar hakan ba.

Salma da Nayla sun jima basu dawo ba har kusan mintina talatin kafin su dawo, Didi ce kawai ta sha tea amma shi ruwa kaɗai ya sha bayan nan bai sake ɗaukar komai ba.

Nayla ta kalli Didi ta ce, "Didi har kin ci?." Didi ta ce, "na sha tea Nayla, in zan yi tafiya bana son cin abinci wallahi." Nayla tayi murmushi tana satar kallon Omar da ya ajjiye ruwan da ya sha a lokacin.

"Yaushe zaki zo mana Kano?." Nayla ta kalli Didi ta ce, "ai sai bikinki, aiki ya saka ni a gaba ya hana ni zuwa ko ina. Ni dana sanin ma fara aikin nake yi wallahi."

Didi tayi dariya ta ce, "Allah ya kaimu, ya taimaka miki." Ta amsa da amin wajan ya yi shiru babu mai magana. Didi ce ta sake cewa, "Salma an kaiwa driver abincin?." Salma ta ce, "na tabbatar ma ya cinye yanzu." Didi ta yi murmushi suka sake yin shiru. Ƙarar wayar Nayla ce ta katse shiru ta kalla ta ga Abbas ne ta kalli Salma ta ce, "Yayanki ne." Salma tayi dariya ta ce, "yayan mu dai, kema ai yayanki ne. Baza ki ɗauka ba?." Nayla ta ce, "ana babbakar giwa waye zai je ƙaure zomo?."

Salma ta murmusa cikin tausayin yar uwarta ta ce, "Gaskiya ne." Didi ta kalli Nayla ta ce, "Nayla zan shiga banɗaki." Salma ta ce, "mu je na raka ki." Didi ta miƙe ta fita

ita da Salma aka bar Omar kawai da Nayla a zaune. Wani irin yarrr Nayla take ji a jikinta, gashi dai kamar bai san tana zaune ba amma wani irin suka zuciyar take yi ga farin ciki da yake mamaye zuciyarta. Ganin ba ita yake kallo ba kawai sai ta zuba masa ido tana kallon sa cikin shauƙi ko ƙifta ido bata yi.

Waya ta ɗauka kamar tana dubawa tana yi masa video ta yadda bazai fahimta ba. Omar kuwa shi kansa wani iri yake ji, ya na kallon su har fitar su Didi ya kuma san tana zaune ita a falon. Wani iri yake ji a jikinsa kamar taɓa zama da mace shi da ita kawai ba. Duk da dai akan Narma kawai ya faru amma sai yake jin wannan daban kamar bai taɓa shiga irin yanayin da yake ji ba.

Hannunsa ta kalla ta kuwa yi farin gani, domin azurfar da ta bashi tana sanye a ɗan yatsansa na biyun ƙarshe a hannun haggu. "Wayyo Allah!." Ta furta bata san ta ce ba saboda farin cikin da ya sake mamayeta. Jin abinda ta furta sai ya ɗago ido yana kallonta a lokacin ta rufe ido ita kuma saboda tsananin farin ciki. Ɗauke kai ya yi ita kuma ta buɗe ido, gabaɗaya ta kasa sarrafa kanta ƙiris take jira ta fita daga hankalinta

Didi da Salma ne suka dawo Didi ta kalle ta ganin sai murmushi take yi ita kaɗai sai ta kalle shi taga babu alamun ma sun yi magana da ta san hali. Mamakin murmushin Nayla take yi saboda ta san tsoron Omar take ji, amma yanzu gashi an bar su su biyu tana ta murmushi mai kyau.

Nayla ta kalle ta ta ce, "Didi mu je ɗakina ki kwanta ki huta." Didi tayi dariya ta ce, "Sallar azahar kawai zamu yi mu juya, kwanciyar me zanyi gashi har sha biyu da rabi tayi?." Nayla ta ce, "kai Didi, ni na ɗauka sai yamma."

"Gwara mu shiga Kano kafin duhu ya yi Nayla." Nayla ta girgiza kai tana ta murmushi abin ta kamar sabon kamu. Omar dai baya magana Didi sai girmama hali irin na sa take yi, yazo har gidan su yarinya amma ya kasa ce mata ya jiki bayan a gabansa aka ce bata da lafiya.

Salma ta ce, "Didi mu je ɗakin Nayla ki yi alwala ki yi sallah." Didi ta amsa da to Nayla dai bata son tafita amma haka ta miƙe a lokacin Jawad ya shigo ya zauna yana ɗan jan Omar da hira duk da bai sake ba. Nayla bata so barin wajan ba, haka suka shiga babban falon suka hau sama har ɗakin Nayla.

Didi girmama gata irin na Nayla take yi, musamman yadda Abiy ya ruɗe akan ciwon ta ga kuma girman ɗaki kamar baza tayi aure ba. A nan suka yi sallar azahar suna ta hira da Didi, duk da ta lura Nayla bata cikin walwala dawowar su ɗakin amma bata tambaya ba.

Bayan an idar da sallama suka sakko suka haɗu sa Mama ta bawa Didi kaya a leda sannan ta bata kuɗi ta ce in ji Abiy ya ce su yi kuɗin mai. Ta dinga yi mata godiya sosai, Nayla ta riƙe mata kayan ita da Salma suka fito har bakin motar.

A tsaye suka tarar da Omar shida driver da alama su suke jira. Didi ta buɗe motar sannan ta kalli Nayla ta ce, "Nayla baƙo zai yi halin sa, Mun gode da karrmawa Allah ya bar zumunci." Nayla ido ya ciki da hawaye ta ce, "Amin Didi. Allah ya kiyaye hanya." Salma ta riƙe hannunta tace, "Nayla meye na kukan?." Sai ga hawaye shar ya sakko mata, ta juya da sauri ta rungume Didi ta ce, "bana so ku tafi Didi, don Allah ku kwana." Omar da yake jin me cewa ya kalle ta yana mamaita su kwana, Lallai ma yarinyar bata da hankali.

Didi ta ce, "Nayla banda abin ki meye na kuka kuma? Ki yi haƙuri wata ran ai zan dawo in sha Allah." Nayla ta ɗago daga jikinta ta ce, "to Didi. Wallahi bana so ku tafi, ji nake kamar na bi ku."

"Ki yi haƙuri kin ji? Ai zaki zo Kano ɗin ko?." Ta ɗaga kai kamar yarinyar ƙarama Didi ta ce, "to kin gani, ki yi haƙuri kar ki saka ni kuka nima." Nayla ta goge ido ta ce, "Allah ya sauke ku lafiya."

"Amin Nayla. Allah ya baki lafiya, ji ke ki ga likita gabaɗaya kin canja kin rame kamar ba ke ba."

Nayla ta ce, "to Didi zan je in sha Allah." Didi ta shiga mota Salma ta riƙe Nayla ta ce, "ki yi haƙuri ki ta addu'a, canji zai zo daga wajan Allah."

"Ina yi Salma, kema ki dinga yi min."

"Ina yi miki kullum Nayla, Allah ya sassauta miki. Ba dan ban cewa Daddy zan kwana ba ai da nayi zamana na ɗebe miki kewa. Amma zan dawo." Ta ɗaga kai kawai tana kallo Salma ta shiga motar.

Kallon inda Omar yake tayi suka haɗa ido dan kallon ta ya ke yi yana tunanin meyasa yake yawan ganinta tana kuka, shagwaɓa ce ko sangarta ko rashin hankali?. Ganin sun haɗa ido sai tayi murmushi idonta duk hawaye ta ce, "Allah ya kiyaye hanya….Yaya Omar!.." Wani iri yaji a zuciyarsa, mace ta farko da ta taɓa ce masa Yaya kenan a rayuwarsa. Sai yaji wani irin rauni da bugun zuciya, har lokacin kallon ta yake yi hawaye suna sakko mata daga idonta.

Samun kansa ya yi da yin murmushi ya ɗaga kai ya ce, "Amin, Mun gode" daga haka ya buɗe motar ya shiga. Ai Nayla suman tsaye tayi a wajan saboda gigicewa. Na farko murmushin da ya yi mata, na biyu maganar da ya yi, na uku godiyar da ya yi mata sai take ji kamar an yi mata babban albishir.

Horn ɗin motar ne ya saka ta dawo hankalinta, ta share hawaye tana dariya tana kuka ta ɗaga musu hannu suka fita daga gidan ita kuma ta juya a sanyaye ta koma cikin gida.

KRB2P012

Arewabooks@nanahaleema11.

Sai la'asar suka shiga Kano, Didi sai da ta shiga wajan Hajja ta bata labarin duk abinda ya faru har kayan da Mama ta bata da kuma kuɗin da Abiy ya bayar ta nuna mata. Hajja ta dinga murmushi dan ta san daman baza ta ji kunya ba dan Didi ta je gidan su Nayla ba, saboda kirkin Abiy da matar gidan. Dubu hamsin ta lissafa a dubu ɗari biyun da Abiy ya bayar ta bawa Salma ta ce, "Salma ga na saka data." Salma tayi dariya ta ce, "Haba Didi, wallahi bazan karɓa ba, na gode sosai."

Didi da mamaki ta ce, "Meyasa baza ki karɓa ba?."

"Haba Didi, dan na raka ki sai kin bani kuɗi? Wallahi bazan karɓa ba." Didi ta ce, "to ki bawa Sayyadi driver Hajja ya saka kati." Salma ta karɓa ta ce, "zan bashi in sha Allah." Didi ta dinga godiya sannan ta tashi ta shiga gidan su.

Sallar la'asar tayi tare da yin wanka sannan ta dawo falo ta zauna. Yunwa take ji amma bata tunanin zata iya girki a gajiye take sosai. Baccin gajiya ne ya ɗauketa

sai kiran sallar magriba ne ya tashe ta. Miƙewa tayi tana salati ta yi alwala ta dawo ta tayar da sallah, bayan ta idar ne ta iya tashi ta dafa musu indomie ta zuba a plate kenan ta fito falon ya shigo da sallama.

Amsawa tayi sai ta bashi plate ɗin hannunta ta ce, "tun ɗazu na so nayi mana girki sai nayi baccin gajiya." Karɓa ya yi ya zauna ta koma ta ɗauko ragowar da ta ajjiye masa ta dawo ta zauna ta fara ci kamar yadda yake ci shima. Sai da ta kusa cinyewa sannan ta tura masa ragowar kuɗin da Abiy ya bayar ta ce, "Mahaifin Nayla ya bada dubu ɗari biyu ya ce mu zauna mai a mota, na bawa Salman Hajja dubu hamsin taƙi karɓa, amma na ce ta bawa driver da ya kaimu shima ya siyi kati. Ga ragowar nan, ga kuma kayan da Mamanta ta bani. Lace ne da atampa sababbi da turaren wuta, humra da mayafi" ta faɗa tana nuna masa kayan akan kujera.

Bai ce komai ba sai da ya kusa cinye indomie ɗin sannan ya ajjiye plate ɗin ya kalle ta ya ce, "Didi baki kyauta min ba, abinda kin ka yi min sam ban ji daɗi ba." Didi da mamaki ta ce, "me nayi maka?."

"Meyasa baki faɗa min in za a ce waje irin wannan ana siyan abu a kai ba? Sai gani nayi kawai kin bada tsaraba ba tare kin faɗa min ba. Shiyasa ake cewa ke ce kike ɗaukar ɗawainiya ta bana yi miki komai." Didi da mamaki ta ce, "Omar da girman ka da komai sai na faɗa maka? Baka san ya kamata ba dai?."

"Didi ban sani ba, ban sani ba. Bani da mahaifiyar da zata faɗa min abinda ya kamata da wanda bai kamata ba. Ban ji a raina ya kamata ace na siyi wani abu na kai ba saboda ban saba zuwa ba, ban taɓa yiwa wani godiya a duniya ba daga shi sai Hajja. Da nake zaune a gabansa ji nake kamar ana ɗaure ni, ban taɓa jin nauyi da girman mutum a idanuna kamar yadda na ji na shi ba. Na ji na kasa haɗa ido dashi balle na yi magana, a karo na farko a rayuwata da naji girma da nauyin wani mutum, duk na ɗauki hakan a rashin sabo saboda ban taɓa zuwa wajan wani da sunan godiya ba. Meyesa kafin mu tafi baki faɗa min ana siyan abu a kai ba?."

Didi kallon sa take yi har ya kai ƙarshe ganin da gaske yake maganar sannan ta ce, "shikenan naji laifina ne ban faɗa maka ba, nan gaba sai ka aikata ba tare da an faɗa maka ba. Kuma in na siya kamar ka siya ne ai." Omar ya ce, "ni dai ban ji daɗi ba, da kin faɗa min da ko wani abun an siya an haɗa an ka. Da kin faɗa min da ni zan bada kuɗin abinda zaki yi." Didi ta ce, "shikenan ai ya wuce."

Ajiyar zuciya ya yi ya ce, "Nawa ki ka kashe?."

"Gurasa ce fa ta dubu goma ba wani abun ba." Hannu ya saka a aljihu ya ɗauko dubu bakwai ya ajjiye mata ya ce, "ga kuɗin da ki ka kashe. Sannan ki haɗa da wannan ma ki riƙe hidima ce a gabanki" ya faɗa yana nuna mata wanda ta turo masa kusa dashi. Didi tayi murmushi ta ce, "to na gode."

Wayar Didi ce ta katse masa maganar da ta yi niyar yi, ta duba taga Nayla ce sai ta saka a speaker daga can ɓangaren Nayla ta ce, "Didi ina fatan kin sauka lafiya, Ina ta kiran ki ɗazu baki ɗauka ba." Didi ta ce, "mun sauka lafiya lau Nayla. Bacci nayi shiyasa baki same ni ba. Ya jikin naki?."

"Jiki da sauƙi Didi."

"Kin daina kukan?." Nayla ta ɗan murmushi ta ce, "Didi na daina" ta faɗa a sanyaye. Didi ta ce, "ai gwara da ki ka daina, gabaɗaya duk na damu wallahi:"

Yar dariya tayi ta ce, "An gode Didi, na ji daɗin zuwan ku sosai." Didi ta ce, "mu ne da godiya Nayla. Yadda aka karɓe mu a gidan ku wallahi ya fi min komai daɗi."

"Babu komai Didi. A gaishe da.....Yaya Omar" ta faɗa a rabe muryarta har rawa take yi. Didi tayi murmushi ta kalli Omar da yake suraren su ta ce, "Yaya Omar yana jinki." Nayla tayi murmushi ta ce, "na san bazai yi magana ba, amma ki ce ina yi masa bangajiya mun gode sosai."

Didi ta ce, "to Nayla, mun gode da tarba mai kyau Allah ya ƙarawa Abiy tsahon rai." Nayla ta amsa da amin tayi shiru ko Omar zai yi magana amma bai ce komai ba dole ta yanke wayar. Murmushi Didi tayi bayan ta kashe wayar ta ce, "Wai Yaya Omar, Nayla akwai ta da bin dariya. Ko yaushe ya zama Yaya ɗin oho mata."

"Ban cancanci ace min Yayan bane shiyasa har sunan ya baki dariya?." Da mamaki ta kalle shi dan bata ɗauka zai yi magana ba, sanin halin sa ba tankawa zai yi ba musamman Nayla da yake yawan faɗar haushinta yake ji.

Didi ta sake yin dariya ta ce, "A'a ni ban ce ba Malam Omar, meye nawa na cewa baka cancanta ba? Kawai na san haushinta ka ke ji ne." Bai yi magana ba ya share ta Didi ta ce, "anyi kiran sallar i'sha, sallah zan yi" ta faɗa tana tashi ta shiga ciki ya bita da kallo.

Yaya Omar ɗin da Nayla ta faɗa a lokacin da zasu bar gidan su da yadda hawaye yake zuba a idonta kawai ya tuna, ajiyar zuciya ya yi ya rufe ido sai kuma Narma ta faɗo zuciyarsa itama lokacin da take kuka lokacin da ta je wajansa. Tashi ya yi ya bar falon zuciyarsa cike da tunani kala-kala.

Bayan Kwana biyu.

Bikin Didi ya matso sosai an kai lefe gidan Kawu akwatina goma sha huɗu kaya masu yawa sosai. Baba Adamu kamar yadda ya ce an gama zuba komai na gidan Didi, hatta kayan kitchen ya zuba sai abinda Didi ta siya ta ajjiye aka kai can. Gida ne babba da falo biyu da bedroom uku, sai dai unguwar babu jama'a sosai amma gida kan ya yi kyau sosai.

Didi ana ta yi mata gyaran jiki duk da ita kaɗai take yi komai, sai Hajja da Salma da suke taimaka mata dan bata da wani dangi da yake taimakon ta tunda ba sabawa suka yi sosai ba. Har gwara Umma Sarood ƙanwar mahaifiyarta ta kawo mata turaren wuta irin nasu na mutanen Chad, har kayan gyaran jiki ta haɗo ta kawo mata. Mama Zainab Yayar mahaifiyarta ita kuma ta ɗauƙi nauyin zuba turaren wutar gidan, ta ce duk wani abu indai na ƙhamshi ne ita zata yi amma bata so Omar ya sani. Didi ta ji daɗi sosai har ta nuna musu, kuma suna yawan kiranta su ji shirin biki, zuwa ne dai basa yi saboda haɗuwa da Omar baya zama alkhairi. Duk wani shiri ita da Hajja ake yi sai Salma da ta kasance tana tare da Hajja ko yaushe.

Ɓangaren Omar ya watsar da duk wani abu da yake yi a baya, duk da daman ya jima da watsarwa amma yanzu yana ƙoƙarin ganin ko cikin yʻan uwansa yʻan daba na baya ya daina shiga. Ya tattara kayan sana'ar da yake so ya fara kawai yake yi, shida yaran sa su uku gabaɗaya sun bashi haɗin kai wajan yin sana'ar da suke fatan zata kai su inda basu yi tunani ba. Duk abinda ake saka shi a ciki a ɓangaren daba yanzu an daina, ko an zo masa da maganar zai ce babu ruwansa a kai maganar gaban hukuma. Duk da hakan dai ba a kawo masa wargi saboda lasar yaji baya hana gyaɗa yin garɗi, duk da haka akwai sauran tsoro da kwarjinin da yake dashi a wajan mutanen gari. Halayyarsa baby abinda ya canja, baya shiga harkar kowa kuma baya sauraren kowa, fuskarsa kullum a haɗe magana ma ba ya yi.

Lamarin Narma ya ajjiye a gefe, duk da yana tunawa musmaman yadda abubuwa suka faru a gidan su, kuma yana matuƙar tausayinta in yaga tarin messages da kiran da take yi masa baya ɗauka. Wani messages ɗin ya karanta kamar ya yi mata kuka haka yake ji dalilin da ya saka ya daina buɗewa gabaɗaya, dan in yana buɗewa zata iya karya masa zuciya wata ran ya saurareta, shi kuma in yayi gaba baya komawa baya, in tsallake baya sake tsallakawa.

••••••

Nayla kuwa duk yadda ta kai ga dauriya ɓoye abinda yake ranta ta kasa, gashi Abiy ya matsa mata da tambaya abinda yake damunta, da ya gaji ya haɗa ta da Jawad suka je asibiti, da ta faɗawa likita abinda yake damunta ya tabbatarwa da Jawad tana tare da damuwa a tambaye ta aji abinda yake damunta. Duk ta tsorata saboda kar Abiy ya tambaye ta dan gaskiya bazata iya cewa ga abinda yake damunta ba dan ta san ba abu bane mai yuwa.

Bayan sun dawo daga asibitin suna zaune wajan Abiy Jawad yana yi masa bayanin abinda likitan yace. Jawad ya ce, "Zancen gaskiya Abiy likita ya ce tana tare da damuwa sosai. Dalilin damuwar shi ne yake haifar mata da zazzaɓi da kuma ciwon ƙirjin da ta ce tana yi. Na tambayeta abinda yake damunta amma ta ce babu komai, na tambayeta ko akwai wani mai takura mata a wajan aiki ko barazana nan ma ta ce babu komai."

Abiy ya kalli Nayla da take zaune a gefen sa a tausashe ya ce, "Mamana me yake damunki?." Nayla ta sunkuyar da kai ta ce, "Abiy babu komai."

"Ƙarya ki ke yi, likita ai bazai miki ƙarya ba sannan yanayinki ya gwada kina tare da damuwa mai tarin yawa. Me ya ke damunki? Ki faɗa min ko meye zan miki maganinsa." Nayla ta yi ajiyar zuciya tayi shiru bata ce komai ba.

Abiy a tausashe ya ce, "ban kai na ji damuwarki bane?." Ta girgiza kai alamun A'a ya ce, "ni mahaifinki ne, Jawad yayan ki ne, Maman ku kuma babarki ce. Babu abinda zaki ɓoye mana na rayuwarki saboda mu ne ahlinki, ki faɗa min abinda yake damunki nayi miki alƙawarin zan yi miki maganin ko meye."

Nayla ta yi ajiyar zuciya bata ce komai ba. Ganin haka sai Mama ta ce, "Abiy ka bar ni da ita zamu yi magana." Abiy ya kalli Mama ta ɗaga masa kai ta ce, "zan yi magana da ita, zata faɗa min in sha Allah. Nayla tashi ki je ki shirya, ko ba zaki je Kano bikin Didi ba?."

Nayla a sanyaye ta ce, "Zan je Mama."

Mama ta ce, "to tashi ki je ki shirya." A sanyaye ta tashi ta fita. Mama ta kalli Abiy ta ce, "kar ka damu, ka bari ta je Kano ta dawo zan tambayeta a nutse na tabbatar zata faɗa min. Sai ta kasa faɗa maka damuwarta amma ni ta faɗa min, na san ta yadda zan bi da ita har naji abinda yake zuciyarta."

Abiy ya ce, "meyasa zaki ce ta ce ta tafi Kano bayan yanayin da take cikin na rashin lafiya?." Mama ta ce, "zuwa Kano zai ɗebe mata kewa sosai, ko babu komai zasu haɗu da Jidda da Salma." Ambatar Jidda da tayi sai wani abu ya shiga zuciyar Abiy amma bai nuna ba ya ce, "shikenan ai, Allah ya dawo da ita lafiya. Ki tambayeta har batun samarinta."

Mama ta ce, "in sha Allah." Bata sake cewa komai ba shima haka, amma a zuciyarta tana ji lokacin da take jira ne yake gab da zuwa, da wannan damar zata yi amfani wajan cika burinta a akan Nayla.

KRB2P013

ArewaBooks@nanahaleema11

Bayan sallar juma'a Nayla suka tafi Kano, kamar ko yaushe a gidan Hajja ta sauka a lokacin Didi ma tana gidan ana ta shirye-shirye ana walima gashi washe gari ne ɗaurin aure. Gabaɗaya bata da walwala bata sakewa ayi komai da ita, tana daga gefe tana tunani ko Omar ɗin bata son gani saboda kar ya taso mata da abinda take son binnewa a zuciyarta.

Washe gari da safe aka ɗaura auren Aisha da AbdulHamid, Didi ta sha kukan farin ciki, tayi kuka kamar babu gobe Hajja ce ke aikin rarrashi tana sake tuna mata sai yanzu lokacin auren ta ya yi. Omar ma tunda aka ɗaura auren yake ciki da matuƙar farin ciki, duk da yana daga gefe aka yi komai, Kawu ne ya bada aurenta bai hana hakan ba saboda burinsa a ɗaura auren kuma an ɗaura. Yana sanye da manyan

kaya riga da wando na farar shadda sai hula da ya saka, ya kame kansa a waje ɗaya ko magana ma ba yayi sai masu yi masa Allah ya sanya alkhairi.

A gidan Hajja ake taron yɗan uwan su Didi na ɓangaren uwa da uba duk sun zo,musamman su Umma Saroot da suka kasance iyaye a gareta duk suna nan aka ɗaura auren. Su Jidda dasu Salma har da iyayen su Salma ɗin ma duk sun zo saboda kowa ya san Didi.

Ana ta hidima, ko wanne dangi yana so ya nuna ƙauna ga Aisha da ƙaninta. Wannan ya ciko cooler da abinci, wannan ya bada kuɗi a siyo abinda ake buƙata duk burin su su wanke laifin da suka yi a baya. A ɓangaren Didi zata iya cewa ya wuce ta karɓe su hannu biyu matsayin iyaye, babu kamar dangin Maman su in tana kallon su sai ta ga kamar mahaifiyar su take kallo. Ɓangaren Omar ko kallon kirki ma basa samu, in ya gansu bazai nuna ya gansu bama balle ya yi magana. Su kuma tsoron dizgi da wulaƙancin da ya saba yi ne ya saka basa kula shi.

Bayan ɗaurin auren ne Didi ta nemi Nayla ta raka ta gidan su suka fito ita da Nayla da Salma zuwa cikin gidan. Tana shiga takar gidan taga babu kowa sai Omar da yake ya jingina da bango ya harɗe hannayen sa a ƙirji yayi shiru kamar mai cike da damuwa.

"Omar!." Didi ta furta murya na rawa, Omar sai ya kalle ta ya miƙe tsaye sosai ya yi murmushi ya ce, "to meye na kukan Didi?." Da sauri ta ƙarasa wajansa ta rungume shi har lokacin murmushi yake yi ya ɗora hannunsa a bayan ta kafin ya ɗagota daga jikinsa ya riƙe kafaɗarta ya ce, "meye na kuka kuma? Yau ranar farin ciki ce a gare mu gabaɗaya, me ya saka ki kuka?."

"Sai naga kamar baka murna" ta faɗa murya tana rawa. Ɗan ƙaramin tsaki yayi yana murmushi ya ce, "Kiɗa ki ke so kiga na saka? Ko tsalle-tsalle ki ke so ki ga ina yi sannan zaki tabbatar ina murna?." Ta yi dariya kaɗan ta ce, "kusan hakan." Ya kalle ta ya ce, "ban san meyasa ba amma har na fara kewarki, gabaɗaya bana jin daɗi."

Didi ta ce, "Omar nima ina jin hakan a zuciyata, ina ta tunanin wacece zata dinga kula min da kai?." Ɣar ƙaramar dariya ya yi ya kalle ta bayan ya ɗage gira sama ya

ce, "yaro ne ni da za a kula dani? Allah Didi kin raina ni" ya faɗa yana share mata hawaye da hannunsa.

Didi ta ce, "Omar rayuwarka kai kaɗai ce bana so, don Allah kawai ka yi aure." Idanu ya wara waje sosai sai kuma ya sake yin dariya mai sauti ya ce, "kawai dan kin yi aure sai nima nayi kamar yan wahalar matan su Kawu? Su ne duk abinda ɗaya ta yi sai sun yi." Zata sake magana ya ce, "Didi don Allah ki yi shiru, a bar maganar nan tukunna dai."

"Ka ci abinci yau kuwa?." Ya kalle ta cike da tsonaka ya ce, "waye zai bani abinci? Bani da kowa fa" ya faɗa cike da tsokana yana kallon ta. Sai zuciyar ta sake karyewa ido ya ciko da hawaye ya ce, "Wasa nake miki fa, na ci abinci tun ɗazu. Kar ki yi kuka, Allah bana so." Idanunta goge tana murmushi ta ce, "ni na san cin abincin ka kuma sai yadda hali ya yi tunda babu mai ce maka gashi, daman ya lafiyar kura balle ta yi zawo."

Murmushi ya sake yi ya ce, "Yaushe za a tafi kai ki? Bana son taron mata nan da kaina zan kai ki gidanki" ya faɗa bayan ya ɗaure fuska. Kallon sa tayi ganin ya ci magani alamun da gaske yake sai tayi dariya ta ce, "to babban yaya."

"Da gaske nake, na faɗawa mijin na ki bana son taron hayaniya. Baza a je gida ai ta kallo babu mai addu'a ba."

Murmushi tayi ta ce, "Ai daman kai kullum da gaske ka ke, wannan kalma kamar a bakin ka aka yi ta. Komai ka ce da gaske nake."

"To da ƙarya nake?."

"A'a, indai ka ce to da gasken ne." Share ta ya yi bai sake magana ba, tayi sosai tana mamakin ƙarfin hali irin nasa kafin ta juya ga Nayla da Salma da suke tsaye har lokacin.

Didi ta ce, "Nayla ku shiga ciki na bar ku a tsaye." Kai tsaye inda ta kalla ya kalla ya haɗa ido da Nayla da take murmushi tana hawaye. Salma ya kalla ya ga murmushin itama ta ke yi amma ita babu kuka. Ya ɗan taɓe baki kaɗan ya ce, "ita wannan kullum cikin kuka?" Ya tambayi Salma yana nuna mata Nayla da girarsa.

Ba Nayla da Salma kaɗai ba, har Didi sai da tayi mamakin abinda ya ce, kuma har lokacin idanunsa na wajen fuskarsa a ɗan sake. Nayla ta sunkuyar da kai tana murmushi cikin farin ciki, ko babu komai yana kula da yanayin ta, hakan ya yi mata daɗi sosai har bata san ta riɓe hannun Salma ba. Salma ganin fuskarsa a sake sai ta ce, "tana kewar Didi ne."

Bai amsa ba ya kalli Didi da ta ce, "Nayla tana kuka ne saboda taga Ina kuka, murmushin ma tana yi saboda Ina yi Omar. Bata da lafiya amma ta taho daga Kaduna tazo kawai saboda aurena, Ina ji da ita sosai kamar yadda nake ji da kai. Kai ƙanina ne ita kuma ƙanwata ce." Girgiza kai ya yi bai ce komai ba ya ɗauke kai yana taɓe baki, ya sake kallon gefen da take ya ga kanta a sunkuye amma murmushi take yi.

Didi ta ce, "Nayla mu shiga ciki." Tare suka shiga falon Nayla tana ji kamar kar ta shiga ta tsaya ta dinga kallon Omar tana samun sauƙin abinda yake damunta.

Shigar su babu jimawa suka fito harabar gidan da niyar komawa gidan Hajja. Turus suka yi ganin Narma da Najwa sun shigo gidan har lokacin Omar yana tsaye a inda suka bar shi. Narma ta kalle shi ta ce, "Faruk!." Ɗago idanu ya yi ya kalle ta sai ta zube a wajan tana kuka sosai. Ido ya kulle ya buɗe ba tare da ya kalle ta ba ta ce, "Omar me nayi maka ka ke hukunta ni da laifin da ba nawa ba? Faruk ni meye laifina da ko wayata baka ɗauka?. Na yi maka message sau babu adadi amma ka ƙi ka saurare ni Faruk, meye laifina a maganar nan?."

Bai motsa ba balle ya yi magana wani wajan daban yake kallo ta sake cewa, "Ina sonka, Ina ƙaunar ka, Ina so na rayu da kai. Shikenan kuma sai laifin iyayena ya shafe ni Faruk? Daman laifin wani yana shafar wani ne Faruk?. Ban ƙi ka ba, nace a haka Ina sonka, na ce zan bika mu dawo nan a ɗaura mana aure koda iyayena basa so amma ka ƙi ji. Ya kake so nayi da raina ne Faruk? Na mutu kawai?."

Ƙaramin numfashi ya yi ya ɗago idanunsa da suka fara komawa jajaye ya kalle ta. Zunbur ta miɓe ta ƙarasa kusa dashi tana kallon idanunsa tana kuka ta ce, "kalli yadda na koma, kalli kaga yadda soyayyar ka ta kayar dani, ka tambayi Najwa ko bacci bana iya yi, ko abincin kirki bana iya ci kullum cikin tunanin ka da son ganin ka. Iyayena basu san na baro London ba, kai tsaye daga can Kano nazo saboda kai Faruk, saboda kai kawai na taho tun daga London dan na ganka. Wallahi in na rasa ka zan iya mutuwa" ta ƙarasa faɗa a sanyaye tana sake zubewa a wajan tana kuka.

Najwa ce tazo ta ɗaga ta a inda take zube, ta riƙeta a jikinta tana kuka ta kalle shi ta ce, "Yaya Narma tana sonka, a da bana goyan bayan auren ka da ita, amma yanzu Ina goyan baya sosai. Don Allah ka taimaki Yayata ko iya waya da ita ne ka dinga yi kafin komai ya daidaita a wajan iyayen mu. Na tabbatar maka da zasu soka zasu amince da auren ku nan kusa, don Allah ka yi haƙuri ka manta da komai kar Yayata ta rasa tunaninta a dalilin ka" ta faɗa tana kallon sa tana hawaye.

Hasbunallahu wani'imal wakil shine abinda yake furtawa kawai a zuciyarsa, zuciyarsa bugawa take rauni ya mamaye masa jikinsa gabaɗaya. Tausayin Narma na tasiri sosai a jikinsa amma ya kasa ce mata komai. To me zai ce mata bayan shi ya riga ya ajjiye shafin ta a rayuwarsa?. Hannunsa Narma ta riƙe ta ce, "baza ka ce komai ba?." Zame hannunsa ya yi daga riƙon da tayi masa, domin in ta riƙe shi kamar haɗuwar wuta da ruwa haka yake ji a jikinsa. Kallon ta ya yi ido cikin ido kafin ya sauke numfashi ya ce, "Narma!." Luuu tayi ta faɗa jikin Najwa ta riƙeta sosai tana kallonsa.

"Ki manta da abinda ya faru, ki manta da abinda ya wuce ki bi umarnin iyayenki. Babu abinda zan iya yi miki a yanzu, na yi iya abinda zan iya yanzu komai ya ƙare!."

Narma ta bishi da kallo ta ce, "kenan kana nufin na manta da kai?." Ya ɗaga mata kai ta ce, "bazan iya ba, wallahi bazan iya ba. Ni kaina da ace na san inda zan ajjiye soyayyarka da na ajjiye na hutawa zuciyata. To ban sani ba Faruk, ban sani ba!"ta ƙarasa faɗa da ƙarfi tana kallon sa.

A kausashe ya ce, "ya kamata ki sani Narma, ya kamata ki sani!. Komai ya ƙare, komai ya wuce, bazan yaudare ki da kalaman da na san bazan cika su ba, bazan faɗa miki abinda na san bazan yi ba. Shiyasa nake faɗa miki gaskiya, kije ki bi umarnin iyayenki, sannan ki tafi!."

Narma murya na rawa ta ce, "na tafi kace fa?." Ya ɗaga kai ya ce, "eh ki tafi, babu abinda zan iya yi miki a yanzu, ki tafi kawai."

"Na tafi ka ce?" Ta sake maimaita tana kallon sa. A birkice ya ce, "eh ki tafi! Ki je ki yi abinda iyayenki suke so ki ƙyale ni!."

Kuka take yi sosai mai sauti na kusan minti biyu bata ce komai ba, ɗaga kai tayi bayan ta goge idanunta tace, "Farul ka san mutane ƙalilan ne suke samun kusanci da zuciyar mace? For examples iyayenta da yan uwanta, tunda tana tare dasu tana samun soyayya da ƙauna daga gare su tun tana yarinya. Kaima haka naji a kanka, na ji a raina kamar na tashi tare da kai tun ina ƙaramar yarinya Faruk, ji take soyayyarka ta shiga jinina kamar na jima da sanin ka. Tun daga wannan lokacin naji kawai so nake nayi rayuwata a tare da kai, ko kaso ni ko kar ka soni har abada bazan daina sonka ba Faruk, ko ka so ko kaƙi zuciyata saboda kai kaɗai take bugawa. Har yanzu ina sonka Faruk!."

Ta sake goge idanu ta ce, "zan tafi Faruk, amma ka sani zan dawo ko ban dawo ba duk abinda ya same ni ka sani soyayyar ka ce sila. Bazan taɓa daina sonka ba har a tashi duniya" ta faɗa tana fita daga gidan a guje.

KRB2P014

Arewabooks@nanahaleema11.

An kai amarya gidan ta mai kyau ana ta yabon kyaunsa saboda ko ina a gidan yayi kyau sai dai babu mutane sosai a kusa da ita amma kyau kam gida ya yi kyau. Jinkirin auren ta bai tashi a banza ba ya zame mata alkhairi domin kuwa da gidanta da lefen ta komai ma sha Allah.

Su Nayla gida suka dawo suna sauka a ƙofar gidan Hajja suka hangi Omar a zaune a ƙofar gidan Didi akan farar kujera ya ɗora ƙafa kan ɗaya yana kaɗawa. Nayla murmushi tayi ta ɗauke kai ta shiga gidan Hajja bata sake kallon sa ba.

Shi kuwa Omar kewa yake ji sosai a zuciyarsa, ya rasa abinda zai yi ya ji daɗi. Ya san Didi kuka zata yi in suka haɗu shiyasa ya gudu bai bari sun haɗa ba dan baya son ganin kukanta. Gidan yake son shiga amma in ya tuna bata nan sai yaji babu amfanin shigarsa gwara yayi ta zaman a ƙofar gidan in yana ganin mutane zai fi jin daɗi. Bai san ya damu da Didi ba sai yanzu, bai san haka Didi take da tasiri a gare shi ba sai yanzu, bai ɗauka zai yi kewarta har haka ba sai ya tabbatar da bata nan.

A kan idanunsa su Nayla suka shiga gidan Hajja ya sauke ajiyar zuciya ya cigaba da zama a wajan. Sai sha biyu na dare sannan ya iya miƙewa ya shiga gidan, kewarta ta damu zuciyarsa sosai, haka ya zubawa ido yana kallo kamar zai ganta ko ya ji muryarta, ga tausayin Narma zuciyarsa. Tabbas yana jin tausayin Narma amma

babu abinda zai mata in ba ya nisanta kansa da ita ba shiyasa ya aikata abinda ya aikata. Da wannan tunanin ya kwanta yana tunanin Didi bacci ya ɗauke shi.

Washe gari.

Nayla haka ta tashi da nauyin jiki tayi wanka ta shirya tsaf cikin doguwar riga ta atampa mai kyau. Falo ta fito wajan Hajja ta zauna a kan kujera ta ce, "Hajja Baba Salisu ya taho yazo zamu wuce gida." Hajja ta bita da kallon tuhuma ta ce, "Hauwa me ya ke damunki ne haka?." Hajja ta kalli Salma da ta fito tana shan tea ta ce, "Salma me yake damun yar uwarki?."

Salma ta zauna ta miƙawa Nayla cup ɗin tea Nayla ta karɓa ta ce, "na gode." Salma ta kalli Hajja ta ce, "Hajja bana ce ba, ni ma dai haka nake ganinta. Kawai ki ta yi mata addu'a." Hajja ta ce, "Me ya ke damunta? In ba zaku faɗa ba zan kira babanta na tambaye shi. Ya ina tambayar ku kuma ce min babu komai? Ina ganin duk wani motsin ku fa, yadda ku ke yin komai a sanyaye na tabbatar akwai abinda yake damunta." Nayla ta ce, "Hajja babu komai ba wani abun bane, shima Abiy ɗin haka yake cewa kuma na faɗa masa babu komai."

"Mu in baki faɗa mana ba ai Salma da Jidda sun sani." Salma ta ce, "Hajiya ni ban san komai ba gaskiya sai dai ko Jidda" ta faɗa tana miƙewa ta bar wajan. Hajja tayi musu banza bata sake magana ba amma tayi kuɗurin tambayar Abiy abinda yake damun Nayla.

Lokacin da Baba Salisu yazo sai da ta kai masa abinci kamar ko yaushe, ta dawo daga kai masa abincin idanunta ya sauka akan masoyinta yana tsaye suna magana dasu Bashir suna nuna masa wasu kaya a leda. Ɗauke ido tayi tana takawa a sanyaye ta shiga gidan Hajja ba tare da ta sake kallon sa ba dan gabaɗaya hankalinsa baya kanta. Bata jima da shiga ba ta gama haɗa abinda tazo dashi ta kai mota, Baba yana gama cin abincin ya huta tayi musu sallama Salma ta rakata har bakin mota ta shiga suka tafi.

••••••

Amarya Didi ta wayi gari a gidan miji cikin aminci da kwanciyar hankali, ganin abun take kamar a mafarki wai itace tayi aure bayan shekarun da ta kwashe ba tare da auren ba. Tana girmama ikon Allah da kuma lokaci da mutane suke faɗa sai yazo komai zai faru. Tabbas ta amince da aure lokaci ne, duk yadda ka kai ga son yinsa in lokacin yin bai yi ba baza ka yi ba. Kamar mutuwa ce, duk yadda ka kai ga yin jinya in lokacin mutuwar bai ba babu inda zaka je, amma da zarar lokaci yayi kamar ƙiftawar ido anyi an gama. Ita kam taga tasirin haƙuri, taga tasirin miƙawa Allah lamarinta, taga tasirin ƙin sanya damuwar rashin aure a zuciyarta. Gashi fa lokacin yayi har ta wayi gari a gidan mijinta kamar almara.

Tana zaune a falon ta gabaɗaya kewar Omar ta cika mata zuciya, AbdulHamid ya shigo falon da sallama ta amsa ya ce, "Omar ɗin kike tunani ko?." Didi tayi dariya ta ce, "wallahi, ina ta tunanin ko ya ci abinci." Ya yi dariya ya ce, "banda abin ki Omar ai ba yaro bane ba" ya faɗa yana zama kusa da ita.

Didi ta ce, "baka san halin Omaar bane, baya son cin abinci sai ance masa gashi, ko ance gashi ɗin sai yaga dama. Bara ba kira shi" ta faɗa tana ɗaukar wayata kira shi. Ɗauka taji anyi ta ce, "Assalamu alaikum." Daga can ɓangaren Omar ya ce, "Wa'alaiki Salam, Hajiya Didi amarya."

"Alhaji Omar ƙanin amarya." Dariya Omar ya yi ya ce, "ya naji maganar ki a dashe? me ya same ki?."

"Babu komai, mura ce kawai." Omar ya ce, "Kin sha ruwan sanyi kenan, shi bai san in kika sha ruwa mai sanyi kina tari ba ya bari ki ka sha?."

AbdulHamid da yake surarensa ya yi murmushi amma bai ce komai ba. Didi ma murmushin tayi ta ce, "jiya shine ka gudu ko?." Omar ya ce, "ni ai bana guduwa, kawai na ɓuya ne saboda ban son damuwa." Didi ta ce, "Haɗuwa dani ɗin ne damuwa?."

"Kukan da zaki yi min shine damuwa, a haka ma kin barni da tunani inaga kin saka ni gaba da kuka?." Didi tayi dariya ta ce, "To yaushe zaka zo?."

"Zan zo, Zan zo ko dan na yiwa mijin ki huɗuba ya san wacce yake aure, akwai gaɓar da zan tabbatar masa da Yayar Damisa yake aure." Didi da AbdulHamid suka yi dariya gabaɗaya AbdulHamid ya ce, "To Alhaji Omar ina nan jiran ka, Allah ya kawo ka."

Murmushi shima ya yi Didi ta ce, "ka ci abinci? Har sha biyu na rana tayi, Allah ya sa ka karya." Omar ya ce, "ban ci ba, ban jima da tashi ba. Yanzu dai nake tunanin abinda zan ci."

"Ka tashi ka yi girki mana, akwai abinci a kitchen da gas da komai ka dafa ka ci don Allah."

"To Didi zan ci."

"Ka kuma shiga gidan Hajja kayi mata godiyar abubuwan da suka faru."

"Didi nifa bana son godiyar nan kin sani."

"Ta zamar maka dole ne Omar, ta zama dole kaje kayi mata godiya." Ɗan tsaki ya yi ya ce, "to zan je."

Didi ta ce, "zan kira ka in anjima naji in kaje." Da to ya amsa a taƙaice ya kashe wayar ta kalli AbdulHamid tana murmushi. Shima murmushin yayi ya ce, "Kina ji da Oamar kamar yadda yake ji dake." Didi ta ce, "to mu kaɗai Allah ya bawaa iyayen mu, kuma iyayen na mu su ma babu."

"Gaskiya ne. Allah ya ƙara muku zumunci." Ta amsa da amin tana murmushi yana ta tsokanarta da sunan amarya ita kuma tana murmushi cikin jin nauyi.

Bayan Kwana biyu.

Abuja.

Najwa tausayin Narma take yi sosai, gashi ana ta batun ɗaura aurenta a ranar kuma bata sani ba. Duk tayi wani iri kamar ba ita ba kana kallon ta kasan tana tattare da damuwa mai yawa. Najwa ta fita wajan mahaifinsu ta zauna ta ce, "Dad don Allah kar a ɗaura auren nan, ku ƙyaleta taji da abinda yake damunta mana don Allah. In kuka aura mata Ashraf yanzu ba shi take so ba, ku ƙyaleta taji da damuwarta."

Mum ta kalle ta cikin harara ta ce, "kin fi mu sanin abinda ya kamata ne?." Najwa ta ce, "A'a Mum, Amma ina guje mana danasani a nan gaba." Dad jikinsa ya yi sanyi, maganar Najwa gaskiya ce amma bashi da zaɓi ko mafitar da ta wuce wannan, kuma dole ita zai bi dan samar mata da lafiya da kwanciyar hankali ta kuma manta da batun Omaar gabaɗaya a rayuwarta.

Dad ya ce, "Najwa ki bar zancen nan, aure za ayi shi yau in Allah ya kaimu. Sannan bance ki faɗa mata ba." Najwa ta tashi ta bar wajan cikin tausayin Narma sosai.

Narma tana zaune tana shan tea a falon sama tayi wanka ta saka ƙananun kaya riga da wando, wando iyakarsa guiwa sai riga mai baya a buɗe. Najwa wajanta ta dawo ta zauna bata ce mata komai ba itama bata ce ba tea kawai take sha a hankali.

Sun jima a haka kafin suji ana hayowa sama ba tare da ta kalli wajan ba ya dai jin motsin mutane. Muryar Dad ta ji yana cewa, "gata nan ma a zaune." Kallon wajan tayi sai ta ga gwamna Katsina ne da Ashraf da kuma minister sai Dad da Mum da Nabil. Bata yi ƙoƙarin miƙewa tsaye ba Dad ya karaso ya zauna kusa da ita mahaifin Ashraf shima ya zauna ya ce, "Daughter ya jikin na ki?."

Murmushi tayi ta ce, "Da sauki Daddy. Ina yini."

"Lafiya lau. Ina fatan babu abinda yake damun ki?."

"Babu komai Dady" ta faɗa tana ɗauke kai daga wajan.

Ya ce, "ma sha Allah, Allah ya ƙara lafiya." Ta amsa da amin tana ji suna maganar da ita ba ganewa take yi ba kafin duk su sauka ya rage daga Dad sai Mum sai ita a wajan. Dad ya kalle ta ya ce, "Narma yanayin damuwa da tashin hankalin da kike ciki, yau ciwo gobe lafiya shiyasa muka yanke hukunci a kanki." Da sauri ta kalli Dad ta ce, "ka yarda da Omaar?." Mum ta yi tsaki ta ce, "waye wani Omaar? Daughter ki nutsu mana, ki daina zancen wannan banza."

Shiru tayi bata ce komai ba. Dad ya ce, "Ashraf shine saurayinki wanda zaki aura a baya, kina sonsa shima kuma yana sonki. Wannan dalili ya saka yau ɗin nan mun ɗaura auren ku ke dashi, zaku tafi America ku je ku huta in kika nutsu sai a dawo ayi biki gabaɗaya." Kofin da take shan tea ne ya suɓuce daga hannunta ta kalli Dad murya na rawa ta ce, "au....re...Dad?."

"Yeah Aure, an ɗaura miki aure keda Ashraf yanzu. Kuma gobe in anjima zaku tafi america ku huta daga baya sai ku dawo."

Narma kallon mahaifin nata take yi ba tare da ta iya cewa komai ba, muryarta rawa take yi haka jikinta ma rawa yake yi cikin tsananin tashin hankali. An aura mata

wani ba Omaar ba? Kenan yanzu bata da hope ɗin aurensa ake so ace ko me?. Ganin yadda jiki ta yake rawa ya saka Mum ta riƙeta calmly ta ce, "Calm down my daughter! Kar ki damu Ashraf yana sonki kuma zai kula dake yadda ya kamata. Mun yi haka ne saboda ki dawo nutsuwarki bama so mu dinga ganin ki cikin damuwa."

Murya na rawa ta ce, "Mum in dai bakwa sona cikin damuwa meyasa baza ku aura min Faruk ba? Meyasa baza ku amince na aure shi ba?. Bana son Ashraf, Faruk nake so dashi nake so nayi rayuwar aure ba Ashraf ba, don Allah ku ce wasa ku ke yi min ba ku yi min aure dashi ba, please Dad you're just kidding me right?" ta faɗa tana haɗe tafukan hannayenta waje daya alamun roƙo.

Mum ta ce, "Zaki manta dashi a hankali, asirin da yayi miki zai bar jikinki saboda tasirin auren da aka yi miki. Kar ki damu ki nutsu."

Narma kuka take yi sosai zuciyarta nayi mata zafi, shikenan an rabata da Oamar ɗinta kenan? Shikenan yanzu bata da damar aurensa tunda gashi an aura mata wani ba shi ba. Tuna hakan ne yake sakawa ta ƙara ƙarfin kukanta cike da ƙunar zuciya. Rarrashinta suka dinga yi amma taƙi ta daina sai kawai Dad ya kira Ashraf ya ce ya hayo saman, yana shigowa saman ya samu tana wannan kukan duk sai jikinsa ya yi sanyi.

Dad ya kalle shi ya ce, "ka rarrasheta" abinda ya ce kenan suka bar musu wajan shi da Mum. Ashraf a hankali ya taka zuwa inda take ya ɗagota daga kan kujerar ya haɗata da jikinsa ya rungumeta tsamtsam yana shafa fatar bayanta a hankali kasancewar rigar bayanta a buɗe yake. A kunne yake raɗa mata yana cewa, "Shiii! relax my wife, i'm here for you, stop craying."

Kuka take yi sosai a jikinsa shi kuma ya matse ta ya hanata koda motsin kirki sai kukan da take yi. "Ki bar kuka my wife Ina tare dake a ko yaushe, bana so ki dinga zubar da hawayenki. Ina sonki zan zauna dake a ko wanne yanayi ki ke, don't be nervous about this early marriage. I'll take care of you, i promise i'll always be there for you and make you happy. I love you so much my love, I love you! I love you! you're my heart, you're my life, you're my world. Stop crying, please..." a kunne yake raɗa mata cikin salo mai ɗaukar hankali da son rarrashi yana sake hura mata iska a cikin kunnenta tare da sake matse ta a jikinsa.

Narma duk tana jinsa amma bata daina zubar hawaye ba, imagination take yi wannan kalaman da yake faɗa mata ace Faruk ɗin tane yake faɗa mata da bata san farin cikin da zata yi ba, hango kanta take a rungume a jikinsa ya matse ta yana faɗa mata wannan kalaman. Nan take tsigar jikinta tashi ta runtse ido zuciyarta na bala'in bugawa har shi Ashraf yana jin bugun zuciyar a jikinsa.

Ido a kulle tana daga jikinsa ta ce, "I love him, I love Faruk. Dashi nake so nayi rayuwa, shi nake so na aura. Bana son zama da kai, dashi nake so na zauna.....!" ta furta cikin wata irin murya mai nuni da raunin da yake tare da ita. Maimakon ya ji haushin kalamanta sai ya zaunar da ita akan kujera ya zauna a gefenta ya riƙe hannunta ya ce, "ina jin irin abinda ki ke ji, komai zai wuce na tabbatar da kina sona soyayyata zata dawo a cikin zuciyarki. Ina so kawai ki nutsu ki bani dama zan saka ki manta dashi a cikin rayuwarki gabaɗaya."

"Bazan taɓa mantawa dashi ba, shi nake so ba kai ba, shi nake so na aura ba kai ba, dan haka ka ƙyale ni" ta faɗa tana miƙewa da sauri ta shiga ɗaki tare da kulle ƙofa ta saka key. Bai yi ƙoƙarin binta ba sai ma murmushi da yake yi, tunda dai an aura masa ita koma me zata yi daga baya ne.

Narma tana shiga a kan gado ta zube tana sake fashewa da kuka mai tsuma zuciya, lokaci ɗaya kanta yayi nauyi sosai saboda ciwo idanunta suka tasa saboda kuka. Sai da tayi kukan mai isarta sannan ta tashi zaune tana sauke ajiyar zuciya. A sanyaye ta ɗauki waya ta nemo number Omar da tayi saving da my Faruk ta kira. Bata da tabbacin zai ɗauka ko bazai ɗauka ba, ta yi shiru tana jiran tsammani.

Kʼit taji ta katse alamun bai ɗauka ba ta ajjiye wayar a gefe tana kallon sunansa cikin bahagon yanayi. Kamar a mafarki sai ga kiransa na shigowa ta zabura ta ɗauki wayar hannu yana rawa ta kai kunnenta. Kafin ya yi magana ta ce, "Hello...hello...my Faruk kaine ka kira ni?.....Wayyo Allah! yau ya kira ni, Allah na gode maka. My Faruk Ina kewar ka Ina so na ganka..." abinda take faɗa kenan a ruɗe kana ji kasan bata cikin yanayi mai daɗi.

Omar da yake jinta bai ce komai ba ta sake cewa, "My Faruk su Dad suna son kashe ni, wai sun ɗaura min aure da wani ba kai ba, mutuwa kawai zan yi....!" Ta faɗa cikin kuka mai ban tausayi. Omar ya lumshe idanu jin abinda ta ce, maganar tayi masa daɗi kuma bata masa daɗi ba. Ɓangare ɗaya yaji daɗin aurenta kodan ta daina takura masa ta daina damun kanta a kansa ta san ita matar aure ce.

Ɓangare ɗaya kuma bai ji daɗi ba saboda tausayinta, ya san tana sonsa, aura mata wani a wannan yanayi bazai mata daɗi ba.

Narma ta ce, "ni da kai nake so na rayu, bazan iya rayuwa da kowa ba sai kai. Don Allah ka amince nazo na zauna da kai, ni kai kaɗai nake so nayi zaman aure dashi ba wani ba. In na zauna da Ashraf mutuwa zanyi! Bana sonsa, kai nake so da kai zan rayu.....!"

"Narma! Ki nutsu" ya furta a hankali cikin murya mai taushi. Numfashi taja kamar ya saka mata pause ta dakata da kukan sai ajiyar zuciya da take yi. Ya sake cewa, "Kin ce an ɗaura miki aure ko?." Kamar tana gabansa ta ɗaga kai ta ce, "eh, amma bana sonsa, ni kai...." Dakatar da ita ya yi ta hanyar cewa, "Matar aure ce ke, furta kina son wani ba mijinki ba babban laifi ne. Kina jina?."

"Ina ji" ta faɗa murya na rawa sosai.

"Waye ni a wajanki?."

"Wanda nake matuƙar so, wanda nake so na rayu dashi har a aljanna."

"Na isa nace ki yi abu ki yi? Na isa na ce ki bari ki bari?."

Narma ta ce, "har ka yi yawa ma Faruk! Har ka yi yawa wallahi. Zan iya sadaukar maka da raina da rayuwata." Ya ɗan yi jimm kafin ya ce, "to ki riƙe aurenki, ki yi abinda iyayenki suke so ki zauna da mijinki..." Katse shi ta yi ta ce, "Amma bana sonsa, bana ƙaunarsa ta ya zan iya zama dashi?."

Omar ya ce, "ki koya, ki koyi sonsa zaki iya. Ina faɗa miki gaskiya matsayina na Yayanki, in na ce miki Ina kallon ki matsayin wacce nazo gidan ku a matsayin mai sonki a yanzu ƙarya nake miki, gwara na faɗa miki gaskiya ki riƙe aurenki ki daina tunanina a cikin rayuwarki. Narma Allah bai rubuta ni da ke zamu zauna a inuwa ɗaya matsayin ma'aurata ba, ki karɓi ɗaddara hannu biyu Allah ne ya tsara ba ni ko ke ba. Iyayenki da kike gani kamar basu kyauta miki ba ba laifin su bane, babu ni a cikin rabon ki Narma, babu ni a cikin ƙaddararki saboda haka ki kwantar da hankalinki yi fuskanci rayuwa."

Narma hawaye take yi, ta san gaskiya yake faɗa mata amma zuciyar baza ta iya ɗaukar kalamansa ba, zuciyarta bugawa take yi sosai ta runtse ido tana jin

kalamansa kamar saukar ruwan zafi a zuciyarta, ta wani ɓangaren kamar saukar ruwan sanyi a zuciyarta.

"Wataƙila akwai Omar a ciki rayuwarki ta gaba, wataƙla babu. Ni dake babu wanda ya isa ya amsa kiran rabon da ba na shi ba. Dan haka ki nutsu, ki riƙe aurenki ki daina tunawa da kin san mai suna Omar a rayuwarki. Ina yi miki fatan alkhairi da fatan samun rayuwa mai albarka" ya sake faɗa cikin taushin murya wacce take ratsa zuciyar Narma.

Kai take girgizawa tana hawaye ta ce, "A'a Faruk, kar kace haka don Allah, bazan iya rayuwa babu kai ba, Ina sonka, ina son rayuwa dakai. Na san kaina kana jin abinda nake ji, ka amince min kawai nazo na rayu dakai ta ko wanne hali."

"Matar aure ce ke, Zancen na amince dake bai tashi ba. Kuma ni babu abinda nake ji a kanki kema ki daina ji a kaina, Ki manta dani ki kalli rayuwar aurenki zai fi miki kwanciyar hankali. Indai da gaske zan saka ki abu ki yi kamar yadda kika ce to ki riƙe aurenki, ki kuma manta dani!."

Jin tana kuka mai sauti ya saka Omar ya ce, "Ina yi miki fatan alkhairi, sai anjima" yana faɗa ya yanke wayar ta kifa kai akan wayar tana kuka sosai. Sai da ta gaji da kanta sannan ta dakata, kanta ya riƙe sosai saboda kuka ta koma sauke ajiyar zuciya. Bata san haka soyayya take ba, bata san haka ake ji a soyayya ba, bata san haka azaba da raɗaɗin soyayya yake ba da bata yi gangancin fara son Omar ba. Numfashi take saukewa a hankali a hankali cikin rashin sanin abinda zata yi.

KRB2P015

Arewabooks@nanahaleema11.

Tana ji ana buga ƙofar bata buɗe ba sai daga baya ta tashi ta buɗe, Najwa ta gani ta kalleta ta ce, "Ya ki shirya before magrib zaku wuce." Rungume Najwa tayi tana cewa, "Bana so Najwa! Bana son Ashraf, Ni Faruk nake so!. Ya zanyi? Ya ake so nayi da raina?." Najwa hawaye ya cika mata ido amma bata yi ba ta ce, "ki yi haƙuri." Ajiyar zuciya take yi a hankali kukan ma ya daina zuwa idanunta sai kanta da ya yi nauyi sosai.

Idanu a kulle ta ce, "Nayi magana da Faruk, ya ce wai na riƙe aurena na manta dashi. Hmmm ki ji fa Najwa, taya zan iya mantawa dashi? Shi ne wanda naso kuma

nake so har yanzu. Ya kasa gane irin yadda nake ji a kansa." Najwa ta ce, "Gaskiya ya faɗa miki Ya Narma, mantawa dashi ɗin shine yafi alkhairi a gare ki da kuma shi kansa. Yanzu kina da aure ya zama dole ki manta dashi, addu'a zaki dinga yi a hankali komai zai wuce." Bata ce komai ba ta bar jikin Najwa ta koma ta zauna a gefen ta dafe kanta.

Najwa da kanta ta jawo trolly bag ya fara haɗa mata kaya a ciki. Komai da ta san zata yi amfani dashi ta zuba tayi zipping bag ɗinta ta ajjiye ta fita. Bayan sallar la'asar Najwa ta sake dawowa ta tarar ta idar da sallah kalle ta ta ce, "Ya Narma ki tashi ki shirya." Kallon Najwa tayi kamar zata yi magana sai bata ce komai ba, kalaman Omar ne suke yi mata yawo a zuciyarta. Mum da Dad suka shigo ɗakin a tare, Dad ya kalle Narma a tausashe ya ce, "Daughter ki tashi ki shirya zaku wuce America." Kallon Dad tayi da idanu ta da suke a kumbure ta ce, "Dad ka san bana sonsa ka ce na bishi ko?."

Dad ya ce, "Narma mun gama wanna maganar dake, kar ki sake dawo da ita please. Ni na haife ki fa Narma, bazan taɓa yin abinda zai cutar da rayuwarki ba. Duk duniya babu wanda ya kai ni sonki, Ina sonki, Ina son inganta miki rayuwarki. Kar ki dinga kawo tunani mara kyau a zuciyarki na tabbatar da komai zai wuce nan da lokaci kaɗan." Narma tayi ajiyar zuciya ta ce, "Yanzu me zanyi?." Mum ta ce, "ki tashi ki shirya zaku wuce." Narma ta miƙe tsaye ta ce, "To zan yi, Tunda kun yi min auren dole zan tafi. Shima haka Faruk ɗina ya ce, ya ce kar na sake kiransa, na manta dashi wai ni matar aure ce" ta kalle su ta ce, "tambaya ta yake yi indai Ina sonsa nayi abinda ya ce. Tunda haka yake so kuma haka yake so zan yi" ta faɗa a sanyaye.

Tausayi ta bawa Najwa ta kawar da kai bata son yin kuka a gabanta. Duk sun ji me ta ce Mum ta kalli Dad ya ɗauke kai Narma ta shiga banɗaki.

Mum ta kalle shi ta ce, "bai daina bibiyar min yarinya ba kenan ko?." Najwa ta ce, "Ya Narma itace take bibiyarsa, ko a yanzun ma itace ta kira shi kuma tayi sa'a ya ɗauka dan baya ɗaukar wayarta. Gwara ma da ta kira shi ɗin ai, ba dan ya ce taje ɗin ba da baza ta tafi ba" Najwa ta faɗa tana fita daga ɗakin. Mum ta kalle Dad ta ce, "kaga tabbacin asiri ya yiwa Narma ko? Kana ɗaukar maganar nan wasa, Ina faɗa maka abinda ya kamata a yi kana mayar dashi wasa ko Dear?. Shikenan" ta faɗa tana ficewa daga ɗakin.

Narma duk tana jinsu tana daga bandaki a haka tayi wanka ta fito ta shirya cikin riga da wando. Rigar tana da tasho har guiwar ta dauki Jessy veil ta nada a kanta ta zauna a gefen bata ce komai ba. Najwa ce ta shigo ta kalle ta ta ce, "Ya Narma muje" ta fada tana daukar mata jakar. Har Najwa zata wuce sai taga charger din wayarta zare ta saka a jaka ta fito daga dakin ita kuma tana bayan ta.

Ashraf yana tsaye a falon kasa suka sakko ya riko hannunta bata kwace hannunta ba dan bata da karfi a jikinta. Mum ce ta budе mata hannu alamun taje jikinta, ta zara hannunta daga na Ashraf ta karasa ta shiga jikin Mum ita kuma tana murmushi ta ce, "Fatan samun kwanciyar hankali da nutsuwa my love." Dad ma kallon ta yake yi bayan ta dago daga jikin Mum ta karasa wajan Dad shima ya rungume ta ya ce, "Allah ya yi miki albarka my love, fatan samun lafiya."

Dagowa tayi ta kalli Yayan ta Nabil Shima ta shiga jikinsa ta rungume shi ya ce, "Allah ya dawo dake lafiya." Zare jikinta tayi ta koma kusa da Najwa ta tsaya. Dad ya ce, "Ashraf ga Narma nan please ka bita a sannu, kaga dai ba lafiya ce da ita ba sai ka yi hakuri na dan lokaci saboda yanayinta. Bani da wani tunani mara kyau a kanka, na san kana sonta zaka iya kula da ita a ko wanne yanayi. Please ka bata farin ciki, ka tabbatar da ta dawo nutsuwarta." Ashraf yana murmushi ya ce, "in sha Allah Dad kamar an yi an gama." Suka amsa gabadaya suka fito harabar gidan suka shiga mota Najwa ma ta shiga dan zata rakata airport suka tafi.

Motar su na wucewa Mum ta dawo gida ta sauke ajiyar zuciya ta ce, "Sai nake ji kamar na sauke wani abu mai nauyi, Daughter zata sumu kwanciyar hankali ko ya ya ne." Dad bai ce komai ba ya murmusa kawai amma a zuciyarsa ya san basu kyautawa Narma ba, irin wannan aure da suka yi mata ba tare da shiri ba, amma in ya tuna haka shine zai saka ta samu kwanciyar hankali ta manta da Omar sai ya ji dadi har hankalinsa ya kwanta.

•••••••••

Omar tunda ya yanke wayar wayar Narma ya jingina da kujera ya lumshe ido. Sautin kukan ta yake ji a kunnensa sai ya ji rauni ya mamaye zuciyarsa gabadaya. Da a ce ya san haka lamarin Narma zai zamar masa da tun farko bai bata fuskar da zata saki jiki dashi har su saba haka ba. Da ya san haka zata dinga shiga damuwa ta dalilinsa da bai tsaya ya saurareta ba, da bai bari yaji abinda yaji a kanta a lokacin baya ba. Tana bashi tausayi sosai, bai san abinda take ji a zuciyarta ba, amma ya

tabbatar ko meye yana da zafi da raɗaɗi mai yawa. Ya sauke ajiyar zuciya ya buɗe idanunsa a hankali yana kallon falon cikin kewar Didi.

"Assalamu alaikum, Boss na dawo" aka faɗa ana shigowa falon. Ya kalli Tk a kasalance ya ce, "ya ake ciki?."

"An samu shagon akan titi, kuma babba ne yana yana da girma zai yi yadda ka ke so."

"An karɓa?."

"E, an karɓa. Yanzu kai mu ke jira mu ji ya za a yi." Ajiyar zuciya ya yi ya kalle shi ya ce, "a gyara shi a saka abinda za a buƙata. Ku yi lissafi duk abinda kuke ganin ya dace ayi, kar dai ku yi min hauka a ɓarnatar min da kuɗi. Zan fito zuwa anjima sai mu ga yadda abin yake."

"An gama Damisa" ya faɗa cike da girmamawa ya fita. Bai bari tunanin Narma ya dawo zuciyarsa ba ya tashi ya shiga kitchen dan samun abinda zai ci.

Kallon kitchen ɗin yake yi kafin yaja tsaki a bayyane ya ce, "Rashin Didi babbar illa ce a gareni, daman ni maraya ne na rashin iyaye yanzu na sake maraicewa. Ko me zan ci ma oho" ya faɗa yana sake kallon kitchen ɗin. Tea kawai ya haɗa ya zuba madara mai shegen yawa tare da sugar, dan shi Allah ya yi masa son madara da sugar, in zai sha shayi to fa sai yayi kauri sugar kuwa sai yayi masa yadda yake so. Da tea ɗin ya fito ya zauna yana sha yana kallon falon yana tunanin Didi.

•••••••

Nayla tunda ta koma gida gabaɗaya ta sake zama shiru babu walwala balle ta sake a zauna a falo ana hira da ita. In ka tambaya ta ce babu abinda yake damunta amma da ka kalle ta ka san tana cikin damuwa. Jin daɗin ta ma in ta fita tun safe sai yamma take dawowa, wannan ya saka bata zama gida sosai ba kasafai ake game yanayin ta ba.

Haka Nayla ta cigaba da rayuwa cikin dauriya da juriyar abinda take ji a zuciyarta. Suna waya da Didi suna gaisawa kamar yadda suka saba bata taɓa ce mata ga abinda yake damuna ba itama bata tambayarta ba sai dai a yi hira kawai a kashe wayar.

Cikin kwanakin Abiy ya yi fama da rashin lafiya shiyasa maganar masu neman auren Nayla bata tashi ba saboda baya jin daɗi. Amma abun yana zuciyarsa so yake ya warware ya kira ta yaji ta bakin ta.

Yau ta kama ranar Asabar Nayla tana gida babu aiki tana kwance a ɗaki suna waya da Twiny cikin hirar su da bata wuce guda ɗaya. Mama ce ta shigo ɗakin da sallama Nayla ta amsa tana kashe wayar tare da tashi zauna. Mama ta ƙaraso ta zauna kusa da ita ta ce, "Keda Jidda ne?." Nayla ta ce, "itace Mama." Mama ta girgiza kai ta ce, "Nayla kin san tun kafin kije Kano bikin maƙociyar Hajja mahaifinki yake maganar ki fitar da miji a cikin samarinki ko?." Gaban Nayla ya faɗi ta ɗaga kai alamun eh Mama ta ce, "ni ce na ce a ƙyale ki saboda a lokacin bakya jin daɗi kuma bakya tare da nutsuwarki. Kwana biyu kuma kinga bashi da lafiya shiyasa bai tayar da maganar ba. Amma jiya da daddare ya ce yau ki faɗa min waye zaɓinki a cikin samarin nan guda huɗu."

Zuciyar Nayla bugawa take yi matuƙa ta kalli Mama da itama ita take kallo. Mama ta ce, "Ina jin ki, wa kike ɗauka ki ke ganin zaki iya rayuwar aure dashi?." Numfashi ta sauke tare da yin ajiyar zuciya a sanyaye ta ce, "Mama ni...." Sai maganar ma maƙale saboda bata san ne zata ce ba. Mama ta ce, "Ke me? Faɗi ina saurarenki."

"Mama ni ban san ne zan ce ba." Mama ta ce, "to haka zan faɗawa mahaifinki baki san ne zaki ce ba?." Nayla ta girgiza kai alamun A'a Mama ta ce, "to faɗa min, a wannan lokacin bazai ƙyale ba Nayla sai kin fitar da gwani dan burinsa a yanzu bai wuce auren ki ba. Ya ce ya gaji da ganin samari har huɗi a matsayin masu neman aurenki, wannan rashin lafiyar da yayi ko wannen su babu wanda bai zo ba kuma ya yi hidima. Har gwara shi Abbas daman ko babu soyayya ɗan uwanki ne amma sauran fa?."

Nayla tayi shiru cikin rashin sanin mafita. Ita bata san abinda zata ce ba dan dukkan su babu wanda take so babu kuma wanda take ji zata iya zama dashi a zuciyarta. Zuciyarta mutum ɗaya take so kuma bayan shi babu wanda zata iya bawa dama. Mama ta katse mata tunani ta ce, "ko na ce masa ya sake baki lokaci?." Da sauri ta ɗaga kai alamun eh ta ce, "E Mama, don Allah ki ce ya sake bani lokaci har yanzu babu wanda nake ji a cikin zuciyata. Dukkan su bana sonsu."

"Omar maƙocin Hajja kike so ko!?." Tambayar ta zo a bazata da sauri ta kalli Mama Gabanta na faɗauwa sosai, tsoro ya bayyana akan fuskarta ƙkarara dan bata san ya

aka yi Mama ta san labarin ba. Mama tayi murmushi ta ce, "kina mamaki ya aka yi na san waye a zuciyarki Nayla?. Hmm Nayla kenan, kar ki manta ni fa uwa ce a gare ki." Nayla ta sunkuyar da kai cikin bugun zuciya da tsoron bayyanar sirrin zuciyarta ga mutanen gidan su.

Mama a tausashe ta ce, "A da in kin dawo daga Kano labarin Yayarsa kike yi ba shi ba, in hirarsa tazo cikin labarin kina sako shi ne kina tsaki saboda tsoro da haushi yake baki. Amma daga baya sai hirar ta zama hirarsa kawai kike yi, kina bada labarin yanayin yadda yake kyau in yana murmushi. Daga lokacin da akace an kama shi hankali ki ya tashi kika yi ruɗewar da baki san kin yi ba. Muka je Kano bikin Shayida kika kusa yin accident a mota saboda kina so kizo ki samu mahifinki da maganar kina so a fito dashi. A yadda kike yiwa Abiy bayani kowa zai fahimci rauninki a kansa ne ba akan Yayarsa ba, kowa zai fahimci kina roƙon a fito dashi ne saboda shi kike so ba dan kina tausayin Yayarsa ba. Da Abiy ya amsa har ya kira Senator a lokacin farin cikin ki ya kasa ɓoyuwa akan fuskarki. Daga lokacin da akace ya dawo a ranar ke kuma ki ka dawo gida gabaɗaya rasa nutsuwar kiki yi Nayla, har wayata kin karɓa kin kira Salma saboda bata ɗaukar kiranki ke kuma kina so ki ji ko ya dawo."

Mama ta riƙe hannunta sosai ta ce, "tun daga lokacin na saka alamar tambaya akansa a zuciyarki. Abinda ya saka na tabbatar da zargina a kanki lokacin da suka zo gidan nan, kin ruɗe gabaɗaya, duk da ciwon da kike ji wanda ya hana ki zuwa aiki a ranar nan da nan kika neme shi kika rasa. A nan na tabbatar da Omar maƙocin Hajja shine wanda kike so."

Kawai sai ta fashe da kuka ta kifa kanta a hannun Mama tana kuka sosai. Mama ta dinga shafa bayanta a hankali tana murmshshin da ita kaɗai ta san ma'anarsa. A sanyaye ta ce, "Ki yi shiru mana Nayla, ba ga ni ba? zan tsaya a ɓangarenki wajan ganin kin samu abinda ke so. Ki nutsu mu yi magana bana son yawan kukan nan naki."

Ta ɗago fuskarta ta jiƙe da hawaye ta ce, "Mama in Abiy ya ji wannan maganar fushi zai yi dani, Bazai amince da zancen nan ba kawai gwara abar maganar Mama." Mama ta shafa fuskarta ta share mata hawaye ta ce, "Faɗa min gaskiya kina son Omar so na aure ko bakya sonsa?." Nayla ta kalli Mama sai ta sunkuyar da kai ta ce, "Mama faɗar bashi da amfani."

"Ni nace ki faɗa min, zan kuma tabbatar miki da amfaninsa yanzu ko nan gaba." Nayla ta ce, "Ina sonsa Mama, wallahi Ina sonsa son da ban san yawan sa ba. Kuma...kuma....ni ban san lokacin da na fara sonsa ba, haka kawai na wayi gari naji Ina jinsa a zuciyata. Ban san me zan yi ba Mama, na rasa mafita ki taimaka min" ta faɗa a raunane tana kallon Mama.

Mama ta girgiza kai ta ce, "to naji, nutsu mu yi magana." Nayla tayi ajiyar zuciya Mama ta ce, "kuma zaki iya aurensa a yanayin da yake ciki?." Nayla ta sauke jiyar zuciya t ce, "Mama bana kawo hakan a zuciyata gaskiya."

"Ina tambayarki, in kika samu dama zaki aure shi?."

"Mama ai bazan samu ba ma." Mama tayi murmushi ta ce, "ki amsa min tambayata mana, in kika samu dama zaki iya auren shi?." Nayla ta ɗaga kai alamun eh tana kulle idanunta.

Mama tayi ajiyar zuciya ta ce, "shikenan share hawayenki zan taya ki da addu'a, sannan zan san yadda zan yi Abiy ya amince da aurenki da Oamar." Da sauri ta kalli Mama cikin tsoro Mama ta ɗaga mata kai ta ce, "kar ki damu, zan tabbatar da kin samu abinda kike so kedai ki bani haɗin kai kar ki bani kunya. In mahaifinki ya ji maganar ya tambayeki kar ki ce masa a'a, ki faɗa masa abinda yake zuciyarki, mahaifinki yana sonki kuma na tabbatar da zai amince da abinda kike so. Sannan duk abinda nace kiyi, ta haka ne zaki samu cikar burinki."

Nayla kallon Mama kawai take yi amma a zuciyarta tana jin kamar hakan bazai yu ba. A sanyaye ta ce, "Mama hakan zai yu kuwa? Ni da zaki bar maganar kawai zan haƙura na ɗauki mutum ɗaya a cikin wanda Abiy ya ce na aure shi."

"Haka zaki zauna da wanda bakya so? Gangar jikinki fa kawai ya aura zuciyarki na tare da Omar. Baza ki iya yi masa biyyaya ba saboda ba shi kike so ba, ke kin san auren wanda baka so kuwa? Ko me mijinki zai miki bazai burge ki ba, tunanin Omar kawai zaki dinga yi kina ɗaukarwa kanki zunubi." Nayla ta ce, "To Mama ya zanyi? Abiy bazai amince ba."

Mama ta ce, "zai amince. Kin san mahaifinki ba kuɗi ne a gabansa ba, bai saka a zuciyarsa lallai sai kun auri masu kuɗi ba, tunda kina aikin ki kuma kina da shago wannan bazai dame shi ba. Kuma in ya so zai iya mayar da Omar yadda yake so,

yana da dukiyar da zata azurta Omar. To mahaifinki ba haka yake so ba, ba gidan kuɗi yake burin aurar daku ba, a riƙe masa yarinya kawai shi yake buri da ra'ayi."

Nayla ta girgiz kai ta ce, "ni dai Mama tsoro nake ji." Mama ta ce, "ki daina jin tsoro ina tare dake, Ke dai kiyi duk abinda na ce zaki mallaki Omaar in sha Allah." Nayla ta ce, "Mama ɗan daba ne fa, taya Abiy zai amince?."

"Da ya ke ɗan daba ai, ba naji kuna waya da Salma tana tabbatar miki har shago ya buɗe na sana'a ba?." Nayla ta ɗaga kai ta ce, "eh Mama."

"To kar ki damu, labarinsa na baya ya wuce labarin yanzu ake yi. Kedai ki kwantar da hankalinki, wannan kukan ne bana so na ga kina yi, bana so na ganki cikin tashin hankali. In mahaifiyarki na raye na tabbatar zata yi duk abinda zata yi wajan ganin farin cikin ki, to nima haka take a wajena. Kar ki damu zan san abinda zan yi dan ganin kin yi farin ciki."

Faɗawa jikin Mama tayi ta rungume ta yana hawaye, Mama tayi murmushi tana shafa bayanta tana murmushin da ita kaɗai ta san manufarsa, dan wannan dama ce da ta jima tana nema yanzu tazo mata cikin sauƙi. Ta ɗago ta daga jikinta ta shafa fuskarta ta ce, "ki kwantar da hankalinki, Ina tare dake a ko yaushe." Nayla tayi murmushi cikin farin cikin da take ji a zuciyarta ta ce, "Na gode Mama." Mama taja hancinta ta miƙe ta fita ta bar Nayla na murmushi ita kaɗai kamar zararriya.

Mama tana fita daga ɗakin tayi dariya ta ce, "Nayla kenan, na samu dama a hannuna ba tare da na sha wahala ba zan aikata duk abinda zan aikata. Zan tabbatar da na yi abinda nake so cikin sauƙi ba tare da tashin hankali ba. Mu je zuwa" ta faɗa tana murmushi ta bar ƙofar ɗakin zuwa ɓangaren Abiy.

KRB2P016

Da sallama Mama ta shiga ɓangaren Abiy yana zaune yana duba littafi a hannunsa, ya kalle ya amsa yana cigaba da duba littafin. Zama tayi ta ce, “A kawo kunun gyaɗar?.” Abiy ya ce, “A’a barshi sai anjima. Ya kuka yi da Nayla?.” Mama tayi ajiyar zuciya ta gyara zama ta ce, “yanzu muka gama magana da ita.” Abiy ya kalle ta ya ce, “to Ina jinki.” Mama ta ce, “Abiy ka ƙara mata lokaci saboda yanzu….” Ya katse Mama ya ce, “kamar ya na ƙara mata lokaci, wanne irin lokaci yake so na ƙara mata?. Auren ne bata so ko me?.”

Mama ta ce, “A’a ba haka bane…” Nan ma ya katse ta ya ce, “to yane? Faɗa min waye zaɓin taa cikin mutane huɗu?.” Mama ta kalle shi ta ce, “babu wanda take so a cikin su.” Abiy ya ajjiye littafin hannunsa ya kalli Mama da mamaki ya ce, “babu wanda take so a cikin fa ki ka ce? duka mutane huɗun babu wanda ya yi mata?.” Mama ta ɗaga kai ta ce, “babu, shiyasa nace maka tana buƙatar lokaci.”

“Wannan ma ai shirmen banza ne da wofi, dan tsabar rainin hankali samari har huɗu ta ce babu wanda take so a ciki dan ta raina ni ta mayar dani ƙaramin mutum?. Mtsw!” Yaja ƙarmain tsaki yana ɗaukar waya ya saka a kunne ya ce, “Nayla zo falon sama ki same ni.”

Nayla da ta samu kiran Abiy gabanta ya faɗi tsoro ya mamaye zuciyarta kar taje Mama ta faɗa masa halin da ake ciki. A sanyaye ta nufi ƙofar da zata kai ta falon sa na sama, ta shiga da sallama ya amsa yana kallon ta. Yanayin fuskarsa da take a ɗaure ya saka ƙirjinta cigaba da bugawa, ta taka a sanyaye ta shiga ta zauna a akan carpet ta ce, “Abiy gani.” Ya kalle ta ya ce, “Naji saƙonki akan samarin da suke naman aurenki, ki ka ce babu wanda kike so a cikin su?.”

Ta sunkuyar da kai bata ce komai ba. Abiy ya ce, “ke nake saurare.” Nayla ta yi gyara zama nan ma bata ce komai ba. Abiy ya ce, “magana nake miki, da gaske babu wanda kike so a cikin su?.”

Ta ɗaga kai alamun eh, yayi tsaki a ɗan fusace ya ce, “magana zaki yi min!.” Murya a sanyaye ta ce, “E Abiy.”

“To wa kike so?.” Gabanta ya faɗi ta sauke kanta ƙasa bata ce komai ba. Abiy ya sake cewa, “In ina tambayarki kina yi min shiru ranki ne zai ɓaci. In bakya sonsu wa ki ke so?.”

Nayla ta ce, “Babu kowa Abiy.” Abiy ya ce, “to ki tabbatar da kin samu wanda zaki so a cikin kwana biyu, na baki nan da jibi kizo ki faɗa min wa kika ɗauka a cikin su in ba haka ba zan aura miki duk wanda naga dama. Na gaji da wannan shirmen naki, gabaɗaya kin canja kin koma wata shiru-shiru, da kin dawo daga aiki kika shiga ɗakin bakya fitowa. An tambaye ki damuwarki kinƙi faɗa, likita ya ce kina da damuwa amma kin ƙi faɗar abinda yake damunki. Dan kinga na ƙyale ki shine kuma zaki kawo min iskanci? To baki isa ba, nan da jibi ki tabbatar da ko ma waye kin zaɓa an sanar dani in ba haka ba kuma ranki zai ɓaci wallahi. Na gaji da lallaɓaki,

yau ciwon kai, gobe zazzaɓi, jibi ciwon ƙirji. Dan kin raina mu kuma kin kalle mu kince baki da damuwa.”

Nayla jin Abiy yana faɗa abinda ba sosai yake yi ba sai tayi sanyi ta ce, “Kayi haƙuri Abiy.” Abiy ya ce, “Nayi yanzu, amma ki sani jibi bazan yi haƙurin ba.”

“To Abiy.”

“Tashi ki bani waje.” Ta miƙe a sanyaye ta fita cikin rashin sanin abinda zata yi.

Ya kalli Mama ya ce, “ke kike goya mata baya take abinda take so, ki faɗa mata wannan karan bazan ɗaga mata ƙafa ba wallahi, na gaji da wannan yazo tace bata so dole ta zaɓi ɗaya daga a cikin waɗanan huɗun in ba haka ba ni zan aurar da ita ga wanda nake so.” Mama ta ce, “in sha Allah hakan bazai faru ba, zan mata magana in sha Allah.”

“Ya fi muku” ya faɗa yana ɗaukar littafin da ya ajjiye yana cigaba da dubawa.

•••••••

Narma tunda lokacin da suka sauka a Texas cikin ƙasar America tana yadda take bata canja ba, ko yaushe tana cikin ɗaki a zaune tana aukin tunani ko magana ba ta haɗata da Ashraf. Shi kuwa yana sane ya ƙyaleta dan ta ɗan nutsu amma yaga abin nata ya yi yawa haƙurinsa ya fara ƙarewa, ko magana bata yi masa balle ya saka ran wani abun daban.

Kamar ko yaushe tana sanye da ƙaramar riga iyakar ta guiwa mai siririn hannu tana kallon taga, kasancewar lokacin snow ne ko Ina a garin ya lulluɓe da ƙanƙara sanyi yayi yawa sai da taimakon wood stove da take ɗumama ɗaki. Shigowa Ashraf yayi ya kalle ta tun daga gashin kanta da yake a buɗe har ƙafar ta da take sanye da room slippers.

Abinda ya saba ji a kanta yaji yana jansa zuwa gareta, a hankali yake takawa inda take har yazo daf da ita ya leƙe kansa ta kafaɗarta yana kallon window ɗin da take kallo. Hannunsa ya saka ya riko cikinta ya jawo ƙugunta ya haɗa shi da jikinsa yana kallon gefen fuskarta. “My love tunanin me kike yi?” Ya faɗa a kunnenta yana kallon

fuskarta. Bata motsa ba dan Omar ɗinta take tunani har lokacin zuciyarta ta gaza karɓar Ashraf a matsayin mijinta, Omar ɗin dai shi ne a zuciyarta.

Kiss yayi mata a wuyanta hakan ya saka ta kalle shi suka haɗa ido ya ce, “Haba my love kina wahalar dani, kin san Ina sonki fa, please daina wahalar dani.” Hannunta ta saka ta cire hannunsa gaga cikinta ta ce, “I need rest, please leave!” ta faɗa a sanyaye tana ƙoƙarin barin wajan. Riƙo hannunta yayi ya dawo da ita baya yazo daf da ita yana kallon idanunta ya ce, “i don’t want to leave your side, ina sonki sosai Narma. Allow me to show you how much you mean to me” ya faɗa tana riƙe wuyanta yana shafawa a hankali har gashin kanta.

“Kai ka ce zaka iya zama dani a ko wanne irin yanayin ko? To bani buƙatar your love or time and whatever, ka ƙyale ni a haka, haka nake son zama bana son takura” ta faɗa tana janye jikinta ta fita ta bar masa ɗakin. Girgiza kai yake yi cikin ɓacin rai ya ce, “No Narma baki isa ba, baki isa ki dinga saka ni a damuwa da yanayi mara daɗi ba. I feel your desire a strongly, and i want to satisfy, tun kafin na aure ki nake jin son kasancewa dake a zuciyata. Yanzu matata ce ke baki isa ki yi min iyaka da jikinki ba” ya faɗa shi kaɗai yana shiga toilet. Koma meye sai dai ya faru bazai sake barin ta haka yana kallon ta kamar wacce ya dasa yana jiran ta girma ba.

Narma falo ta koma ta ɗora ƙafa kan ɗaya tana kaɗawa cikin tunani. Yanzu in ta kira Omar sau dubu bata shiga ma balle ta same shi, ta gwada WhatsApp duk a banza. Gashi iya WhatsApp ta san yana yi bata sani ba ko yana da wani handle a social media platform. Ajiyar zuciya tayi ta ɗauki wayarta tana duba hoton da ta yi masa tana murmushi cikin soyayya.

Karɓar wayar taji an yi suka haɗa ido ta ga ya ɗaure fuska ta sauke kai ya ce, “Narma bazan juri wannan shirmen naki ba fa, da aurena a kanki ki dinga kallon hoton wani banza?.” Narma ta kalle shi ta ce, “kar ka sake ce masa banza, ai na faɗa maka daman bana sonka kace ka shirya aurena, to gani ga ka ai.”

A fusace ya yo kanta ya ce, “na rantse da Allah bazan juri wannan shirmen naki ba, na juri iya abinda zan iya yanzu bazan jure ba. Mijinki ne ni dole ki yi abinda nake so.” Narma kallon sa take yi kafin ta ce, “ni bani da wani miji in ba Faruk ba, don haka ka daina wahalar da kanka baza ka taɓa samu na a matsayin matar ka ba.” Ya ɗaga idanunsa ya kalle ta ya ce, “au haka ne? Zan tabbatar miki da ni ne mijin ki ba

shi ba, kuma zan nuna miki nike da iko dake bashi ba, kuma har abada bazaki aure shi ba.” Wuce shi ta yi zuwa ɗaki dan lokacin sallar azahar ya yi.

Sai da ta idar da sallah ta cire abayar da ta ɗora akan rigarta ajjiye ta zauna akan gadon tana tunani. Asharaf ya shigo ɗakin yana binta da shu’umin kallo, a yadda yake jinsa wannan lokacin ko cikin Mum zata koma bazai iya ƙyaleta ba. Ya gwada damarsa tana dakatar dashi, a wannan lokacin bazai dakatu ba sai ya tabbatar da abinda yake so ya samu.

A hankali yake takowa zuwa inda take, zai zauna sai kuwa tayi zumbur ta miƙe ya riƙo hannunta shima ya miƙe ya jawo ta baya. Juyowa tayi zata yi magana ya hana ta ta hanyar haɗe bakinsa da nata. Kiciniyar ƙwacewa take yi amma ta kasa ya riƙe ta sosai haka bai hana ta daina ƙoƙarin ƙwantar kanta ba amma ya hanata. Ganin ta dage ƙarfi zata gwada masa sai ya ya saka hannunsa a bayanta ya sake haɗe ta da jikinsa yadda bazata samu damar motsi ba.

Gently yake kissing ɗinta cikin ƙaramin lokaci ya kashe mata jiki, ƙoƙarin ƙwantar kanta da take yi sai ta daina jikinta ya yi sanyi tayi luf a jikinsa. Ganin ya fara samun kanta sai ya fara yawo da hannunsa a jikinta bayan ya sauke hannun rigar ƙasa. Ganin da gaske ya samu abinda yake so sai ya murmusa dan wutar sha’awarta sake kunnuwa tayi a zuciyarsa, da azama ya ɗauketa ya ajjiye a kan gadon yana kashe hasken ɗakin ta hanyar saka hannun a gefen gadon.

••••••

A cikin kwanakin da suka gabata Omar sun fara aikin sarrafa takalma na maza da na mata, takalma suke yi masu kyau suna kaiwa kasuwa. Cikin ikon Allah sun fara sana’ar da sunan Allah, domin kuwa batch ɗin farko na takalma guda ɗari suka yi amma sai da ya ƙare tas ya zamana ana nema suka sake yin guda ɗari biyu shima ya ƙare ana nema. Sosai hakan ya faranta ran Omaar yana kuma hango nasara wacce tafi haka a gaba.

Yana zaune a falon Didi na gidan su shida Bashir da Tk yana sake bada sabon design ɗin da suke gani ya kamata ayi. Bashir ya ce, “Boss ya kamata ace mun sakawa company nan namu suna, bamu san inda zai je ba nan gaba.” Omaar ya kalle shi ya ce, “Zamu yi wannan tunanin daga baya, yanzu dai a je ayi wannan.

Duk kun iya aikin ma kuwa?.” Bashir ya ce, “ni dai ina gwadawa, Tk dai ya iya sosai.”

“Yanzu meye a ƙasa?.”

“Anyi guda ɗari uku yanzu, an raba su a kasuwa.”

“Dakyau, zan shigo zuwa anjima duk abinda za a yi sai a yi.” Suka amsa suna tashi suna fita.

Gaisawa yaji suna yi da mace a cikin gidan sai abin ya bashi mamaki, dan tunda Didi ta bar gidan babu macen da ta sake shigowa, suma mazan sai su Bashir kawai bayan su babu wani baƙo da yake zuwa. Didi ce ta shigo falon hakan ya saka ya ce, “Nayi mamaki da naji ana gaisawa da mace a gidan nan, har nace wacce mai neman a raunanata ce ta shigo gidan nan.”

Didi tayi dariya ta ce, “Omar kana nan da halin ka, Ban da abin ka wacce mace ce zata shigo gidan maza?.”

“Mai rabon wahala mana” ya faɗa yana kallonta da murmushi a fuskarsa. Zama tayi ya bita da kallo yana hango canjin da ya gani a tare da ita ya ce, “Amarya da kanta, Kin yi haske amma kin rame kaɗan. Shi mijin naki baya baki abinci ne?.” Didi tayi dariya tana mamakin yadda akayi ya fahimci tayi haske ta kuma rame, lallai Omar yana kula da lamarinta sosai, in ba haka ba babu ta yadda za a yi ya fahimta lokaci ɗaya.

Ta ce, “Kai ba sai ka bani abincin ba.” Ya murmusa kaɗan ya ce, “Allah kin rame, Ina fatan lafiya?.”

“Lafiya lau wallahi, bani da damuwar komai Omar. Jinkirin aurena ya zamar alkhairi a rayuwata, haƙiƙa in ka yi haƙuri ka barwa Allah komai ka kuma riƙe mutuncin ka wallahi Allah bazai wulaƙanta ka ba. Na ga hakan a kaina Omar, Ina kukan farin ciki ina godewa Allah da ya jinkirta min zuwa wannan lokaci.” Omar ya ɗan taɓe baki ya ce, “Yayi. Amma baki amsa min tambayata ba, kin rame, babu damuwa ko?.”

Didi tayi dariya ta ce, “na amsa mana Omar, babu komai kawai na ɗanyi rashin lafiya ne daga shekara jiya zuwa yau.” Ya ɗaga kai bai ce komai ba ta bishi da kallo ta ce, “kaima ka rame ai, kuma ka ɗan yi duhu kaɗan. Lafiya ka ke?.” Sai ya langwaɓar da kai kamar ƙaramin yaro cikin shagwaɓa ya ce, “to bani da uwa, bani da Yaya, bani da mai kula dani, ba dole nayi duhu na rame ba?.” Sai taji babu daɗi a

zuciyarta ta ce, “Baka girki?.” Ya kalle ta ya ce, “Didi ba fa zaman banza nake yi yanzu ba, in na fita tun safe wani lokacin har dare Ina can ana aiki. Yaran basu gama iya aikin ba ni ne nake yi da kaina, har yaushe na dawo na ce zan yi girki?.”

Sai ya bawa Didi tausayi ta ce, “Ayya haka ne kuma. Ka yi haƙuri kaji ƙanina, yau nazo zan maka girki ka ci har sai ka barshi.”

“Gobe fa?” Ya tamabaya yana kallonta. Ajiyar zuciya tayi ta kalle shi ta ce, “To ka yi aure mana Omar, yanzu kana da sana’a kuma ka rage rashin ji zaka iya riƙe mata ai ko?.” Kallon ta yayi na wani lokaci kafin ya yanje ido ya ce, “ba yanzu ba.”

“Sai yaushe? Ko kana jiran Narma ne?.”

“Wace haka?” Ya tambaya yana kallon wani wajan daban.

Hararsa tayi ta ce. “Ban sani ba.” Sai ya yi shiru bai bata amsa ba. Didi ta sake cewa, “ya kamata ka fara neman aure zuwa yanzu, kaga watan ramadan zamu shiga zaka sha wahala, ga azumi, ga aiki, ga kuma girki. Mu ba yɗan uwa a kusa ba balle mu ce zaka dinga karɓa a wajansa.” Hararata yayi ya ce, “kawai sai na karɓi abinci a gidan wani ɗan uwa, haka akwai dan mutuwar zuciya?. Ba halina bane, ko a gidanki bazan karɓa ba balle wani.”

Didi ta yi murmushi kaɗan ta ce, “yanzu dai me zaka ci yau?.” Ya marairaice fuska yana lumshe idanu cikin jin daɗin ganinta ya ce, “kema kin sani ai Didi.”

“An gama.”

“Me kika fito yi ne?.”

“Ganin ka mana, tunda kai baka je inda nake ba ai ni nazo inda kake. Kullum cikin tunanin ka nake, sai da na fito nazo na samu nutsuwa.” Omar ya shafa kansa yana murmushi cike da ƙaunarta ya ce, “naso nazo kuma fa, zan zo dai ba yanzu ba.” Bata ce komai ba tayi murmushi kawai.

Kallon ta ya kuma yi fuskarsa a sake kamar zai yi magana sai ya fasa. Ta ɗaga kai ta ce, “Faɗi abinda yake bakin ka.”

Yayi yɗar dariya ya ce, “a dai yi shiru kawai, amma naji daɗin ganinki.” Murmushi ta kuma yi ta ce, “na shiga wajan Hajja ta ce min kwana biyu bata ganin ka, shine nace Omaar kai kuwa baka shiga ku gaisa?.”

Ya wara idanu ya ce, “Wai Hajjan nan wacece tawa? Uwata ce ko kakata?. Babu dangi uwa da uba ki dinga saka ni zuwa wajan ta?.” Didi ta ce, “babu ɗaya, amma ta wani ɓangaren tafi dangin uwa da uban, saboda tayi mana abinda si basu yi mana ba a lokacin da muke buƙatar taimako. Bani da wacce nake kallon matsayin uwa da Kaka sai ita, in kai baka kallonta a haka ni a haka nake kallonta.”

“Ke ki ka ga zaki iya” ya bata amsa ba tare da ya kalle ta ba.

Didi tayi dariya tana girgiza kai ta ce, “oh halin ka dai na zafin kai yana nan, Allah ya sauke maka shi ka huta.” Bai ce komai ba sai leda da ya ɗauko a gefen sa yana fito da takalma daga ciki. Didi ta ce, “kai ma sha Allah! Omaar wannan design ɗinku ne?.” Bai yi magana ba ta sake duba takalmin, daga can ƙarshen takalmin wajan dunduniya akwai wani ƙaramin sign da aka rubuta tiger cikin wani rubutu da yake a kwance sai ka kula zaka fahimta.

Didi tayi murmushi ta ce, “kai amma yayi kyau takalmin nan Omar, kamar ba hannu ne yayi shi ba.” Ya kalle ta ya ce, “na ki ne, gana mijinki. Ban san size ɗinsa ba ban sani ba ko zai masa” ya faɗa yana bata. Iri ɗaya ne takalmin banbancin design na maza da mata, amma iri ɗaya ne sak komai da komai. Didi ta ce, “kai amma mun gode. Kuma kaga zaku iya fara siyar da wannan couple design ɗin wallahi za a yi ciniki.”

“Ana yi sosai ma, sai dai ki cigaba da taya mu addu’a” ya faɗa tana kallon ta.

“In sha Allah Omar, addu’a kullum cikin yi maka ita nake. Yanzu ma tunanin sadakar azumi nake yi, ban san ya za a yi ba. Can unguwar mu babu wasu jama’a sosai sannan ban san kowa ba tukunna, nan kuma kai kaɗai ne da ace kayi aure ne sai matarka cigaba da yi, amma zan san abinda zan yi. Yadda Allah ya dafa mana ana cinikin nan dole mu dage da sadaka, Allah ya cigaba da riƙo da hannun mu ya gafartawa iyayen mu.”

Ya amsa da amin kana ya ce, “Ki dai faɗa min in za’ayi kar naji kin bayar da kuɗin da kanki, sadakata ce daman ai.” Tayi dariya ta ce, “tamu dai, ai tare muke yi ba kai kaɗai ba.”

Omar dai bai tanka mata ba ta sake juya takalmin da yayi kyau sosai ta ce, “Amma kuna ɗora a social media ko?.” Omar ya ce, “eh to bana ce ba, ana yi amma ba’a mayar da hankali sosai a kai ba, amma za’ayi.”

“Ya dai kamata wallahi, daman kai alhajin danne-danne in baka ɗora kana talla ba ai danna wayarka bai yi rana ba. Nima a turo min hotuna zan saka a status da kuma Instagram page ɗina. Customers dina na abinci in sun gani zasu siya sosai ma kuwa.”

“To. Bashir ne mai yin hotuna ya iya ɗaukar hoto sosai. Zan tura miki.”

“Wanne suna za a sakawa company?.”

“Ni wallahi ban sani ba, zaɓi.”

“Ga tiger na gani a rubuce, mai zai hana ba za a sakawa company suna Exclusive Footwear by Tiger ba, sannan sai ya zama logo ɗin takalman da hoton Tiger a jiki, amma a canja wannan na jiki.”

Kai ya ɗaga ya ce, “za a yi hakan.”

“Ai gwara, ta yadda duk inda aka ga takalman a san na mu ne. Tunda dai wannan suna na Tiger ya shiga jininka, gwara ma a saka shi yadda kowa zai san naka ne yanzu ka bar rayuwar baya.”

Kai ya ɗaga mata kafin ya ce, “za a yi, amma fa sabon kashe kuɗk ne ni duk na talauce” ya ƙarasa faɗa yana murmushi. Dariya tayi ta ce, “da rarrafe yaro yake fara tafiya, wata ran sai kuɗin sunzo ka rasa me ma zaka yi dasu. Allah ya taimaka ya bada nasara ƙanina.” Murmushi yayi ya ce, “Amin Didi. In sha Allah sai na saka ki farin cikin da baki taɓa yi ba a rayuwarki, zan cika miki dukkan burinki na duniya indai ina da rai.”

Daɗi ya mamaye zuciyar Didi ta ce, “Allah Amin. Ya rabbil alamin ka cikawa ƙanina burinsa, ka bashi ikon neman halak ta hanyar halak.” Murmushi ya sake yi ya amsa da amin bai ce komai ba amma a zuciyarsa yaji daɗin ganinta ya kuma ji daɗin addu’ar da take yi masa.

Kallon falon tayi ta ce, “ɗaɗi da kai baka da lalata waje, sannan kana da ƙoƙarin gyara. Babu laifi dai kawai zance, amma gidan da yar ƙura kaɗan, kalli fa tv can.”

Omar ya kalli inda ta nuna ya ce, “tunda ki ka bar gidan nan ban taɓa ta ba, kin san bana ƙura ko wajan ma bana kallo.”

Murmushi tayi daman ta san kallo bai dame shi ba, shi dai barshi da ya zauna kawai shi kaɗai hakan yafi masa komai daɗi. Tana ta yabon takalmin kafin tashi ta shiga kitchen tana ji a zuciyarta sana’ar nan da Omaar ya fara zata kai shi inda bai yi tunani ba.

KRB2P017

Didi tana kitchen tana ta yi amsa mita ya bar ƙwai sun lalace shi dai yana zaune dan shi bai ma duba ba balle ya san akwai wani ƙwai a kitchen ɗin. Gajiya yayi da ya bar wannan, ya lalata wancan da take ta faɗa ya fita. Wayarsa ce tayi ƙara a lokacin ya duba sai ya ga DPO da suka saba dashi ne. Ɗauka yayi suka gaisa yake sanar dashi in yana da dama da lokaci yana son ganinsa, ya amsa masa da zan zo in ya fito daga nan suka yi sallama ya kashe wayar.

Wajan Didi ya koma a lokacin ta fito daga kitchen ta ce, "Komai na kitchen ɗin nan ya la'ance Omar, gas ɗin duk ya yi baƙi saboda baka gyarawa." Ya kalle ta ya ce, "to aikina ne? Ina iya abinda zan iya na bar sauran."

"Yanzu dai ka bayar a siyo kayan miya nayi maka girki."

"To zan aiko dashi, zan fita yanzu amma ba zan jima ba dawo."

"Kar ka manta dai ka bayar a kawo." Da kai ya amsa mata ya fita ita kuma ta koma ciki.

Bashir ya kira a waya yazo ya ɗauke shi a machine suka tafi police station ɗin. Har offfice ɗin dpo suka shiga suka gaisa Omar ya zauna shima Bashir ya zauna yana kallon sa. Dpo ya ce, "Damisa daman na kira ne akan yaran da suka dame mu da faɗace-faɗacen nan na daba da ƙwacen waya da sace-sace. Mutanen gari suna cewa yan sanda basa yin komai wajan kama irin waɗanna mutanen, gwamtani ta matsa mana lamba akan mu kawo ire-iren waɗannan ɓata gari da ake nema. Wannan dalilin ya saka na kira ka dan ka taimaka min wajan kama su."

Omar ya ce, "amma kwanaki ka kira ni na tabbatar maka da duk abinda ya shafi wannan ɓangare na fita a ciki, aikin ku ne kama mai laifi ba ni ba, na yi iya abinda zan yi muku a baya amma yanzu babu ruwana a cikin wannan lamari."

"Na sani Damisa, taimako nake so ka yi min wajan bani list na waɗanan ɓata garin da ka sani dan a taimaki al'ummma." Omar ya kalle shi ya ce, "dole sai an haɗa kai da mutanen gari da masu unguwa sannan za a kawo ƙarshen wannan faɗan na cikin unguwa. Ko wacce unguwa a san su waye ɓarayin sun kuma san masu tayar da fitina, wani lokacin masu faɗace-faɗace daban masu sata da ƙwace waya daban, amma da yake su masu faɗan su ake gani da makami duk abinda ya faru kawai su ne. Kowa na unguwa ya san waye ɓarawon unguwa ya san mai faɗan daba, kowa ya san har cikin gidan su amma tsoro sai ya hana a faɗa. Misali kamar ni a baya, kowa ya san ina daga cikin ɓata garin da ku ke nema, amma in zaku kwana kuna tambaya a unguwar babu lallai a faɗa muku saboda ana jin tsoro. Kowa ya san ta inda ɓarna take ɓullowa a unguwanni shiru kawai ake yi, iyayen su kuma in aka zo ana faɗa sai suce su ƙarya ake yiwa yaran su kuma bayan sun san gaskiya. Wannan abinda kake so nayi maka aikin yan unguwar da ka ke nema ne, shugaban unguwar zaka je ka samu ya baka list na mutane da ake zargi a wannan ɓangaren."

Dpo ya ce, "Wannan gaskiya ne Damisa, kuma inda yan unguwa zasu yi ƙungiya suzo wajan hukuma su faɗi suna da inda waɗannan mutane suke wallahi da sun rage mana aiki. To kowa ya san ɗan iska amma sai a ƙi faɗa, in an faɗa an kama iyaye su shiga radio suna cewa an kama musu yara ba tare da laifin komai ba kuma sun san gaskiya. Yanzu ƙananun yara ake samu da wannan ɗabi'a, wani yaro da aka kama da laifin ƙwacen waya bai fi shekara sha biyar ba. Da aka kama shi mahaifiyarsa zage-zage ta dinga yi mana wai ƙarya ake yiwa ɗanta, da aka tambayi yaron ya amsa a gabanta ya aikata, akace meye dalili ya ce baya cin abinci ya ƙoshi shiyasa yake ƙwacewa ya siyar dan ya ci abinci. Tsakani da Allah wannan ba laifin iyaye bane?."

Omar ya ce, "shiyasa na faɗa maka mafita, kowa ya san na kirki ya san na banza. Manyan unguwa zaka samu a haɗa kai dasu a hukunta duk mai laifi."

"Kai na san ka sansu, shiyasa ana nemo ka dan ka taimaka min." Omar yaja numfashi ya kalle shi ya ce, "ni unguwar da nake babu wannan matsalar gaskiya, sai dai sauran unguwanin."

"Su nake so ka bani list na waɗanda ka san basa jin magana." Omar ya girgiza kai kafin ya kalle shi ya ce, "To ni yanzu bazan iya banbancewa ba saboda kaga na jima da fita harkar nan, kullum samun sabbabin fuska ake yi musamman yaran da ka

faɗa wanda suke fara ta'addaci saboda babu. Amma idan na tattara zan turo maka koda ta waya ne." Dpo ya ce, "na gode sosai Damisa. Samun irin ku masu taimakawa hukuma abin alfahari ne sosai." Ya kalli Bashir ya ce, "ma sha Allah! Kaima ka dawo kamar Ogan ka."

Bash ya ce, "duk inda Damisa yake a nan muke." Murmushi yayi ya ce, "Gaskiya ne. Gwara hakan, yanzu kowa ya ganku ya ga mutanen kirki. Duk da dai daman Damisar naku bai yi irin kamannin ku ba." Omar miƙewa yayi suka sake gaisawa da shi sannan ya fita suka wuce shago kai tsaye.

Ana ta aikin takalma shagon ma ya yi kaɗan sai da aka sake karɓar wani haya aka haɗa biyu saboda ɗaya ya matse. Ya jima a can sai bayan sallar la'asar sannan suka koma gida Bashir yana sauke shi ya tafi shi kuma ya shiga gida.

Kallon gidan ya tsaya yi domin an share shi tass babu ƙura ko kaɗan sai ƙhamshi yake yi, ya yi murmushi dan ya san aikin Didi ne ya shiga falon da sallama. A zaune ya same ta tana waya yana shigowa ta kashe wayar ta ce, "ina ka shiga tun safe?." Zama ya yi ya ce, "na je shago ne. Ni na ɗauka kin tafi."

"Ban tafi ba, sai zuwa magriba zai zo mu tafi." Bai amsa ba ta ce, "da sai na fita na bar gidan a buɗe?."

"Yau aka fara?" Ya faɗa yana kallonta.

"To kaje dai ka ci abinci."

"To Didi, an gode." Kallon sa dai take yi cikin tausayi dan gabaɗaya tausayi yake bata, rashin uwa babban masifa ce a duniya, inda ace mahaifiyarsu tana da rai da Omar bazai yi maraici dan tayi aure ba. Tashi yayi ya shiga kitchen ɗin sai ga shi ya dawo da abinci a bowl ya zauna yana ci sai aka kira shi a waya ya ɗauka yana amsawa duk magana akan sana'ar da ya fara ne kafin ya kashe.

Kallon sa ya ga tana yi ya ɗauke kai bai ce komai ba, ya kuma kallonta ya ga dai kallonsa take yi ya ce, "Didi ya dai?."

"Omar ka daure ka yi aure don Allah." Ya ɗan yi murmushi kaɗan ya ce, "Ikon Allah, wai meye damuwarki akan nayi aure ne?."

"Saboda ina so ka fita daga maraicin nan da ka ke ciki."

"Wa zan aura?."

"Ga mata nan da yawa sai wacce ka zaɓa. Ka duba yadda ka koma saboda rashin mai kula dakai." Ɗan taɓe baki ya yi ya ce, "to zan yi."

"Ko ka bani dama na zaɓa maka matar?." Kallon ta yayi sai ya ɗaga mata gira alamun eh ta ce, "da gaske fa nake."

"Nima haka" ya bata amsa yana cigaba da cin abinci dan so yake ya katse zancen auren nan da take yawan yi masa.

Kamar yadda ta ce sai bayan sallar magriba AbdulHamid yazo suka shiga har wajan Hajja suka gaisa sannan suka fito, Omar ta kira a gida suka gaisa yana ta tambayar yaushe zai kawo musu ziyara ya ce zai zo. Sallama suka yi suka tafi shi kuma ya koma gida zuciyarsa babu daɗi ko kadan.

••••••••

Ashraf duk yadda ya kai ga rarrashin Narma abin ya ci tura sai kuka take yi kamar ranta zai fita, hankalinsa ya tashi sosai dan bai ɗauka zata yi kuka har haka ba. Ya ɗagota jikinsa yaji jikinta akwai zafi alamun zazzaɓi ya ce, "Haba my love! ki daina wannan kukan mana, jikinki yayi zafi sosai." Narma ta ture hannunsa daga jikinta ta ce, "ka ƙyale ni."

"Ta ya zan ƙyale ki bayan baki da lafiya? Ki tashi na kai ki asibiti kinji." Tsaki tayi ta juya ta kwanta tana share hawaywe. Babban baƙin cikinta da Ashraf ya same ta a banza a wofi, ta so tayi tattalin jikinta har ta kai wa Omar masoyinta amma gashi a banza a wofi ya same ta komai ya lalace.

Shi kuwa Ashraf baya ya koma yana kallonta, sai da ta gaji da kukan dan kanta sannan tayi bacci ya tsaya yana kallonta. Murmushi ya yi yana shafa fuskarsa, tarin sha'awarta da yake ji gabaɗaya ta kau sai shauƙi da ya ke mamaye masa zuciya. Leɓensa yake lashewa a hankali in ya tuna irin abinda ya tarar a jikinta sai yaji tsigar jikinsa na tashi har yana mararin sake kai kansa gare ta.

Ta jima tana bacci har akayi sallar i'sha sannan ta farka, tunawa da abinda ya faru da ita sai baƙin ciki ya mamaye zuciyarta, tsanar Ashraf ta yi mata dirrar mikiya a zuciyarta. Daƙyar ta iya tashi ta kai kanta bandaki ta jima a ciki sannan ta fito. Doguwar riga kawai ta saka ba tare da ta saka komai ba ta saka hijjabi ta tayar da sallah. Jiri taji yana ɗaukarta a tsaye sai da ta zauna ta iya ƙarasa sallar.

Tana idarwa kiran Mum ya shigo wayarta ɗauka murya a dashe ta ce, "Mum!." Daga can ɓangaren Mum ta ce, "Subahanallah! Daughter me ya same ki? Kar ki ce min kuka kika yi?." Narma ta ce, "Mum bana son zama a nan ni gida zan dawo, bana son zama da Ashraf baya sona ko kaɗan."

"Me ya faru?."

"Mum raping ɗina yayi" ta faɗa murya na rawa alamun kukan zata sake yi. Mum da mamaki ta ce, "raping! Ashraf ɗin ne yayi raping ɗinki?."

Narma ta ce, "Eh Mum." Mum ta ce, "Narma! he's your husband fa, dan hakan ya faru baza ki kira shi da raping ba."

"Amma Mum ai ya faru ne without my consent, ya san bani da lafiya bana cikin nutsuwata amma bai iya ƙyale ni ba sai da yayi raping ɗina. Ya bari na amince mana, ya bari na samu lafiya mana. Ni na gaji bazan iya zaman nan ba Nigeria zan dawo."

Mum ta tausasa murya ta ce, "i'm sorry, yanzu me kike ji?." Narma a shagwaɓe ta ce, "my whole body is in pain, I can't event sit properly. Mum I don't think I can stay here anymore" ta faɗa a sanyaye cikin sangarta da shagwaɓa. Mum ta ce, "ki daina kuka, kin sha magani?."

"Uhum uhum."

"Ina Ashraf ɗin?."

"I don't know."

"Okay, let me call him to take you out to hospital" Tana faɗar haka ta yanke kiran.

Ba jimawa Ashraf ya shigo ya ƙaraso ya ɗuka a gabanta ya ce, "i'm sorry my love, I'm sorry. Tun ɗazu nace mu je asibiti kika ƙi, yanzu ga Mum ta kira ni tace na kai ki asibiti. Please saboda Mum ki tashi mu je kin ji?." A tausahe yake maganar amma jin maganarsa take yi kamar ta aljanu saboda haushinsa da take ji.

"Please my love!" Ya sake faɗa yana kallonta tare da ɗagota ta miƙe tsaye. Zare hijjabin jikinta ya yi ya ajjiye ya kalle ta ya ce, "na saka miki kayan?." Idanunta a kulle yake ya kalli kayan jikinta yaga ana hango komai na jikinta. Wajan kayanta yaje ya duba ya ɗauko doguwar riga wacce tafi ta jikin ta kauri sai dai itama roba ce. Bai damu ba ya ƙaraso ya bata ya ce ta saka.

Zame ta jikinta tayi ta fara saka wacce ya bata yana tsaye yana kallonta, lumshe ido yayi yana sake ƙarewa surarta kallo da take a bayyane babu abinda ya rufeta. Ashe duk abinda yake gani a cikin kaya yana ɗaukar hankalinsa ba komai bane, yanzu ne yake ganin asalilin sura da abinda ya aura, dan shi kam surarta ya aura dan ba ƙaramar sha'awarta yake yi ba. Babu abu mai ɗaukar hankali a jikinta kamar ƙugunta, hips ɗinta a cike yake sosai ga wrist ɗin nata ɗan ƙarami kuma siriri hakan ya bawa shape ɗinta damar fita sosai, in ta juya baya boobs ɗinta ma abin kallo ne.

Daƙyar ya iya kawar da kai ta saka kayan amma taƙi motsawa ƙarshe sai dauƙota ya yi suka fito harabar gidan. Da yake akwai mota a apartment ɗin da suke yana fita ya ajjiyeta ya buɗe garage ya ɗauko mota sannan ya sake fitowa ya ɗauketa ya sakata ciki suka tafi. Koda suka je can ma duba ta aka yi aka bata magani aka saka mata drip dan jikinta ya saki. Bacci ta sake yi shi kuma yana tsaye yana kallon ta cikin tsantsar shauƙi da son sake kasancewa da ita a karo na biyu.

••••••••

Da daddare hankalin Nayla sam baya jikinta kasancewar washe gari shine ranar da Abiy ya bata zata faɗa masa waye zaɓinta. Bata cikin kwanciyar hankali dan bata san abinda zata ce masa ba. Tana zaune a falo tana kallon tv amma ba fahimta take yi ba tunanin ta na ga abinda zata cewa Abiy ya amince da ita. Dan ita dai ta san bata son waɗannan mutane, in tace ta ɗauki ɗaya wanda zata iya zaman aure dashi ta cuci kanta ne, kuma kamar yadda Mama ta faɗa zata dinga kwasarwa kanta zunubi ne kawai.

Mama ce ta shigo ɗakin har ta zauna kusa da ita bata sani ba sai da ta taɓata sannan ta kalleta ta ce, "Nayla tunanin me kike yi haka?." Nayla ta sauke numfashi tace, "Mama tunanin gobe nake yi, ban san me zan cewa Abiy akan maganar nan ba."

Mama ta ce, "har yanzu bakya jin zaki iya zama da mutum ɗaya a cikin su?." Nayla ta ɗaga kai ta ce, "bana ji Mama, wallahi bana ji gabaɗaya." Mama tayi ajiyar zuciya ta ce, "Kawai zan faɗa masa akwai wanda ki ke so." Nayla ta wara idanu waje tana kallon Mama da firgici ta ce, "don Allah Mama kar ki faɗa masa, in kika faɗa masa ya nemi sanin waye shi fa?."

"Sai mu faɗa masa waye, in ya kuma kira ki ya tambaye ki ki tabbatar masa da kina sona kuma aurensa kike so ki yi."

Nayla ta fara girgiza kai cikin tsoro ta ce, "bazan iya ba Mama, bazan iya ba wallahi." Mama ta dafata ta ce, "ni zan iya yi miki faɗan Nayla, abinda nake so in ya kira ki ya tambaye ki ki tabbatar masa dake shi kike so kuma shi ki ke son aura. Zaki iya ko baza ki iya ba?."

Nayla ta kalli Mama cikin rauni ta ce, "Mama bazan iya ba, bazan iya kallon Abiy na tabbatar masa Ina son Omar ba, bazan iya ba gaskiya." Mama ta ce, "zaki iya, zuciyarki zaki saurara da zarar ya kiraki, kar ki bar harshen ki ya sarrafa kalaman zuciyarki, kai tsaye ki bari su fito daga cikinta ki faɗa masa gaskiya, in ba haka ba in ya gano da kansa ransa ne zai ɓaci sosai."

Nayla ta ce, "Mama gwara ya gano da kansa da ace nice na tabbatar masa." Mama ta dafata cikin rarrashi ta ce, "Nayla bazan taɓa bari naga kina son abu ina da damar baki shi ban baki shi ba, sannan bazan taɓa bari naga kina shan wahala akan abinda bai fi ƙarfin ki ba kuma na zuba miki idanu. Zan iya yin ko meye wajan ganin na samar miki da farin ciki koda ni zai zama silar baƙin cikina. Dan haka ki bani haɗin kai Nayla, na tabbatar miki zanyi abinda mahaifinki zai baki abinda kike so ba tare da tashin hankali ba ko wani abun."

Nayla ta kalli Mama cikin gamsuwa da kalamanta ta ce, "Na sani Mama, amma bakya ganin Abiy zai yi fushi dani?."

"Babu fushin da zai yi dake, ki bar komai a hannuna ina tabbatar miki da babu abinda zai faru sai alkhairi." Nayla ta sauke numfashi ta ce, "To Mama" ta faɗa a sanyaye tana wasa da hannunta. Mama tayi murmushi ta ce, matar Omar." Kunya ta bata sai ta rufe fuska da hannunta kafin ta buɗe ta ce, "Mama shi fa bai san Ina sonsa ba, taya zan aure shi?." Mama ta yi murmushi cikin shigar kwantar da hankali

ta ce, "ke dai ki jira mu gama da Abiy zamu koma kansa." Kai ta ɗaga kawai bata ce komai ba Mama ta fita ta barta a zaune tana tunani.

Washe gari a ɗarare ta shirya ta tafi aiki, ko a can ma haka take yin komai babu kuzari har lokacin dawowar ta gida yayi ƙarfe biyar na yamma. Tana ajjiye motarta taga motar Abiy sai da gabanta ya faɗi tayi saurin wucewa ciki ta shige ɗakin ta harda kulle ƙofar da makulli.

Bayan sallar i'sha kamar yadda Abiy ya saba yana zaune shida Mama bayan ya gama dinner ya kalli Mama ya ce, "ya kuka yi da Nayla? yau ne kwana biyun da na bata." Mama ta fuskance shi sosai ta ce, "maganar gaskiya Nayla bata son samarin nan guda huɗu." Abiy ya kalleta cikin mamaki ya ce, "kamar ya bata sonsu? Duka mutane huɗun babu wanda take ji zata iya aure?. Wannan ai shirmen ne da rainin hankali, na bata iya lokacin da zan bata kuma tazo min da wannan iskancin?." Mama ta ce, "hmm wani daban zuciyarta take so ba su ba."

Abiy da mamaki ya ce, "wani daban kuma take so? Waye shi?." Tayi ajiyar zuciya ta ce, "Wani ne daban a Kano, babban abin haushi da tashin hankalin ma data buɗe baki ta faɗa min waye yafi komai ɗaga min hankali. Kuma wai bai ma san tana sonsa ba, duk wannan rashin lafiyar da take fama da ita cikin kwanakin nan duk saboda shi ne, wannan ramar da tayi da rashin nutsuwa duk akansa ne. In da ace mutumin kirki ne na gari dan tayi haka a kansa ba laifi bane, amma ni har kunyar faɗa maka waye nake yi wallahi" Mama ta faɗa cikin zallar nuna takaicinta.

Abiy da yake so Mama ta kai ƙarshen maganar a ƙagauce ya ce, "wa take so? Waye shi ki faɗa min bana son zagaye-zagaye." Mama ta ɗan yi shiru kafin ta ce, "wannan ɗan daban yaron nan da ka yiwa hanya aka fito dashi har suka zo gidan nan godiya. Shi Nayla take mutuwar so, ta tabbatar min da in baka amince ta aure shi ba zata iya barin gidan nan, ta ce min zata iya barin kowa na gidan nan taje ta tare dashi kaɗai. Wannan kalma ta tayar min da hankali, nayi rarrashin na nuna mata hakan kuskure ne amma Nayla sam ta kasa amincewa."

Mutuwar zaune Abiy yayi jin kalaman Mama ya zuba mata ido ya kasa cewa komai, Daƙyar ya iya tattaro kalaman bakinsa ya ce, "Omar ɗan daban Kano take so? Wai maganar nan gaskiya ce ko wasa kike yi min?."

"Wallahi da gaske nake, ita da kanta ta faɗa min. Da farko na ɗauka wasa ne amma Jidda ta tabbatar min da gaske shi take mutuwar so. Abin haushin ma ko ta ita baya yi, in da na kirki ne ma da sauƙi to na banza ne. Wallahi ji nake kamar na yi kuka."

Abiy ya rasa ma abinda zai ce kawai sai ya miƙe ya shiga zuwa cikin gidan ya hau sama har ɗakin Nayla ya same ta a zaune tana ganinsa ta firgita ta miƙe tsaye. Kallonta yake yi kamar yadda take kallon sa dan in ba rashin lafiya ba babu abinda yake kawo Abiy ɗakinta sai dai in bata da lafiya.

Abiy kallon ta yayi ya ce, "Nayla da gaske ne abinda Maman ki ta faɗa min? Da gaske kina son Omar na Kano?." Gabanta ya yanke ya faɗi ta ɗago ido ta kalli Mama da take gefen ta tayi mata alama da ta amsa ta sake saukar da ido ƙasa tare da zube guiwarta duka biyun a gaban Abiy.

Abiy ya ce, "tambayar ki nake da gaske kina sonsa? Da gaske akan sa kike wannan rashin lafiyar?." Nayla ta sake sunkuyar da kai hawaye na zuba a idonta. Mama ta ce, "Abiy ka yi mata a hankali" ta ƙaraso kusa da Naylar ta ce, "Nayla ki faɗa masa abinda yake ranki. Da gaske kina son Omar?." Nayla zuciyarta bugawa take yi sossai, zuwan Mama kusa da sai ya ƙara mata ƙarfim guiwar da ta amsawa Abiy tana so ɗin.

Dafata Mama tayi hakan ya saka tayi ajiyar zuciya ta sake saukar da ido ƙasa ta ce, "Da.....gas....ke....ne.....Abiy....."ta faɗa a rarraebe cikin tashin hankali da tsoro. Abiy ya ce, "da gaske ne me? Da gaske shi kike so?." Ta ɗaga kai alamun eh. Abiy ya ce, "'magana zaki yi min!." Tsawar da ya yi mata sai da ta tsorata, a firgice ta ce, "Eh Abiy, da gaske shi nake so..." ta ƙarasa faɗa cikin muryar tsoro da tashin hankali.

KRB2P018

“Hauwa!” Abiy ya faɗa cikin tsawa yana kallonta cikin ɓacin ran jin kalamanta masu kama da rashin hankali ko wacce bata cikin hankalinta. Dumm ƙirjin Nayla ya buga, ta wara idanu waje cikin tsantsar tashin hankali da firgici. Tunda take da Abiy bata taɓa ji ya kira asalin sunanta ba, koda wasa bai taɓa kiranta da Hauwa ba sai dai ya ce Mamana ko kuma Nayla, amma yau gashi ya kira sunanta da murya mai amo mai nuni da tsantsar ɓacin ran da yake ciki.

Kasa ɗago kai tayi dan yanayin muryar mahaifin nata da taji bata taɓa jinta a kausahe haka ba, hakan ya saka ta kasa ɗago kai ta amsa kiran da ya yi mata. Abiy ya ce, “kina cikin hankalinki kuwa?.” Nayla ta sake sunkuyar da kai kamar ruwa ya cinyeta ko motsin kirki bata so ta yi.

“Wannan yaron ki ke kallona kina cewa shi kike so Nayla? Me ya shiga kaaki ne?. Wannan dalilin ne ya saka kika tayar da hankalin ki a karɓo shi daga hannun Senator?.” Yadda yake magana cikin murya mai amo ya saka Nayla yin danasanin furta abinda ta ce dan gabaɗayata rasa nutuswarta. Abiy baya taɓa yi musu tsawa tunda suka tashi, yadda yake yi mata a yanzu ya sakata take ganin abun baƙo shiyasa ya tsoratata sosai.

Mama ce ta kalle shi ta ce, “ka yi mana a hankali Abiy.” A fusace ya ce, “bazan yi mata a hankalin ba, yarinya ce ko kuma bata da hankali? Bata san abinda ya dace da wanda bai dace ba ko me?. Duk mazan duniyar nan, duk mazan da suke Kano da wajan Kano ta rasa wanda zata fara so sai riƙaƙken ɗan daba wanda aka yi masa shaida mara kyau?. Meye abin so a tare dashi!.” Mama ta kalli Nayla da ta kasa motsi ma balle tayi magana, ta kalli Abi zata yi magana ya dakatar da ita ya kalli Nayla ya ce, “Hauwa!.”

Nayla murya na rawa ta ce, “Na’am Abiy.”

“Tunda ta nan ki ka ɓullo zan yiwa tufkar hanci, zan sake baki dama ki fitar da mijin aure a karo na uku, in kika sake aikata irin abinda kika aikata yanzu bazan sake baki dama ba har abada. Sannan ki cire batun wannan yaron daga zuciyarki, ba mijin aure bane, in ma bakya cikin hankalinki to ina mai baki shawara da ki dawo cikin nutsuwarki ki san waye a gaban ki!” Ya ƙarasa faɗar maganar da tsawa yana nuna ta da yatsa.

“In da ace ya dace ya kuma cancanci ya zama mijinki zan iya amince miki, amma yanzu ki adana kalamanki bana son sake jin magana irin wannan daga cikin gidan nan, ki ɗauka baki san shi ba, ki kuma manta dashi a cikin zuciyarki. Kin ji abinda na ce ko?.” Nayla ta ɗaga kai kafin ta ce, “Naji abiy, zan yi in sha Allah.”

“Yafi miki” yana gama faɗar hakan ya fita daga ɗakin ya barta a ita da Mama.

Mama ce ta riƙeta ta miƙar da ita tsaye ta ce, “ki kwantar da hankalinki komai zai zama daidai nayi miki alqawarin hakan, kar ki damu da kalaman mahaifinki zan san

yadda zan yi ya sakko ya fahimce ki.” Nayla ta ce, “Mama kawai ki ƙyale shi, ni daman sai da nace tsoro nake ji kar a faɗa masa kika ce a faɗa masa, kinga ransa ya ɓaci yanzu ni kuma bana son hakan. Don Allah ki ƙyale shi kawai Mama ni na haƙura, zan ɗauki mutum ɗaya a cikin waɗancan kawai na huta.” Mam ta ce, “kar ki cuci kan ki, kar ki cutar da zuciyarki saboda faɗan mahaifinki na yanzu. Zai sakko na yi miki wannan alqawarin, zai amince da auren ki da Omaar kar ki damu.”

Nayla dai hawaye take gogewa tana ji zafi a zuciyarta da ta fara son wanda soyayyar sa bata da wani amfani a gareta da cikin rayuwarta baki daya.

Mama fita tayi zuwa wajan Abiy ta same shi a zaune da alama har lokacin ransa a ɓace yake sosai ta zauna ta ce, “Lamarin Nayla ya fara bani tsoro wallahi, da gaske sonsa take yi fa. Ka ji irin kalaman fitar hankali da take faɗa bayan fitar ka? Ita sai ta aure shi, shine farin cikinta, kalamai dai barkatai. Allah ya kawo mana mafita a wannan lamari kawai.”

Sake tunzura zuciyar Abiy Mama tayi ya yi ƙwafa ya ce, “Ashe da gaskiyar Senator Sagir da ya ce na bincika anya nima bai yiwa Nayla asiri ba, a lokacin sai nake ganin ba haka bane ashe da gaske dai asirin yake yi, tunda ga Nayla ma tana neman fita daga hankalinta saboda shi.”

Mama ta ce, “ni wallahi gani nake ba wani asiri da yake yi, kawai zuciyarsu ce bata yi musu adalci da take fara son wanda bai kamata ma ace ta so ba. Ɗan shaye-shaye, ɗan daba, karen ƴan siyasa, wanda ya yi zaman prison, abubuwa da yawa marasa daɗi akan mutum meye abin so a wajan?. Allah yasa kar ya shirya ya ɗauko ƙafa yazo yace yana son Nayla.”

Abiy ya yi shiru kawai amma gabaɗaya zuciyarsa bata yi masa daɗi, sam bai ji daɗin kalaman Nayla akan tana son Omaar ba. Meye abin so a Omar don Allah? Me yake dashi da har Nayla ƴar cikin sa zata ji tana so duk wannan tarin abubuwa marasa kyaun da suke dabaibaiye shi?. Tsaki Abiy yayi ya sauke numfashi ya kulle ido amma bai ce komai ba. Mama ta ce, “Ashe daman yawan zuwa Kanon da take yi duk saboda shi ne, wallahi ƙunar abinda nan nake ji har zuciyata. Inda mutum ne na gari ma da sauƙi, amma irin wannan ɗan iskan garin meye amfanin son sa?.”

Abiy nan ma bai ce komai ba amma kalaman Mama tuna masa wasu abubuwan suke yi musamman yawan san zuwa Kano da Nayla take dashi, bai taɓa kawo haka a zuciyarsa ba amma yanzu ya kawo hakan ya kuma tabbatar da saboda shi take zuwa Kano a kai a kai tunda maƙocin Hajja. Girgiza kai ya yi kawai ya tashi ya barwa Mama wajan gabaɗaya jikinsa ya yi sanyi.

Mama ta yi murmushi ta ce, “Ai indai Ina nan sai Nayla ta auri yaron nan, a gaban idonka Ina tare da kai, amma a bayan idonka ni ce zan dinga zuga Nayla akan Omar. Haba ai dole ma ta aure shi hakan shine zai saka ni farin ciki da kwnaciyar hankali a zuciyata. Ko babu komai na san zata je inda bazata taɓa farin ciki ba a rayuwarta, tunda baya sonta itace take sonsa kuma ga yanayin halayyarsa komai zai iya faruwa” ta faɗa tana murmushi cikin farin cikin cikar burita.

Nayla haka ta kwana ciwon kai saboda damuwa da kukan da tayi, da safe kasancewar Sunday ce babu aiki ta jima tana bacci sai sha biyu na rana sannan ta fito babban falo ta tarar da Jalil yana game a tv. A sanyaye ta ce, “Auta Abiy yana nan?.” Kai ya ɗaga mata ya cigaba da game ta nufi ɓangarensa.

Mama ta gani ta fito daga apartment ɗin Nayla ta kalleta ta ce, “Mama Ina kwana.” Da kallo ta bita kana ta ce, “Lafiya lau Nayla. Lafiya naga fuskarki ta kumbura? Kar ki ce min kwana ki ka yi kina kuka?.” Nayla ta sunkuyar da kai kafin ta ce, “Mama Abiy yana nan?.” Mama ta ce, “ya kwanta sai dai zuwa anjima. Zo mu je” ta faɗa tana jan hannun Nayla zuwa ɗakin ta.

Mama ta kalleta ta ce, “Nayla faɗa min kuka ki ka kwana kina yi?.” Nayla a sanyaye ta ce, “na dai yi kuka amma ba kwana nayi Ina kuka ba Mama.” Mama ta ce, “mahaifin naki ai ya fara sakkowa, shiyasa nake faɗa miki indai ina nan zan san abinda zan yi ya amince da auren ki da Omaar. Tunda yaron yanzu kince ya daina abinda yake yi ya kama sana’a hannu biyu, to meye aibu? Ai ba a tuna da abinda ya wuce abinda yake faruwa yanzu ake kallo. Yanzu kafin ya kwanta maganar mu ke yi yana tambayata da gaske kina sonsa, na ce kina sonsa mana shine ya ce yana so ya sake tabbatarwa daga bakinki, in kina sonsa sosai zai iya amincewa ki aure shi tunda kina so. Amma in bakya sonsa zai bari ki samu wanda ki ke so.”

Nayla ta kalli da sauri Mama ta ce, “Da gaske mama?.”

“Da gaske mana Nayla. Ke kin san Abiy yana matuƙar son farin cikinki, zai iya sadaukar da nasa farin cikin saboda naki farin cikin kawai. Dan haka ki daina damun kanki a hankali zai amince kawai ki bashi lokaci. Sannan in ya sake tambayarki akan Omar ki tabbatar masa da Omar shine rayuwarki, rasa Omar daidai yake da rasa ranki. Na tabbatar yana jin haka zai amince miki ɗari bisa ɗari.”

Nayla ta ce, “Amma Mama sai nake ganin kamar bazai amince ba. Ni na haƙura wallahi, daman shi ma bai san Ina sonsa ba, bai san ina yi ba gwara na auri wanda suke sona da na auri wanda nake so shi ba sona yake yi ba. Ni kawai ki daina masa maganar,in ya tambaye ni zan faɗa masa sunan ɗaya daga cikin waɗanda ya ce na zaɓi mutum daya a cikin su.”

“Kar ki aikata haka, in kika aikata haka daidai yake da kin saka ƙafa kin yi fatali da farin cikin ki ne. Na faɗa miki Abiy yana son farin cikinki, zai iya yin komai saboda farin cikin ki meyesa ki ke haka? Ko baki yarda dani ba ne?.”

Nayla kamar zata yi kuka ta ce, “Mama in ban yarda dake ba da wa zan yarda?.” Mama ta ce, “to ki kwantar da hankalinki na faɗa miki zanyi duk abinda uwa take yi dan samarwa da ɗanta farin ciki a kan ki, haihuwar ki ce kawai banyi ba, amma ni na raine ki har kika kawo yanzu. Kedai ki bani haɗin kai ko me nace miki ki yi shikenan komai zai wuce. Mahaifinki zai daina fushi dake, kema zaki samu abinda kike so ba shikenan ba?.”

Nayla ta ɗaga kai ta ce, “To Mama, na yarda dake zan kuma yi duk abinda ki ka ce. Na gode Mamana, ina sonki.” Mama ta shafa fuskarta ta ce, “ai ba ke kika ɗorawa kanki soyayyar ba, Allah ne ya ɗora miki kuma shine zai yaye miki. Tunda har Allah ya saka miki soyayyarsa a zuciyarki wataƙila alkhairi ne ga rayuwarki, kar ki ji komai ki ɗauka kamar an yi an gama ne.”

Nayla ta rungume Mama itama ta rungume tana shafa bayanta ciki sigar rarrashi. Nayala gabaɗaya jinta yake wani iri, wani ɓangare na zuciyarta ya amince da maganar Mama wani kuma zuciyarta tana rawa a kai. Ta san Mama bazata cutar da ita ba amma ta rasa dalilin da ya saka zuciyarta take rawa akan kalaman Maman ta.

Nayla bata haɗu da Abiy ba sai yamma, ta same shi a falo a zaune dashi da yaye ta da ƙanenta. Abin mamakin bai nuna mata komai ba sun gaisa kamar ko yaushe, sai taji kalaman Mama sun samu gurbi sosai a zuciyarta, kamar yadda ta ce Abiy ya

sakko kenan ya sakko ɗin tunda gashi sun gaisa hankali kwance bai yi mata faɗa ba bai kuma ɗaure fuska ba. Duk da dai walwalarta ta ragu sosai amma hakan yayi mata daɗi yana lura da yadda yake ta murmsmushi amma bai ce mata komai ba.

Abiy bai sake yi mata maganar ba sai ranar talata da daddare tana zaune a falo ita da Mama da Abiy tana cin abinci kasnacewar su Auta sun kwanta saboda akwai makaranta washe gari. Abiy ya kalle ta yana lura da ita cikin kwanakin gabaɗaya komai a sanyaye take yi, sannan bata da lafiya kawai dauriya take yi saboda shi.

“Nayla!.” Abiy ya kira ta yana kallon ta. Gaban ta ya faɗi ta ɗago ta kalle shi ta ce, “Na’am Abiy.”

Ya kalle ta sosai ya ce, “Ya maganar da mu kayi akan wanda zaki aura ɗin?.” Ta kalli Mama da take kallonta ta sake kallon Abiy ta ce, “Abiy duk abinda kace.”

“A’a abinda kika ce dai, faɗa min waye zaɓin ki?.” Nayla tayi ajiyar zuciya tayi shiru bata yi magana ba. Abiy ya bita da kallo kafin ya ɗauke kai ya ce, “ke nake jira.” Ta yi shiru ta kasa furta komai gabɗaya kwarjinin Abiy ya dabaibaiyeta.

Mama ta ce, “Nayla kar ki ji tsoro mahaifinki ne, ki faɗa masa abinda yake zuciyarki.” Nayla ta kalli Mama ta sake kallon Abiy ta sunkuyar da kai tana ajiyar zuciya. A kasalance ta ce, “Abiy…” Sai ta kasa ƙarasawa ta sunkuyar da kai. Abiy ya sauke numfashi ya ce, “faɗi ina jinki.” Mama ta kalle shi ta ce, “tana jin nauyin ka sosai, ka bari na tambaye ta zata fi sakewa ta faɗa min.” Abiy ya kalli Mama ya ce, “ni baƙonta ne da take jin nauyina?.”

“Amma ka san maganar aure ce, dole zata ji nauyi sosai.” Abiy ya ce, “to ki tambaye ta sannan ku dawo tare.” Mama ta miƙe ta riƙe hannun Nayla suka shiga ɗaki.

Suna shiga dakin Mama ta kalli Nayla ta ce, “Meyasa kike jin tsoron faɗar abinda yake zuciyarki ne? Na faɗa miki kar ki ji tsoro Ina tare da ke amma kin ƙi ji ko?.” Nayla ta ce, “nauyin Abiy nake ji, kuma sai nake ganin kamar bazai ji daɗi ba.”

“Baki yarda dani ba ne?.”

“Na yarda Mama.”

“To ki faɗa masa ke Omar kike so, shine wanda ki ke burin aure.”

“To Mama, Allah ya sa na iya.”

“Zaki iya. Indai da gaske kina sonsa zaki iya, ki rufe ido kar ki kalli idon mahaifinki, ki saurare zuciyarki duk abinda yazo zuciyarki kawai ki furta.”

Nayla cikin gamsuwa da ƙarfin guiwa ta ce, “To Mama zan yi.” Mama ta ce, “nutsu ki biyo ni” ta faɗa. tana fita ta bar Nayla. Nayla addu’a ta fara yi a zuciyarta sannan ta fito ta samu Mama a zaune inda ta tashi itama taje ta zauna inda ta tashi. Abiy ya kallli Mama ya ce, “me ta yanke?.” Mama ta kalle shi ta ce, “Omar ɗin dai.”

Abiy ya kalli Nayla bayan ya ɗan ɗaure fuskq ya ce, “Nayla bani amsa.” Nayla ta rufe ido kamar yadda Mama tace, ta yi shiru tana sauraron bugun zuciyarta sannan ta ce, “Eh Abiy. Shi nake so kuma shi nake so na aura.” Shiru tayi kuma bata buɗe idon ba. Jin shiru yayi yawa ya saka ta buɗe ido taga yadda Abiy ya kafa mata ido yana kallo ko kiftawa baya yi. Ajiyar zuciya yayi ya tashi zaune sosai ya haɗe hannayensa waje ɗaya ya ce, “Omar ɗin Kano kike so ko?.” Ta sunkuyar da kai tare da ɗaga kai alamun eh.

“Faɗa min meye sana’arsa?.” Nayla tayi shiru bata ce komai ba. Abiy a kausashe ya ce, “kar na sake tambayar ki kiyi min shiru!.” Nayla ta gyara zama cikin rauni da sanyin murya ta ce, “ance yana sana’a yanzu.”

“Okay, da fa?.” Nayla ta diririce sosai a raunane take magana ta ce, “ban sani ba Abiy.”

Abiy ya ce, “Faɗa min aikin da ke kika san yana yi.” Nayla saboda tsoro har zufa take yi duk da sanyin a.c da yake tashi a falon, ta ce, “ban san yana ko wanne aiki ba.” Abiy ya ce, “yanzu in kika je neman sa unguwar su Hajja wanne suna za’a faɗa da za a gane shi?.” Nayla ta ce, “Tiger.”

“Meyasa ake ce masa Tiger?.”

“Saboda ɗan daba ne.”

“Meye aikin ɣan daba?.” Tayi shiru bata amsa ba, cikin tsawa Abiy ya ce, “ba magan nake miki ba!?.” Nayla ta tsorata ta ce, “ɗaukar wuƙaƙe.”

“Su yi me da wuƙar in sun ɗauka?.” Nayla hawaye ya sakko mata cikin muryar kuka ta ce, “su yanki mutane.”

“Ko su kashe su ko?” Ya tambaya yana tsare ta da idanu. Ta ɗaga kai alamun eh. Numfashi ya sauke ya kalle ta yayi shiru zuwa wani lokaci kafin ya ce, “duk da tarin abubuwan nan da kika faɗa a kansa kike iya kallona kina cewa kina sonsa Nayla?.” Ta sunkuyar da kai tana goge hawaye cikin karayar zuciya.

Abiy ya canja murya zuwa tausasawa ya ce, “Akwai abinda na rage ki dashi a gidan nan?.”

“Babu komai Abiy.”

“Meyasa kika sake maimaita min kina son ɗan daba Nayla?.” Muryarta fara rawa sai ta kasa magana ta fara kuka sosai. Abiy ya ce, “Nayla! Daga yau, daga yanzu, daga wannan lokaci kar na sake jin kin furta wannan maganar, in har na isa dake kar na sake ji kince ke shi kike so in ba haka ba wallahi zaki dana sani a cikin rayuwarki. Sannan ki yi gaggawar mantawa dashi kafin na saɓa miki. Zan iya ɗaukar ko wanne shirme amma banda wannan, zan iya baki aure mai gadin gidan nan amma banda shi.”

Kuka take yi bata iya cewa komai ba. Abiy ya fusata matuƙa ya ce, “akan sa ki ke kuka!? A kansa kike zubar da hawaye!?.” Nayla ta girgiza kai alamun a’a tana kuka.

“To kiyi shiru ki goge wannan hawayen.” Da sauri ta goge idanunta jikinta har rawa yake yi dan bata da tsawar abiy ba.

Abiy ya ce, “inda ace mutum ne gari na sai na amince miki ki aure shi, inda mutum ne kamar kowa sai amince miki, inda mutum ne mai hankali da ɗabi’a mai kyau sai na amince miki. Amma bazan aurar dake ga namiji irin sa ba, in ma kina wannan mafarkin ki daina, dan baza ki aure shi ba sai dai in bani da rai!!.”

Abiy ya sake cewa, “Dan haka ki goge labarinsa a zuciyarki shine kwanciyar hankalinki kin ji ko?.” Ta ɗaga kai alamun to tana share hawaye. Abiy ya kausasa murya ya nuna ta da yatsa ya ce, “gargaɗi na ƙarshe Hauwa, wallahi kar na sake Jin wannan maganar a bakinki, in dai na isa dake ki ajjiye batun nan, in kuma ban isa dake ba na sake jin wannan maganar Nayla!.”

Nayla tana kuka ta ce, “bazan sake ba Abiy, bazan sake ba. Ka yi haƙuri. Nima ban san na fara sonsa ba, ban san ina sonsa ba. Wallahi Abiy da zan iya mantawa dashi

da tuni na manta, na kasa Abiy, na kasa mantawa!” Ta faɗa cikin fitar hankali ta manta ma abinda take cewa.

Zuba mata ido yayi jin abinda take cewa kafin ya ce, “kina faɗa min kin kasa mantawa dashi ni kuma nace ki manta dashi Hauwa! Dole ki manta dashi, ko kina so ko bakya so. Ba sa’an aurenki bane, ba daidai yake yake ba, rayuwarsa da taki ba iri ɗaya ba ce!.” Sai da ta firgita jin tsawar da Abiy yayi mata ta sake fashewa da kuka cikin ƙunar zuciya da tsoro.

Abiy ya tausasa murya ya ce, “ki daina kuka, ki tashi ki bani waje, kije ki cigaba da addu’a Allah ya cire miki shi daga zuciyarki. Sannan ki tabbatar da kin fitar da wanda kike so in ba haka ba wallahi zan bayar dake ga wanda na ga dama.” Kuka take yi har lokacin cikin wani yanayi da bata san na meye ba. Abiy ganin yadda take kuka kamar ranta zai fita sai ransa ya sosu yaji kamar tausayinta, ya san bai saba yi musu tsawa ba dole ta yi kuka tunda bata saba ba, yayi tsaki ya kalleta ya ce, “tashi ki bani waje.” Da sauri ta miƙe ta fita daga falon a guje har tana tuntuɓe.

KRB2P019

Da kallo Abiy ya bita har ta fita yaja dogon tsaki cikin ɓacin rai ya ce, "wai tana sonsa, kuma bai ma san tana yi ba. Mtsw! da gaskiyar Senator da yace asiri yake yi, nima gashi ya yiwa tawa ƴar. To in ba asiri ba me zai kai Nayla ta ce tana sonsa?. Sai yanzu naji irin abinda Sagir yaji a lokacin da yaje gidansa ya ce yana son Narma. Ashe abun akwai ciwo da ƙunar rai, amma a lokacin da ya faɗa min ɗauka nake rashin haƙurinsa ne kawai." Mama da take gefe ta ce, "ni babban tashin hankalina ma kar ta aikata wani abu wallahi, yanayinta da maganarta kawai zaka ji ka san bata haƙura dashi ba."

Abiy ya ce, "babu abinda zatayi. Kuma da ace yana da halayya mai kyau da background mai kyau me zai hana a bashi ita tunda tana so? To bashi da shi, taƙadarin ɗan daban ne lamba ɗaya wanda ake jin tsoronsa a ko ina, ko meye abin so a wajansa oho."

"Ai ko yana da hali mai kyau meye amfanin bashi aure? Babu wanda ya san asalin su fa, su biyu kawai suke rayuwa. Ga samarin da suka kasance daidai da ita shi ɗin banza? Don Allah ka daina wannan maganar raina ɓaci yake yi."

Abiy ya sauke zuciyar ya ce, "kawai ku fara shirye-shiryen biki, dan bazan sake bata Lokaci ba a wannan karon, zan aurar da ita kawai. Da zarar ta san ta yi aure ai baza ta sake ambatar sunansa ba." Mama tayi ajiyar zuciya itama kafin ta ce, "Allah sarki, amma tana sonsa da gaske." Abiy ya kaawar da kai bai ce komai ba amma zuciyarsa gabaɗaya babu daɗi. Bai saba yiwa yaransa faɗa ba, bai saba saka su kuka ba shiyasa da ya ga Nayla tana kuka sai ya ji zuciyarsa babu daɗi gabaɗaya.

Mama wajan Nayla ta shiga ta same ta a zaune tayi tagumi amma ta daina kukan. Mama ta zauna a gefenta cikin rarrashi ta ce, "Nayla kar ki damu da faɗan da Abiy yayi miki, zai dawo daidai." Nayla a sanyaye ta ce, "ni na haƙura Mama, zanyi abinda Abiy yake so." Mama ta ce, "baza ki haƙura ba, na faɗa miki sai kin samu cikar burin ki tare da amincewar mahaifinki. Abinda nake so dake kawai ki kwantar da hankalinki, ki cigaba da harkokin ki zan san abinda zan yi."

"Mama Abiy yayi fushi, kina ganin Abiy dai faɗa yake yi min abinda baya yi, ni na haƙura kawai. don Allah Mama ki bashi haƙuri ki faɗa masa da gaske na manta da wannan batun har abada."

Mama ta dafata cikin rarrashi da murya mai sanyi ta ce, "Kar ki damu, shima yanzu yake faɗa min da ya sani bai yi miki faɗa ba ya san ba yin kanki bane soyayya ce ta kawo hakan. Amma ki nutsu babu abinda zai faru kin ji?." Nayla ta ɗaga kai alamun to ba dan ta yarda ba. Mama ta dinga rarrashinta cikin kalamai masu daɗi har Nayla ta ɗan saki jikita kuma yarda da kalaman Mama sosai.

Haka Nayla ta kwana tana ciwon kai, da safe haka ta tashi daƙyar ta tafi aiki, da taje can ma sai da suka kai ta asibiti saboda ciwon kai ya takura mata. A asibiti ta yini aka saka mata ruwa bayan an kira gıda an faɗawa Mama. Sai yamma suka koma gida Abiy bai ce mata meye dalilin ciwonta ba ya dai yi mata sannu daga nan bai ce komai ba. Sai da daddare suna zaune gabaɗaya har su Yaya a falo tana cin abinci kamar bata so saboda har lokacin bata jin daɗin jikinta.

Yaya ne ya kalle ta da kulawa ya ce, "Nayla wai ne yake damunki ne? Gabaɗaya kin canja, bakya walwala, bakya hira, kuma kin rame. Meye a zuciyarki?." Abiy ya kalle ta sannan ya kalle shi ya ce, "Soyayya ce." Yaya ya kalli Abiy da sauri ya ce, "Abiy soyayya kuma? Wa take so?." Abiy ya sha tea ya kalle shi bayan ya ajjiye mug ɗin yana juya spoon a ciki ya ce, "Ina wani yaro da shekarun baya ya taɓa taimakon ta lokacin da za a yi raping ɗinta a Kano?."

"Wannan ɗan daban kenan, na gane shi."

Abiy ya sha tea ɗin sannan ya ce, "to shi take so. Akansa ta komai haka gabaɗaya." Jawad da ya wara idanu ya ce, "Mun shiga uku, Tiger ɗin take so Abiy?." Abiy ya ɗaga masa kai alamun eh Yaya ya kalle ta ya ce, "Nayla Tiger ki ke so?." Bata iya magana ba sai sunkuyar da kai da tayi tana juya spoon a cikin abincin ba tare da ta ci ba.

Yaya ya kalli Abiy ya ce, "Abiy kai me ka ce to?." Abiy ya kalle shi ya ce, "kaiɓa ai uba ne a wajanta, yanke naka hukuncin naji." Yaya ya ce, "Abiy ai tun wuri ta ajjiye wannan batu a zuciyarta, banda shirme da rashin hankali ta rasa wanda zata ce tana so sai wancan ɗan shaye-shayen mai kashe mutane?."

"Wallahi baya shaye-shaye!."

A tare suka kalli Nayla jin abinda ta ce, itama sai take kallon su dan bata san abinda tayi ba ta ga dai ana kallonta. Gabanta ya yanke ya faɗi, kenan a zahiri tayi maganar tunda taga kowa kallonta yake yi har Mama da Abiy. "Innalillahi wa'inna ilahir raji'un!" Ta furta a sanyaye jikinta ya gama yin sanyi. Ta san halin Yayan su akwai saurin fusata yanzu sai ya gaggaura mata mari saboda wannan maganar da tayi.

Abiy yayi dariya ya ce, "to gashi nan ta baka amsa, masoyinta baya shaye-shaye." Yaya ya fusata sosai ya kai hannu kamar zai maketa sai ya fasa ya ce, "ni kike faɗawa baya shaye-shaye? Kin fini sanin sa ne!?." Sai data firgita saboda tsawar da yayi mata.

Jawad ya kalli Abiy ya ce, "No wonder ko yaushe tace zata je Kano mana, ashe shi take zuwa gani tunda maƙoncin Hajja. Ka duba ranar da suka zo gidan nan da Yayarsa, gabaɗaya Nayla ta rikice ta kasa zama, a lokacin na ɗauka murnar ganin Yayarsa ne ashe saboda shi ta fita hankalinta." Yaya ya ce, "baza ta sake zuwa Kano ba, daga yau na soke zuwan ki Kano. In kinga kinje Kano to tabbas babban abu ne da ya kamata ace kin je!" Ya faɗa da ƙarfi yana nunata da yatsa.

Yaya ya kalli Abiy yace, "Abiy ba shine wanda ka ce Senator Sagir ya kama shi a Abuja ba?."

"Shine Babana, ni tazo ta saka a gaba tana kuka tana cewa tausayin Yayarsa take ji da surutai kala-kala, ashe nima case ɗin yana nan tafe zuwa gidana."

"Ai in tayi gangancin gayyato shi gidan nan wallahi na saka anyi masa dukan da za a karshi lokaci ɗaya. Meye abin so a wannan abun don Allah? Hasken fatarsa ne ya ɗauke ki ko me?" Ya faɗa yana kallon Nayla da bata ce komai ba ko hawayen ma sun ƙafe.

Jawad ya ce, "Nayla in soyayyar ce baki wuce zuciyarki ta fara son wani ba, amma ki so wanda ya dace ya cancanta ba wannan ba. Ki ce kina son wannan ki ce kin son me don Allah? Ɗan daba mai kashe mutane ko karen yan siyasa?. Wai to shi yana sonki?." Abiy ya murmusa ya ce, "bai ma san tana yi ba Jawad." Yaya ya kalle ta cikin jin haushi da takaici ya ce, "wallahi kin bani kunya Nayla, ina Abbas, Ina Hashim, Ina sauran mutane biyun da suke sonki? Duk basu yi miki ba sai wannan mara aikin yin ne ya yi miki?."

Shiru bata tanka ba kanta na ƙasa sosai kayan jikinsu kawai take gani ban da fuska. Mama ta ce, "Yayansu ka yi mata a hankali mana, ka daina yi mata faɗa haka." Yaya ya kalli Mama ya ce, "Mama Nayla fa ba yarinya bace, tana sane duk abinda yake yi wallahi."

Yaya ya ce, "Abiy ka bani ita mu tafi Lagos, in yaso zan saka ayi mata transfer na aikinta zuwa can. Zan dawo da ita bayan na tabbatar ta bar wannan banzan tunanin."

"A'a, ka barta a nan ana gama azumin Ramadan aure zata yi. Ku fara shirin aurar da ita dan ba za a ɗauki lokaci ba."

Jawad ya ce, "shikenan an huta." Sai sake jagalgwala nmaganar suke yi ita dai Nayla bata iya ce komai ba. Ta ɗauka ma Ya J zai sassauta mata saboda shine mutuminta sai taga shima sai masifa yake yi kamar tace tana son wani ƙaton arne.

Gajiya tayi da zaman kar ta tashi ta sake yin laifi, sai da taji sun yi sanyi da maganar sannan ta miƙe ta hau sama dan ta kwanta. Bacci yaƙi zuwa idon Nayla, tana ganin kiran Salma na shigowa amma bazata iya ɗagawa ba ta kawar wayar gefe ta rasa abinda zata yi ta ji daɗi. Abin mamaki har biyu na dare idanunta biyu, sai kawai ta miƙe tayi alwala ta zo ta tayar da sallah, tana sallah tana kuka. Yadda take kuka a suujjada tana faɗawa Allah damuwarta ma abin taɓa zuciya ne. Sai gab

da asuba ta fara jin bacci, ta hana idanunta bacci sai da tayi sallah sannan ta kwanta.

Sai sha biyu ba rana ta farka, bata fito ba sai da tayi wanka kasancewar alhamis ce azumi take yi baza ta fita ta karya ba. Tana nan zaune Mama ta shigo ɗakin ta bita da kallo ganin ta rame daga jiya zuwa yau, ta zauna ta ce, "Nayla kinga yadda ki ka koma kuwa?."

"Mama Ina kwana" ta faɗa tana kallon ta.

"Lafiya lau, ya ciwon kan?" Ta faɗa tana taɓa kanta. Mama ta ce, "har yanzu akwai zafi a kanki Nayla. Meyasa baza ki sassautawa kanki wannan damuwar ba?."

Nayla tayi shiru bata ce komai ba. Mama ta ce, "na san kina son Omar, Allah kaɗai ya san me kike ji a zuciyarki. Kar ki damu da maganar Yayanki da mahaifinki zan san abinda zan yi."

"Mama da ace na san inda zan ajjiye son da nake masa da na ajjiye, da ace na san inda zan cire zuciyata da na cire na ajjiye Mama. Amma na kasa, nayi addu'a babu adadi amma ban taɓa jin abinda nake ji a kansa ya ragu ba Mama. Ya zan yi? Su Yaya sun kasa gane ba yin kaina bane, sai faɗa suke yi min....." ta faɗa cikin rauni.

"Ni na fahimce ki shiyasa nace Ina bayan ki a ko yaushe. Abinda nake so dake yanzu ki kwantar da hankali ki nutsu, ki tashi ki shirya kayan ki kala uku zan saka a kai ki Kano." Da sauri Nayla ta kalli Mama da mamaki ta ce, "Kano kuma Mama? Baki ji abinda Abiy da Yaya suka ce ba?."

"Na ji, duk duniya babu wanda ya san waye mahaifinki kamar ni, na san abinda zai ɓata masa rai na san abinda zai yi saurin saka shi ya bar fushi. Sannan Yayan ki abinda Abiy ya ce shi zai yi, in Abiy ya bar fushi ya amince da Omaar shikenan. Dan haka Abiy ne abin jin ba Yayanki ba."

"Mama meye amfanin zuwa Kano to?."

"Saboda ki samu nutsuwa, kuma sannan ni zan cewa Abiy saboda kin yi masa laifi ya saka ki ka tafi gidan Twiny dan ya huce. In kinje sai ki yi masa text na ban haƙuri ki turo masa,in kika kwana biyu zuwa ranar Sunday sai ki dawo shikenan." Nayla ta

yi shiru tana kallon Mama kafin ta ce, "Mama anya hakan ya yi? Kar Abiy ya yi fushi dani."

"Bazai yi fushi dake ba, kar ki damu. Ki tashi ki shirya ko bakya son zuwa Kano ɗin?."

Nayla ta ce, "Ina so, amma....."

"Kar kiyi wani tunani, ki tashi ki shirya kawai na saka a kai ki. Amma ki tabbatar kin yi masa text na ban haƙuri tare da addu'a. Kuma kar ki faɗawa mutanen Kano ni na ce ki kije, sannan ko Abiy ma kar ki ce masa ni nace ki je. Abinda ya sa na ce haka in kika ce masa ni na ce ki je zai ga kamar ba ke kika yi niyar bashi haƙuri ba ni na saka ki."

Nayla tayi shiru alamun tunani Mama ta dinga rarrashi tana faɗa mata kalaman da taji a ranta zata je Kano. Nayla ta yi ajiyar zuciya ta ce, "To Mama" ta faɗa tana tashi ta haɗa kaya kamar yadda Mama ta ce ta riƙo hannunta har bakin ƙofar ɗakin sannan tace taje. Mama tana tsaye a balcony tana kallon Nayla har ta shiga mota suka wuce.

Da hanzari ta koma ciki ta ɗauki waya hannuta na rawa ta kira Abiy yana ɗauka ta ce, "Abiy Nayla na cikin damuwa, Nayla tana cikin damuwa tana ta maganganun cewa in ba a barta aurensa ba zata iya kashe kanta. Don Allah ka dawo."

"Mtsw ƙyaleta, babu abinda zata iya,

In na dawo zamu yi magana" yana faɗa ya yanke wayar Mama tayi murmushi ta ce, "Bye bye Nayla" ta faɗa tana sauke ajiyar zuciya ta ce, "mu jira dawowar Abiy."

••••••••

Nayla sai bayan la'asar ta shiga gidan Hajja, Baba Salisu ya sauketa ta shiga cikin gidan da sallama. Salma na ganin ta miƙe ta ƙaraso ta rungumeta tana cewa, "Oyoyo Nayla, sannu da zuwa." Nayla ta ɗaga kai ta ce, "Salma bani ruwa na kaiwa Baba ya sha." Amsawa tayi Salma ta fita da kanta ta kaiwa Baba ruwa sannan ta dawo ta zauna.

Nayla ta kalli Salma ta ce, "bara na yi sallar la'asar." Ɗaki ta shiga tayi wanka tare alwala tayi sallah ta canja kaya zuwa marasa nayi ta fito. Baba Salisu ta tarar yana gaisawa da Hajja sannan ya yi mata sallama ya koma Kaduna.

Nayla ta kalli Hajja ta ce, "Hajja Ina yini."

"lafiya lau Hauwa, ya jikin naki?."

"Da sauƙi" ta faɗa a sanyaye kai da ka ganta ka san bata cikin nutsuwarta. Salma ta kalleta ta ce, "Me ya faru na ganki katsam haka? Kuma gobe juma'a akwai aiki?." Nayla ta girgiza kai ta ce, "bani da lafiya ne bana zuwa ma aikin Kwana biyu, Nazo nan na huta, in na huta sai na koma."

Salma ta ce, "amma ana ganinki a san akwai damuwa a lamarinki." Nayla tayi ajiyar zuciya ta ce, "babu komai" ta faɗa tana tashi ta shiga ɗaki. Hajja ta ɗaga murya ta ce, "baza ki ci abinci ba?." Daga ɗakin ta ce, "azumi nake yi."

"Kina azumi ki ka yo tafiya Hauwa?" Hajja ta faɗa amma Nayla bata amsa ba. Hajja ta kalli Salma ta ce, "me yake damun Nayla ne haka?:"

Salma ta sauke numfashi ta ce, "bara ta huta yau sai ta faɗa min abinda yake damunta, bara na bata lokaci ta samu hutu." Hajja ta ɗaga kai kawai bata ce komai ba amma zuciyarta na faɗa mata akwai wani abun da yake damun Nayla.

A can Kaduna sai bayan sallar i'sha kamar ko yaushe suna zaune an gama cin amma babu Nayla. Abiy ya kalli Jalil ya ce, "jeka ka kira min Yayarka Nayla." Da sauri ya tashi ya hau sama zuwa ɗakinta, ba jikawa ya dawo ya ce, "Abiy bata nan." Abiy ya ce, "bata nan kuma?" Ya faɗa yana kallon Mama. Mama ganin yana kallonta sai ta ce, "tun ɗazu ban shiga ɗakinta ba ban san ita take ba, tun lokacin da muka yi waya da kai ban sake shiga wajanta ba gaskiya."

Jalila ƙanwar Nayla da ta shigo falon a lokacin ta ce, "A'a Mama ni ɗazu naga Anty Naya ta shiga motar Baba Salisu fa, na kuma ganta da jaka a hannunta na ɗauka ma kano ta tafi." Mama ta ce, "jaka kuma? Nayla ɗin?."

"Eh Mama." Abiy bai ce komai ba ya ɗauki waya ya kira Baba Salisu nan yake tabbatar masa da ya kai Nayla Kano.

Mama ta ce, "Innalillahi wa'inna ilahir raji'un! Ba dai maganar da ta faɗa ɗazu ta aikata ba? Na shiga uku, daman tace zata bar gidan nan in dai ba a yi mata abinda take so ba kuma baza ta sake dawowa ba" ta faɗa hannu na rawa tana kiran wayar Nayla. Da yake a speaker ta saka kowa yana jin lokacin da wayarta ce baza ta shiga ba.

Yaya da ya shigo a lokacin yaji abinda ake faɗa ya ce, "Wai Nayla ce ta bar gidan nan saboda ɗan daba?." Mama ta ce, "ta tafi Kano ba tare da sanin mu ba gabaɗaya, Allah ya sa tana lafiya." Abiy dai ya kasa magana ya yi shiru bai ce komai ba dan bai san me zaice ba, zuciyarsa zafi take yi akan abinda Nayla ta aikata wanda bai taɓa tunanin zata yi ba. Ƙarar shigowar message yaji a wayarsa, ya ɗauki wayar ya duba yaga ta Whatsapp ne kuma sunan Nayla. Da sauri ya bue yana karanta abinda ta rubuto masa a zuciyarsa.

Abiy ajiyar zuciya yayi bayan ya gama karantawa yayi shiru na wani lokaci. Kallon Jawad da Ahmad yayi ya ce, "Gobe da safe kuzo zaku raka ni wani waje, amma kuzo da wuri ina so mu isa kafin lokacin sallar juma'a" Abinda yace kenan kawai ya miƙe ya shiga ɗaki zuciyarsa cike da ɓacin ran abinda Nayla tayi masa.

Da sauri Mama ta bi bayan sa ta ce, "Abiy me ya faru?."

"Babu komai, ki bani waje zan huta."

"Ka gwada kiran Nayla ko zaka same ta, Ina so na tabbatar da tana lafiya." Cikin tsawa Abiy ya ce, "nace ki bani waje ko!?." Da sauri ta fita daga ɗakin ya kulle ƙofar.

Bayan fitar Mama waya ya ɗauka ya saka a kunne ya ce, "zan turo maka sunan wani yaro a nan cikin Kano unguwar ƙofar nasarawa, ka tabbatar a daren nan ka nemo min waye shi" yana faɗa ya yanke wayar ya cillar da ita a kan gado zuciyarsa na yi masa zafi.

Babu abinda ya ɓata masa rai a abinda Nayla ta turo masa kamar da tace tayi zata iya barin kowa saboda Omar, In ya tuna irin kalaman da ta yi amfani dasu wajan a saƙon da ta turo masa sai yaji kamar ana soka masa kibiya a zuciyarsa saboda ɓacin rai da baƙin ciki da takaici.

Ranar a gidan gabaɗaya kowa zuciya babu daɗi, Mama ce kawai take farin ciki amma dukkan su babu wanda yaji daɗin abinda Nayla tayi.

Washe gari.

Wai me Nayla ta aikata ne? Wanne irin saƙo ta turowa Abiy haka? Ina su Abiy zasu je?.....A kafta□□

KRB2P020

Arewabooks@nanahaleema11

Ƙarfe takwas na safiyar ranar juma'a Abiy ya sakko daga sama yana ɗaura agogo a hannunsa. A ƙaramin falon ƙasa ya tarar da Mama ta kalle shi ta ce, "Ina zuwa haka da sassafe? Kun yi magana da Nayla kuwa? Ina kiranta har yanzu bana samu." Abiy ya kalle ta ya ce, "ba mu yi waya ba, bana buƙatar yin wayar da ita. Ina su Jawad?." Mama ta ce, "suna main parlor tun ɗazu." Abiy bai ce komai ba ya wuce zuwa falon.

Yana shiga duk suna tashi suna kallon sa suka gaishe shi ya amsa kana ya ce, "Ku zo mu je." Ba musu duk suka bi bayan sa. Jawad ya shiga mota mazaunin driver Abiy ya shiga baya Yaya ya zauna a gaba suka fita daga gidan. Sai da suka hau titi sannan Jawad ya ce, "Abiy ina zamu je."

"Kano" ya bashi amsa ba tare da ya kalle su ba. Basu tambaye shi ba kawai Jawad ya ɗauki hanyar fita daga Kaduna.

Nayla kuwa a lokacin idanunta biyu ta kasa komawa bacci, ganin ƙarfe tara na safe tayi sai ta miƙe tayi alwala ta tayar da sallar walha. Sai da tayi raka'a ashrin sannan tayi addu'a zuwa lokacin har goma na safe ta kusa. Wayarta jawo dan tun jiya bata duba ba ta shiga WhatsApp ɗinta. Abin mamaki an yi hacking account ɗinta, tsaki tayi ta fita ta shiga Google ta duba yadda zata dawo da account ɗin tana karanta yadda zata bi ta dawo dashi.

Salma ce ta shigo hakan ya saka ta ajjiye wayar ta ce, "wai WhatsApp ɗina aka yi min hacking." Salma ta ce, "ai zaki iya dawowa dashi ba wahala ne dashi ba, ki dai yi gaggawa kar a fara tambayar mutanen contact ɗinki kuɗi." Nayla ta ɗauki wayar ta ce, "bara na gani" ta faɗa da tana bin steps ɗin da ta gani a google har ta dawo

dashi. Tsaki tayi ta ce, "ikon Allah, an goge min wasu messages ɗin, suka sani dai" ta faɗa tana ajjiye wayar a kusa da ita.

Kallon Salma tayi da take kallonta sai ta ce, "yaushe zamu je gidan Didi? Ina so naje kafin na koma Kaduna." Salma ta ce, "sai muje anjima in zaki iya. Amma kafin nan Nayla me yake damunki?." Nayla ta ce, "Salma nima bana ce ba wallahi, komai baya yi min daɗi. Babban abin tashin hankalin ma Abiy ya san maganar Omar." Zaro ido Salma tayi ta ce, "mun shiga uku! Kamar ya ya sani? Ta wacce hanya ya sani?."

"Ashe lokacin da muke maganar nan a gidan mu na Kano Mama taji. Mama tana goyan bayana akan soyayyata dashi, hakan ya saka ta sanar Abiy shi nake so ko zai amince. Hmmm Salma! Abiy bai taɓa yi min faɗa kamar lokacin ba, kai tsaye ya ce min Hauwa sunan da bai taɓa faɗa ba."

Salma ta dafe ƙirji ta ce, "Innalillahi wa'jnna ilahir raji'un!. Yanzu ya ake ciki?."

"To bana ce ba dai, ya ce dai duk yadda zan yi nayi na fitar da mijin aure in ba haka ba zai bani wanda ya ga dama. Daman na san bazan taɓa mallakar abinda nake so ba Salma, shiyasa ni zan bawa Abiy haƙuri ya zaɓa min duk wanda ya ga dama. To Mama ce take bani bani ƙarfin guiwar zai iya amincewa da Omar."

Salma ta ce, "Gaskiya Abiy bazai amince da Omar ba, gwara ma ki daina yaudarar kanki. Duk dani shaida ce Omar ba kamar da ba yake ba yanzu ya canja, harkar sana'arsa yake yi kuma Allah ya saka masa albarka. Ke in kika ga takalman da Omar yake yi sai abin ya baki mamaki, sai kin ce daman yana da wannan talend ɗin ya zauna yana ɓata rayuwarsa a banza da wofi.....huhh amma duk da haka rayuwarsa ta baya zata saka a ƙi bashi aure Nayla. Musamman auren irin ki, mai ilimi, nasaba, kyau da sauran su."

Nayla ido ya kawo ruwa ta zubawa Salma ido ta ce, "da gaske kike yanzu Omaar ya koma yin sana'a sosai?."

"Da gaske nake wallahi, bara na nuna miki handles ɗin su da suke posting kayan. Naga didi ta saka a status, shine naje na gani ke baki ga abu ba baza ki ɗauka Omar yana da wayewar yin abubuwa haka ba" Tana faɗa tana danna waya tana duba page ɗin.

Nuna mata wayar tayi ta ce, "kin gani.. wannan shine irin takalman da Omar yake yi yanzu. Shiyasa zaman unguwar nan ma yanzu ba yi yake yi sosai ba, ko yaushe baya nan suna shago suna aiki." Nayla kalla take yi zuciyarta na rawa sosai kafin ta sauke kai ta yi ajiyar zuciya ta ce, "wataƙila babu Omar a cikin ƙaddarata."

"Calm down, ki cigaba da addu'a komai zai wuce. Kuma ba kince Mama na supporting ɗinki ba?."

"Ita kaɗai ba, Yaya cewa ya yi a bashi ni mu tafi Lagos sai na dawo hankalina na dawo gida. Yaya J ma da yake aminina shima yana bayan Abiy. Gabaɗaya jina nake wani iri wallahi."

"Ki dai yi haƙuri. Yanzu ki tashi kiyi wanka, kiyi break sai mu je gidan Didi." Nayla ta ce, "Ina so naje gidan Twiny ma."

"To ki tashi mu shirya." Nayla tayi ajiyar zuciya ta tashi ta shiga banɗaki cikin damuwa mai yawa.

Su Abiy lokacin da suka shigo Kano umartar Jawad ya yi da su wuce gidan su na Kano. Kai tsaye nan suka wuce kamar ko yaushe. Mai gadin gidan jin ana horn ya buɗe ya ƙaraso ganin mai gidan ne da kansa ya saka ya buɗe suka shiga cikin gidan. Falon gidan suka shiga bai yi dauɗa ba sai dai yaɾar ƙura kaɗan mara yawa.

Abiy ya kalle su ya ce, "ku huta zuwa sha biyu da rabi zamu fita." Amsa masa suka yi ya shiga ciki. Ahmad ya kalli Jawad ya ce, "Wai me yake faruwa ne? Me muka zo yi Kano?."

"Wallahi ban sani ba Yaya, abinda na sani kawai jiya Nayla ta bar gida ta taho nan Kano. Da Fari na ɗauka gidan Hajja ɗin zamuje sai naji ya ce mu zo nan." Da mamaki Yaya ya ce, "ta bar gida ta taho nan? To Akan me?."

Jawad ya ce, "Akan wannan yaron mana, ran Abiy ya ɓaci matuƙa a jiya da daddare."

"Daman Nayla bata da hankali ban sani ba? Ana ganin ta mai kirki da hankali ashe itama yaɾar iska ce?. Ta taho na saboda ance bazata aure shi ba ko me?." Jawad ya ce, "nima ta bani mamaki wallahi, ban ɗauka zata aikata haka ba. Ashe macijin sari ka noƙe ce, a haka sumi-sumi da ita kamar bazata aikata ba."

Yaya ya girgiza kai ya ce, "Lallai tana buƙatar duka, dan sai na zane mata jikinta sannan zata fahimci kuskurenta. Bara Abiy ɗin yazo, ɗauketa zan yi wallahi mu tafi lagos na koya mata hankali a can tunda ita shashasha ce" ya faɗa yana fita zuwa ɗakin da suke zama a cikin gidan.

Ba su jima sosai ba Abiy ya yi musu waya ya ce su fito, suka fito suka tarar dashi a bakin mota suka shiga kai tsaye ya ce su wuce unguwar Kundila. Can suka nufa Abiy yana basu address yadda aka faɗa masa suna tafiya sai gasu har ƙofar gidan Kawu.

A ƙofar gidan suka faka motar Abiy ya kalli gidan da aka tabbatar masa nan ne gidan Kawu. Babban gida ne mai kyau kana gani ka san mai shi yana da abin hannu sosai. Abiy ya kalli Agogo ya ce, "mu ƙarasa masallaci muyi sallah in ya so sai mu dawo." Da to suka amsa suka ƙarasa masallacin da yake kusa suka yi sallar juma'a sannan suka dawo mota.

Abiy da kansa ya tambaya aka nuna masa Kawu da yake tahowa yana amsa waya zai shiga gidan ya dawo daga masallaci. Abiy ya ƙarasa ya ce, "Assalamu alaikum." Ya dakata da wayar ya amsawa Abiy suka yi musabaha kafin Abiy ya ce, "na san baka sanni ba, baƙo ne in babu damuwa Ina so zamu tattauna." Kawu ya ce, "to bismillah shigo." Abiy ya yi musu magana alamun su shigo suka biyo bayan Abiy.

A wani babban falo ya sauke su wanda maza biyu suke a zaune ya kalli Abiy ya ce, "yʻan uwana ne, Ina fatan babu damuwa." Abiy ya ce, "babu damuwa. Na ji daɗin hakan sosai." Kawu ya ce, "Da yake yau muna ɗan ƙaramin taro, an kawo kayan lefen yʻar wajan ƙanina gashi a zaune shiyasa muke gabaɗaya" ya faɗa yana nuna masa Kawu Yusuf. Abiy ya ce, "Allah ya sanya alkhairi."

"Amin ya Allah. sai dai ban sanka ba." Abiy ya ce, "Sunana Alhaji Abdullah Ahmad, ni mazaunin garin Kaduna ne. Nazo wajanka ne akan ɗan ƙaninka Omar ƙanin Aysha." Kawu ya gyara zama ya ce, "to Allah yasa ba laifi ya yi ba." Abiy ya murmusa ya ce, "ba laifi ya yi ba, na zo ne ina nemawa yʻata aurensa a yanzu in hakan zai yu."

Duk mutane wajan mamaki ya kama su, suka bi Abiy da kallon mamaki ba tare da ya basu damar magana ba ya ce, "na san komai, kar ku tambaye ni dalili ko meyasa, ina sane duka abinda nake yi. Kawai in zai yu ina so zan bashi aurenta a yanzun nan a ɗaura auren. Tunda ku ne waliyansa ga nata waliyya a zaune" ya faɗa yana nuna su Jawad da suka yi mutuwar zaune.

Kawu ya ce, "To ai ka kulle mana baki ne, wai ka san wanne Omar ka ke magana akai kuwa?."

"Na sani, tunda kaji har nayi maka kwantacesa da Yayarsa ai ka san na sani. Ni sirikin Hajja ne maƙociyarsu."

Kawu ya ce, "ƙwarai na san Hajja, har gaisheta na taɓa shiga nayi sau biyu, kuma Ina jin labarin alkhairinta sosai a wajan Aisha." Abiy ya ce, "na auri yar Hajja kafin mutuwa ta raba mu, yarinyar da zan aura mata yata ce ta cikina kuma jikar Hajja. Amma naga kamar kuna tantama, in kuna so ku tabbatar ku kira Aisha ku tambayata ku ce ta san Nayla."

"Assalamu alaikum, Kawu ashe baƙi ne da kai bara na koma" aka faɗa daga bakin ƙofa ana ƙoƙarin komawa. Kawu ganin Didi ce sai ya ce, "Aisha shigo mana." Didi ta juyo tana takowa a hankali har tazo tsakiyar falon. Kallon Abiy tayi cikin mamaki ta ce, "Abiy! Ikon Allah kaine a nan?" Ta faɗa da fara'a tana kallon sa. Abiy ya murmusa ya ce, "ni ne Aisha."

"Barka da rana."

"Barkan ki, ya gida?."

"Lafiya lau Abiy, ya su Nayla? Tana lafiya?."

"Lafiya lau." Didi ta kalli Kawu ta ce, "Kawu mahaifin jikar Hajja ne Nayla, kuma shine wanda ya karɓo Omar daga hannun Senator kwanaki da abin nan ya faru."

Kawu ya sauke ajiyar zuciya ya ce, "ya yi min bayanin komai Aisha. Wata magana yazo da ita mai girma, wai yana so a yanzu a ɗaura auren yarsa da ƙaninki Omar." Wara idanu Didi tayi tare da dafe ƙirji cikin mamaki ta ce, "Aure Kawu!?." Ya ɗaga mata ka ta juya ta kalli Abiy ta ce, "Abiy auren Nayla da Omar?."

"Haka nake so, yanzu kuma babu ɓata Lokaci."

Jawad da yake gefe ya ce, "Amma Abiy...." Dakatar dashi yayi ta hanyar ɗaga masa hannu ya ce, "kar wanda ya yi min magana yanzu" ya kalli Aisha ya ce, "Auren zai yu?." Didi ta kasa magana sai kallon Abiy da take yi dan ta rasa abinda zata ce. Abiy ya ce, "in bazai yu ba ki faɗa min kawai." Didi cikin kiɗima ta ce, "Abiy ni wallahi ban san me zance ba, abin nake ji kamar a mafarki. Meyasa ka ke son aurawa Nayla Omar?. Abiy na san ka san Omar ba sai na faɗa maka ba, meyasa haka kwatsam zaka yanke wannan hukuncin?."

"Haka nayi ra'ayi" ya bata amsa a taƙaice.

"Amma Abiy Nayla ba sa'ar auren Omaar ba ce, ka san halin sa ba sai na faɗa ba, kowa ma a nan ya san halinsa ba sai an maimaita ba. Meyasa ka ke son aurawa yɗarka shi don Allah?" Ta faɗa a sanyaye tana kallon Abiy.

Abiy yayi ajiyar zuciya cikin ɓacin ran da yake ciki, danne ɓacin ransa kawai yake yi yana magana amma Allah kaɗai ya san irin yadda zuciyarsa take tafasa akan abinda Nayla tayi masa wanda bai yi tunani ba. Ya ce, "Aisha ki amsa min tambayata kawai, in auren zai yu to in bazai yu ba ki faɗa min."

Didi ta sunkuyar da kai dan bata san me zata ce ba, auren Nayla da Omar kuma...? to akan wanne dalili kenan? Kuma ta tabbatar Omar ɗin ma bai san labarin ba, aka ɗaura auren sa bai sani ba ai an shiga tashin hankalin faɗansa, dan tsaf zai saka yi yaƙin duniya. To ita Nayla ɗin ta sani ko bata sani ba..? Meyasa lokaci ɗaya Abiy zai zo da wannan maganar?.

Kawu ya katse shirun ya ce, "zai yu mana tunda kana so, amma ka san waye Omar kuwa?." Abiy ya ce, "kaf labarin Omar na sani, har wanda baku san dashi ba na sani, har wanda kuke tunanin ban sani ba shima na sani, yanayin alaqarku da duk abinda yake yi na sani. Kawai ina so ku amince min ne yanzu babu ɓata Lokaci."

Kawu ya kalli Didi ya ce, "Aisha ya ki ka ce? Kece uwar Omar, kina ganin kin amince?." Didi tayi ajiyar zuciya bata san abinda zata ce ba wallahi, in ta amince kamar ta cutar da Nayla ne duk da bata san dalilin Abiy na aura mata Omar rana tsaka ba, in bata amince ba kuma kamar bata kyautawa Abiy ba duk da tarin taimakon da ya yi mata bai cancanci haka ba. In ta amince ma aka ɗaura auren da wacce fuska Omar zai karɓi auren?.

Numfashi ta sauke a hankali ta ce, "Ayi abinda Abiy yake so." Abiy yayi murmushi ya ce, "na gode. A yanzu nake so a ɗaura auren nan babu ɓata lokaci."

Kowa mamakin Abiy yake yi kawai kallon suke yi, a take aka kira mazan gidan cousins ɗin Omar kenan aka tara shaidu Kawu ya bada sadaki naira dubu ɗari biyu. Abiy ya umarci Jawad da ya je mota ya ɗauko goro da alewa ba jimawa ya kawo aka shaida saurin aure a wajan. Didi dai tana zaune tana kallon su kamar a mafarki take ganin abin, wai yanzu Nayla ta zama matar Omar, ko da wacce fuska zai karɓi auren ma oho, ko meyasa Abiy ya yiwa Nayla haka oho.

Bayan an ɗaura auren Abiy ya kalle su ya ce, "Na gode sosai da karamcin ku a gare ni, duk da baku sanni ba amma ku ka amince ku ka ƙulla aƙalar aure dani, naji ɗaɗi sosai Allah ya saka da alkhairi ya jiƙan mahaifa. Sannan zaku iya tambayar kowa a garin Kaduna waye Abdullah Ahmad, in sha Allah zaku samu magana mai kyau a kaina."

Kawu Mamman ya ce, "Ni na sanka, mun taɓa yin wani taro an gayyato ka matsayin babban baƙo. Na san labarinka kaf, suma baza su rasa sani ba ai kai ba ɓoyyayen mutum bane." Murmushi Abiy ya yi ya ce, "Na gode. Sai a fara shirin tarewar amaryar nan da kwana biyu masu zuwa in sha Allah."

Kowa kallon Abiy yake yi dan gani suke kamar yana da taɓin hankali ko kuma ba yɗarsa ba ce. A haka yayi musu sallama cikin mutunci tare da karɓar number juna suka rako shi har harabar gidan yana kallon su.

Jawad suna so su yi masa magana amma ya ƙi bada fuska dole suka riƙe bakin su suka bari aje gida. Didi ce ta biyo bayan Abiy ta samu har sun fita zasu shiga mota ta ce, "Abiy." Ya jiyo yana kallonta ta ce, "Don Allah meyasa ka yanke wannan hukuncin akan Nayla?."

Abiy ya murmusa cike da takaici da ɓacin rai ya ce, "ki kwantar da hankaliki babu komai, ki fara shirin karɓar amarya ranar lahadi jibi kenan, ranar Nayla zata tare a gidan mijinta" ya faɗa yana shiga mota suka suma suka shiga suka bar unguwar.

Didi ko da ta koma su Kawu tsare ta suka yi da tambayar anya Abiy yana da hankali kuwa, Didi ta ce, "wallahi yana da shi, mutum ne na gari dattdijo ban san meyasa ya aikata hakan ba. Kuma baka ji Kawu ƙarami ya sanshi ba? Babban mutum ne mai kuɗin gaske a Kaduna, zan iya cewa kaf garin Kaduna an sanshi."

Kawu ya ce, "Nima na san shi Aisha, yana da manya-manyan store a garurun dake cikin ƙasar nan. Kawai tantama nake yi akan anya yana da hankali? In kuwa yana dashi anya ita Hauwa ɗin yɤarsa ce?."

"Wallahi yɤarsa ce wacce yake matuƙar ƙauna, kaf yaransa ma babu kamarta."

"Iko sai Allah, to yanzu shi Omar ɗin ya san labarin nan?."

"Wallahi bai sani ba Kawu, tashin hankalina bai wuce Omar ya sani ba. Ban san da wacce fuska zai karɓi auren nan ba."

Kawu ya ce, "kuma ke zaki faɗa masa ba, Haka zaki same shi ki sanar dashi zai iya fahimtar ki. Sai a fara shiri tunda ya ce jibi zata tare." Didi ta ce, "to Kawu ina Omar yaga gidan ma da zai saka amarya?."

Kawu ya ce, "wannan ba abin damuwa bane, ki san yadda zaki yi dashi, akwai gidan da na siyawa ƙaninki mai sunan Omar Baba kenan, an gyara shi anyi komai babu abinda ba a saka ba, hatta solar an haɗa 24/7. Da yake Allah bai nufa zai zauna a gidan ba kinga an fasa auren, ki lallaɓa Omar ki san dabarar da zaki yi masa sai ya zauna a ciki. Kar sunana ko sunan wani ya fito a kyautar gidan nan, ki san yadda zaki yi dashi amma kar ki ce daga hannuna ya fito. Kuma wallahil azim na bar masa kyauta, yadda na siya da sunan ɗana auren bai yu ba na barwa ɗana na wajen marigayi ƙanina Usman gidan halak malak."

Didi a sanyaye ta ce, "To Kawu, an gode Allah...." Dakatar da ita ya yi ya ce, "Aisha kar ki gode min, muje magana ta gaba." Didi ta ce, "To Kawu. Ni yanzu so nake a san yadda za ayi a tunkare shi tukunna." Kawu Yusuf ya ce, "Aisha wannan ai aikin ki ne, mu a cikin mu akwai wanda ya isa ya tari Omar da wannan maganar ne?."

Sai taji jikinta ya yi sanyi a sanyaye ta ce, "kun isa mana Kawu."

"Ba mu isa ba wallahi, kema kin san bamu isa a wajan Omar ba. Tunda hakan ta kasance naji daɗi da kina nan, da bakya nan tsaf zai iya zuwa ƙofar gidan nan ya tara mana jama'a. Ki je ki san yadda zaki faɗa masa."

Kawu Mamman ya ce, "Aisha ni kuma in za a haɗa lefen amarya kizo ki yi min lissafi zan siyi komai in sha Allah." Didi tayi murmushin yaƙe zata yi godiya ya dakatar da ita ya ce, "kije ki tattauna da Omar kawai."

Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "To Kawu zan yi. Bara jama'a su ɗan ragu a gari sai naje na same shi" ta faɗa a sanyaye tana kallon su. Suka amsa mata ta shiga ciki tana tunanin dalilin Abiy da aikata wannan ɗanyen aiki.

Su Abiy sai da suka tsaya a hanya suka siyi abinci sannan suka wuce gida. Suna shiga Abiy ya ɗauki pack ɗaya na abincin yana ci ba dan yana jin daɗinsa ba sai dan babu yadda zai yi ne. Jawad kam sun kasa ci kallon Abiy kawai suke yi suna jiran ƙarin bayani, ƙarfin hali Yaya Ahmad ya yi ya ce, "Abiy meyasa ka yanke wannan hukuncin akan Nayla don Allah? Wannan ba yukunci bane, taya zaka ɗaura auren ta da wannan yaron?."

Abiy bai yi magana ba Jawad ya ce, "Abiy don Allah meyasa aka yi mata haka? Ko me ta aikata ai yarinya ce sai ayi mata uzuri a tsawatar mata, amma ɗaura mata aure dashi ba hukunci bane ba Abiy." Abiy bai ce musu komai ba ya ajjiye abincin ya tashi ya shiga ciki.

Jawad ya kalli Yaya ya ce, "wannan hukunci ne Yaya? Wannan ai lalata mata rayuwa aka yi ba aure aka yi mata ba. Ko me tayi ai wannan ba hukunci bane, sai a zaunar da ita ayi mata faɗa, in auren ya zama dole sai aura mata wani amma ba irin wannan yaron ba." Yaya cike da damuwa ya ce, "ni ban san ma abinda zan ce ba wallahi, ban san abinda ya saka Abiy ya aikata haka ba. Dan ta ce tana sonsa akwai sai a bata shi? Haba gaskiya Abiy bai kyauta mana ba wallahi." Abincin da basu iya ci ba kenan Abiy ya fito ya kalle su ya ce, "abinda ya kawo mu Kano mu yi, ku tashi mu wuce gida."

A sanyaye suka tashi suka bi bayan sa bayan sun ɗauko abincin har wanda Abiy ya ajjiye. Yaya ne yanzu ya shiga gaba wajan mai tuƙawa Jawad ya shiga kusa da shi Abiy ya shiga baya. Har zai kunna motar Abiy ya tuna ya yi mantuwa ya koma ciki.

Jawad kasa haƙuri yayi ya ɗauki waya ya kira Nayla yayi sa a ta shiga, tana ɗauka kafin tayi magana ya ce, "Malama duk abinda ki ke yi a Kano ki tabbatar kin wuce Kaduna yanzu, ko me ki ke yi ki ajjiye ki wuce gida." Nayla ta ce, "Yaya J rana ta yi yanzu, driver Hajja baya nan waye zai kai ni Kaduna yanzu?."

A tsawace ya ce, "ki san yadda zaki yi ki dawo gida, in ba haka ba wallahi sai ranki ya ɓaci sosai" ya faɗa ya yanke wayar ganin Abiy ya taho. Yana shiga motar Jawad ya ce, "Abiy mu biya gidan Hajja mu tafi da Nayla?." Abiy ya ce, "tare muka zo da ita?." Jin abinda ya ce sai ya yi shiru amma zuciyarsa gabaɗaya babu daɗi akan abinda Abiy ya yi, to babu yadda zasu yi ne dole su yi shiru kamar yadda ya ce. Fita suka yi daga gidan bayan sun bawa mai gadi abincin suka ɗauki hanyar Kaduna.

Nayla kuwa da suka je gidan Didi bata nan sai kawai suka wuce gidan Jidda, suna zaune a Jawad yayi mata waya duk sun ji abinda ya ce. Ta kalli Twiny ta ce, "Yaya J ne yau yake yi min wannan faɗan, yanzu waye zai kai ni Kaduna?." Twiny ta ce, "ke share shi, gobe sai ki tafi. Haka kawai sai yaja Abiy ya yi miki faɗa daman gashi Abiy na fushi."

Nayla ta ce, "yanayin maganar Ya J da ɓacin rai ciki sosai Twiny, ko dai naje na hau motar haya na koma?."

"Ki share shi, gobe da safe sai ki tafi." Nayla tayi ajiyar zuciya ta ce, "Allah ya sa Abiy bai yi fushi da tahowa ta Kano ba, Allah ya sa ya fahimce ni ya yafe min laifin da nayi masa." Suka amsa mata da amin. Hira suke ta janta da ita amma ta kasa sakin jikin saboda bata da walwala ko kaɗan, yamma nayi suka wuce gida a motar gidan Hajja da Salma ta kawo su.

KRB2P021

Su Abiy da suka koma gida bai cewa kowa komai ba sama ya hau ya barsu a wajan a tsaye. Mama ta kalle su ganin fuskar su ɗauke da damuwa ta ce, "Wai ne ya faru ne? Me kuka je yi Kano?." Jawad ya kalle ta ya ce, "dangin wannan yaron Omar muka je, abin mamaki Abiy ya bada auren Nayla, dan yanzu haka Nayla matarsa ce." Mama ta wara idanu waje a zahiri, a baɗini kuma farin ciki ne ya mamaye mata zuciya ta ce, "Aure kuma? Auren Nayla da ɗan daban aka yi?."

Yaya ya ce, "Wallahi shi aka yi Mama, Abiy yaƙi faɗa mana dalilinsa, sannan kuma ya hana mu tamabaya. Yanzu zancen da nake miki an ɗaura auren su ita dashi, kuma ko sani Omaar ɗin bai yi ba, haka Nayla ɗin ma bata sani ba."

"Innalillahi wa'inna ilahir raji'un! Meyasa mahaifinku ya yanke wannan hukunci? Me Nayla tayi masa haka?. Ko dan ta tafi Kano ne ya saka ya yanke wannan hukuncin?." Jawad ya ce, "itama bata da mutunci ai Mama, ban da rashin hankali da shirme meye na barin gida a akan wannan maganar? Na rantse da Allah in ta dawo sai na zaɓa mata kamanni."

Mama ta ce, "bara naje na samu Abiy ɗin naku naji dalilin sa na aikata wannan ɗanyen aiki." Yaya ya ce, "Yauwa Mama, in da hali a kira yaron kawai ya sake ta tunda daman bai san anyi auren ba. In yaso ni a bani Nayla mu koma Lagos ta koma zama a gidana, nayi alqawari zan kula da ita babu wata damuwa irin wannan da zata sake kunno kai." Mama ta girgiza kai ta hau sama da sauri wajan Abiy. Sallar magriba ta samu yana yi sai ta zauna tana zaman jiran ya idar suyi magana.

Koda ya idar lazimi ya fara ta san kuma baya gamawa sai za a yi i'sha gashi ita ta ƙagu tayi magana dashi. Mama ta ce, "Don Allah Abiy ka katse lazumin nan muyi magana. Ta ya za a aurawa Nayla wancan yaron?. Bai kamata a biye mata a aikata abinda take so ba." Ko motsi bai yi ba balle ta saka ran zai bata amsa. Mama ta ce, "Abiy don Allah kace wani abu, ka dakatar da lazumin nan muyi magana don Allah."

Ban ma bai kula ta ba Mama ta zauna tayi tagumi tana kallonsa. Gajiya tayi da zaman ta tashi ta fita shi kam bai ma kalle ta ba. Sai da ya kammala yaji ana kiran sallar i'sha sannan ya tashi ya fito dan zuwa masallaci.

Koda ya dawo a falo ya tarar dasu gabaɗaya da alama zaman jiran sa suke yi. Wucewa yayi ba tare da ya zauna ba suka bishi da kallo ganin ya shiga ciki. Jawad ya ce, "Mama don Allah kije kuyi magana ya bar mu cikin tunani." Mama ta ce, "maganar ce baya so shiyasa ya wuce bai kula mu ba, amma bara na sake zuwa naji" ta faɗa tana hawa saman ta barsu a ƙasa.

Tana zuwa ta same shi ya zauna akan kujera yana kallon tv, ta zauna a kusa dashi ta ce, "abinci fa?." Ya girgiza kai kawai alamun baya ci. Mama ta ce, "maganar dai da baka so ita zanyi Abiy. Meya faru ka yanke wannan hukunci akan Nayla?. Naji

bata kyauta ba amma da ka sani baka yi haka ba." Bai ce mata komai ba itama sai tayi shiru bata sake magana ba.

Katse shirun tayi da cewa, "bata kyauta ba abinda tayi na barin gida, bata kyauta ba maganar da tayi ta ce zata kashe kanta akansa amma Abiy bai kamata ka biye mata ba, Nayla yarinya ce ƙarama bata da hankali har yanzu." Abiy ya kulle ido ya buɗe ya kalli Mama ya ce, "gobe ku shiga kasuwa, duk abinda ake siyawa amarya ku siya mata. Duk abinda za ayi ayi shi a gama ba sai ance za ayi order daga wata ƙasa ba. A siyi komai gobe zuwa ranar Sunday nake so tafi gidan mijinta" yana faɗar hakan ya tashi ya bata waje.

Mama ta ce, "meyasa haka...." Katse ta yayi ta hanyar cewa, "kar ki shigo ki dame ni" yana faɗa ya wuce ɗaki. Mama tayi wani mayaudarin murmushi ta ce, "an gama." Canja yanayinta tayi ta sakko ƙasa wajan su Yaya da Jawad suka bita da kallo ganin yanayinta ya nuna musu alamun rashin nasara. Ta kalle su ta ce, "yace gobe na shiga kasuwa na siyawa Nayla duk abinda ake siya na aure, wai zuwa jibi zata tare." Yaya ya ce, "Mama sai kika ce masa me?" Ya faɗa kamar zai yi kuka.

Mama ta ce, "bai bani damar magana ba, ya kuma kalle ni yace kar na dame shi ya shiga ɗaki ya bar ni a falo." Jawad ya ce, "wai me yake damun Abiy ne har haka? Me Nayla tayi masa da ya canja lokaci guda don Allah?."

"Bata kyauta ba Jawad, abinda tayi ba tarbiyyar da ya baku bace gabaɗaya. Amma shima yayi gagagwar yanke hukunci, Nayla yarinya ce yar ƙarama ba babba ba."

Yaya ya ce, "kome tayi ai bata cancanci haka ba, irin wannan aure kamar bata da gata kawai an ɗauketa an bashi ba tare da yana so ba? Babu kuɗin aure, babu komai hatta sadaki biya masa aka yi. Ko da yake bai ma sani ba." Mama ta ce, "ka wuce gida dare yayi, in yaso gobe zai kuzo mu ji in zai yi mana magana." Jawad ya ce, "ai wallahi gobe in bata dawo ba da kaina sai naje na dawo da ita, shashasha mara hankali da tunani" ya faɗa yana fita daga falon shima ya bi bayan sa.

Mama shiga ɗaki ta ɗauki waya ta saka a kunne kafin ta ce, "Yauwa, in zaka iya ka sake hacking account ɗinta na WhatsApp ka sake turawa Abiy saƙo. In zai yu zan turo maka irin abinda da zaka tura masa yanzun nan." Shiru tayi alamun ana bata amsa kafin ta ce, "karka damu, na tura maka kuɗin ka harda na data ka ƙara." Yanke wayar tayi tana kallon wani wajan daban tana ɗan dukan wayar da hannunta.

Murmushi tayi ta ce, "kwanciyar hankalina shine auren nan ya tabbata, babu ta yadda za ayi na bari a warware shi tunda an riga da an ɗaura. Yadda ban ji daɗi zaman gidan nan ba, yadda Bilkisu ta wahalar dani a rayuwar gidan nan Nayla ma sai ta ɗanɗana irin abinda na ɗanɗana. Muje dai zuwa" ta faɗa tana yanke wayar ta shiga banɗaki zuciyarta fes take dan ta san ta zama silar aurawa Nayla wanda baza ta taɓa jin daɗin zaman aure dashi ba.

•••••••

Didi tana barin gidan Kawu gidan su ta wuce ta samu Omar ɗin a zaune ya dawo daga masallaci yana zaune akan kujera ya ɗan zame kansa na bayan kujerar ya ɗora ƙafa kan ɗaya kamar yadda ya saba. Kallon sa take yi ganin yayi mata kyau gashin kansa ya kwanta kamar na jariri, idanunsa a rufe gashin idanunsa sun kwanta a ƙasan idanun.

"Omar Lafiya?" Ta faɗa tana zama daga gefen sa. Buɗe ido yayi ya ce, "Didi! Saukar yaushe?."

"Yanzu na shigo, baka da lafiya ne?."

"Ciwon kai ne yake damuna tun safe."

"Amma ka sha magani?."

"Na sha" ya faɗa yana sake lumshe idanunsa bai ce mata komai ba.

Didi kallonsa take yi tana haɗa kalaman da zatayi amfani dasu wajan sanar dashi abinda ya faru amma ta kasa, ta rasa ta ina zata kamo zaren, ta rasa da wacce kalma zata yi amfani wajan sanar dashi abinda yake zuciyarta akansa. Ajiyar zuciya tayi hakan ya saka ya buɗe ido ya kalleta ya ce "Lafiya dai?." Didi ta kalle shi sai taga idanunsa sun yi ja alamun yana jin ciwon kan sosai ta ce, "ciwon kan ne dai?." Ya ɗaga kai alamun eh.

Lumshe ido tayi ta sake buɗewa tana kallonsa ganin ita yake kallo, ya sauke ƙafa ɗaya ƙasa ya kalleta sosai ya ce, "kar ki damu da kaina na ciwo, ki faɗa min abinda yake faruwa. Naga kin canja alamun damuwa, meye?." Kai ta girgiza ta ce, "Babu komai Omar, Tambayar ka nake so nayi kawai."

"Akan son tambayata kawai kika koma haka?." Kallon sa tayi sai bata amsa ba ya ce, "Ina jinki."

"Omar na isa da kai? Na isa na zaɓa maka abu ka karɓa hannu biyu?." Wani irin kallo yake yi mata na me ya kawo wannan tambayar kafin ya ce, "me ya kawo wannan tambayar? Wani abun ya faru ne?."

"Babu abinda ya faru, ka amsa min tambayata."

"Akwai abinda ya faru, kawai bakya so ki faɗa min ne. Ni kuma Ina so na san meye abinda ya faru kafin na amsa miki."

"Kawai ka amsa min Omar."

"Me zan amsa?" Ya tambaya yana kallonta. Didi ta rausayar da kai ta ce, "na isa da kai? Na isa na zaɓa maka abu ka karɓa?."

Omar ya bita da kallo yana so ya gano dalilin tambayar amma bai gane ba, ya ɗan ɗauke ido yana kallon wani wajan daban kafin ya ce, "kin isa."

Didi ta ce, "Koda matar aure ce? Koda ɗauko mace nayi a yanzu nace maka na saka an ɗaura maka aure da ita zaka karɓa ta?." Omaar ya bita da kallon mamaki ganin ba da wasa take yi kamar yadda ta saba ba, sannan ya ga damuwa a kwance a fuskarta, sannan ya tabbatar da akwai abinda take so ta faɗa masa kafin wannan. Didi ta ce, "ka yi shiru kana kallona." Omar yayi ajiyar zuciya ya ce, "dalilin wannan tambayar nake so naji."

"Ni dai ka amsa min kawai" ta faɗa tana kallon sa. Shiru yayi na wani lokaci yana kallonta kafin ya ce, "eh to, kin isa ki zaɓa min ɗin tunda kece zai karɓa babu yadda zanyi. Amma kin san kin bani ita ne ba dan Inaso ba, kuma zama da wacce bana so bazata taɓa jin daɗin zama dani ba har abada. Kin fi kowa sanin halina, bana son ganin abinda ban saba gani a tare dani ba." Didi gabanta ya yanke ya faɗi tsoro ya mamaye mata zuciya ta ce, "amma zaka iya zama da ita a matsayin matarka dai ko? Babu tsawa, babu tsoratarwa, babu razani, babu harara ko?."

Gyara zama yayi ya shafa kansa zuwa gashin fuskarsa, ya ɗan sosa girar sa da yatsa ɗaya kana ya ce, "gaskiya bazan iya zama da ita matsayin mata ba, zan dai zauna da ita a gida ɗaya matsayin zaɓinki, amma gaskiya ba dai a matata ba."

Kallon sa take yi ta kasa magana dan ya kashe mata baki, ya katse shirun ya ce, "me ya kawo wannan maganar wai? Aure zaki yi min ne?." Jin yana ƙoƙarin gano ta sai ta girgiza kai ta ce, "Kusa hakan, bana son zaman ka kai kaɗai a gidan nan shine nake tunanin zaɓar maka mata na aura maka."

"Kar ki wahalar da kanki bana buƙata, bana so in kika yi ma zaki ɓata lokacin ki ne, ko wacece ita zaki ɓata mata lokaci da rayuwarta ne dan ni ban shirya aure ba. Gwara ki bari taje ta auri wani daban da dai ace ta aure ni, zaman aure da wacce babu ita a rayuwara tun farko babbar matsala ce. Na hutar dake, bance ina so ba, dan haka ki bar maganar nan."

"Baza ka iya kallonta a matsayin matarka ba saboda ni?".

"Haba Didi! Na faɗa miki ban so a bar maganar nan, in ma kina niyar yi ne kar ki yi na hutar dake bana buƙata, zama ni kaɗai baya damuna kinfi kowa sanin haka. Wacce mace zaki ɗauko ki kawota cikin rayuwata ba tare da sanina ba? Don Allah ki adana wannan tunanin, kar kuma kiyi wannan gangancin in ba haka ba zan ta ɓata miki rai, ki ƙyale ni!" Ya faɗa a kausashe yana kallonta dan ta katse batun shi ya gaji da wannan kalaman nata.

Ajiyar zuciya tayi ta rasa da wacce hanya zata yi masa magana ya fahimta, me zata ce masa ne wai? Ta ce masa mahaifin Nayla ya zo ya baka auren ta? To Akan wanne dalili ya aura masa ita? Meyasa yayi hakan?. Ganin ta tafi duniyar tunani sai taji ya murza yatsunsa a kusa da fuskarta sun bada sauti, ta kalle shi ya ce, "Ki faɗa min damuwar ki Didi!" Ya faɗa cikin kakkausar murya yana kallonta. Didi ta buɗe ido tana kallonsa ta ce, "babu komai na faɗa maka, zaman ka haka ne bana so, ya zama dole na nema maka matar aure koda baka so."

"Didi ki daina ƙoƙarin raina min hankali mana, na sanki na san halin ki kar ki manta da wannan. Wallahil azim akwai wani abu a zuciyarki, ki sanar dani damuwarki in kuma baza ki faɗa min ba kice baza ki faɗa ba." Didi ta kulle ido ta buɗe sai ta tashi tsaye ta ce, "Akwai abinda zan ɗauka a kitchen, na san ba amfani kake yi dashi ba

ni kuma ina so. Gwara na haɗa kayan na ajjiye kar na manta" ta faɗa tana shiga cikin kitchen ta barshi a wajan yana kallon ta cikin tunanin abinda yake damunta.

Da ta fito ya fita bata sake ganin sa ba, dan ɗaki ya shiga ya kwanta saboda ciwon kan da yake damun sa. Sai da magriba sannan ya fito yayi alwala ya same ta a tsaye a tsakar gida ta kalle shi ta ce, "zan shiga wajan Hajja." Kai ya ɗaga kawai tazo ta wuce shi.

Da sallama ta shiga gidan Hajja aka amsa mata, abinda ya bata mamaki bai wuce Nayla da ta gani a zaune ba tana yi mata oyoyo. Murmushi tayi ta zauna ta ce, "mutanen Kaduna, saukar yaushe?." Nayla ta ce, "saukar jiya, kuma gobe zan koma. Har gidan ki muka je ɗazu bakya nan." Jin hakan sai Didi ta bita da kallo da alama itama bata san da auren ba. To me hakan yake nufi wai? Meye dalilin Abiy na aurawa Nayla Omar ba tare da ta sani ba?.

Hajja ce ta katse mata tunani suka gaisa kafin ta kalli su Nayla ta ce, "naje gidan Kawu a can na yini sai yamma nazo nan, Meyasa baku yi min waya ba?."

"Muna ta kiran ki taƙi ta shiga shiyasa."

"Ayya, amma kun kyauta na so kun same ni." Nayla tayi murmushi ta ce, "zamu dawo wani lokacin."

Hira suka cigaba da yi da Hajja da kuma Salma dan ita dai Nayla tayi shiru bata magana. Didi ta taɓata ta ce, "Nayla ya dai?." Nayla tayi murmushi ta ce, "babu komai, anyi kiran sallah bara naje nayi sallah" ta faɗa tana shiga ciki duk suka bita da kallo.

Didi tausayi ma take bata wallahi, ko meyasa mahaifinta yanke hukuncin aura mata Omar oho, gashi da alama itama bata sani ba, meye amfanin yin hakan da yayi Allah ne ya sani. Duk tashi sukayi akayi sallah kafin Didi tayi musu sallama ta ce zata tafi, Nayla da Salma suka raka ta bar ƙofar gıda a nan suka ga motar AbdulHamid da alama ita yake jira.

Didi ta ce, "Don Allah kuzo ku taya ni ɗauko kayan a ciki, kayan kitchen ne wanda na san ba amfani dasu zai yi ba na tattaro kayana." Salma tayi dariya ta ce, "wallahi

gwara da kika ɗauko" ta faɗa suna bin bayanta zuwa gida. Ƙirjin Nayla bugawa yake yi sosai ba kamar da suka shiga tsakar gidan, Nayla ta ɗauki leda ɗaya Didi ta ɗauki biyu Salma ma ta ɗauki ɗaya.

Daga falon Omar ya fito sanye da ƙaramar riga mai gajeren hannu mara nauyi, sai wando three quarter. Kallon sa tayi ta ce, "Omar sai da safe."

"Ki kwana Lafiya" ya bata amsa yana niyar wucewa ba tare da ya kalleta ba.

"Ya ciwon kan?" Ta tamabaya tana kallon sa. Juyowa yayi ya kalleta ya ce, "naji sauƙi."

"Baka ga su Nayla da Salma ba? Baka yi musu magana ba."

Kallon su yayi, Nayla dai kanta yana ƙasa Salma ce ma take iya kallonsa kamar zai yi magana sai ya fasa, ya ɗaga ƙafa da niyar barin wajan sai ya juyo ya kalli Didi ya ce, "na rasa meyasa kike son saka ni a abinda bai shafe ni ba" yana gama faɗa ya wuce ya barta a wajan.

Wani iri taji a zuciyarta, dan ita ta san yanzu Nayla matarsa ce shida ita ne basu sani ba, hakan da yayi ya tabbatar mata da karɓar Nayla zai yi masa matuƙar wahala, duk ganin da yake mata gashi bai saba da ita ba. Ita ta ɗauka ya saba da ita har zai iya yi mata magana, tunda shi magana da wanda bai saba ba babban tashin hankali ne a wajan sa.

Didi ta kalli Nayla bata ce komai ba sai Salma da tayi dariya ta ce, "Kema Didi ban da abin ki ina Omar inayi mana magana? Mu je" ta faɗa tana yin gaba duk suka bi bayanta Nayla dai kanzil bata ce ba.

Har motar suka saka mata kayan tayi musu godiya suka gaisa da mijinta sannan suka wuce gidan Hajja. Tunda ta shiga motar shima ya lura tana cikin damuwa mai yawa, ya kalle ta cike da kulawa ya ce, "Ya dai? Akwai abinda ya faru ne?." Didi ta ce, "Akwai wallahi. Kaga yarinyar nan da kuka gaisa mai blue ɗin mayafi?."

"Eh na ganta."

"Itace Nayla, itace wacce ta yi silar da aka fito da Omar daga wajan Senator. Ɗazu mahaifinta yaje har gidan Kawu ya saka aka ɗaura aurenta da Omar."

AbdulHamid ya ce, "Iyee! aure da Omar kuma!?." Didi ta ɗaga kai ta ce, "wallahi, yanzu maganar da nake maka ita matar Omar ce wallahi."

"Ikon Allah, to garin ya haka ta faru?. Daman suna soyayya da Omar ɗin ne?." Didi ta ce, "ita dai tana son Omar, na ji da kunnena suna tattauanwa a ranar ɗaurin aurena da kai. Ta bani matuƙar tausayi, domin soyayya bata yi mata adalci ba da ta saka ta fara son Omar. Ita ba tsararsa bace, ta wuce ajinsa nesa ba kusa ba, ko masu gadin gidansu sun fi Omar matsayi wallahi. Abinda ya bani mamaki ya kuma ɗaure min kai shine; mata guda biyu kyawawa, masu asali da iyaye masu kuɗi da faɗa a ji a ƙasar nan, mata masu ilimi, aji da wayewa sune suke yiwa Oamar irin wannan soyayayar? Anya ta baki Senator ba asiri Omar yake yi musu ba kuwa?."

Abdul yayi dariya ya ce, "Wanne irin asiri ana zaune Lafiya? Kawai haɗuwar jini ce. Kin san mata suna son farin namiji kyakykyawa mai saje kamar Omar ɗin."

"Amma haɗuwar jinin su rasa da wasu haɗa jini sai Omar? Mata kamar su ace sune suke sonsa ba shine yake sonsu ba?. Har gwara Narma ita ya furta min yana so, to Nayla fa da take matsayin matarsa yanzu?."

"Ni maganar auren ce ta ɗaure min kai, haka kawai mahaifinta ya aura masa ita kamar auren ɣar tsana?."

"Wallahi nima ya ɗaure min kai, abin mamakin kuma a yanayin yarinyar na tabbatar da bata san da auren ba kamar yadda Omar bai sani ba. Meyasa mahaifinta ya aura masa ita?."

"Ko ya gano tana sonsa ne?."

"Dan ya gane tana sonsa kuma sai ya ɗaura mata aure dashi yau kwatsam? Gaskiya akwai lauje a cikin naɗi a lamarin nan." AbdulHamid ya ce, "yanzu shi Omar ɗin ya sani?."

"Waye zai faɗa masa? Kaf duniya ni kaɗai ce zan iya tunkararsa da wannan maganar, to nima ɗin na rasa ta wacce hanya zan faɗa masa. Jurwaye mai kamar wanka nayi masa, nace masa na kai matsayin na bashi mata ya zauna da ita, ka san me ya ce?."

Ya girgiza kai alamun a'a Didi ta ce, "cewa yayi zai iya karɓa tunda ni ce babu yadda zai yi, amma bazai iya kallonta matsayin mata ba, zai dai zauna da ita gida ɗaya matsayin wacce na ajjiye masa amma ba matarsa ba." Abdulhamid yayi dariya ya ce, "Wallahi Omar yana burge ni, yanayin ƙarfin guiwarsa da gaskiyarsa tana matuƙar burge ni a halayensa. Yanzu ya zaki yi?."

Cike da damuwa ta ce, "Dole dai ni zan faɗa masa, amma nima ban san ta wacce hanya ba."

"Zaki samo hanya, ki nutsu kawai, ai yana jin maganarki zai yi duk abinda kika ce masa." Didi ta ce, "hmm baka san Omar ba ne, a dai yi shiru kawai" ta faɗa tana kawar da kai zuciyarta cike da tunanin dalilin auren Nayla da Omar lokaci guda haka.

KRB2P022

Narma tana tsaye a tsakiyar bedroom ta idar da sallah tana ninke sallaya Ashraf shiga yana binta da kallo. In ba da sexy dress ya ganta ba bata burge shi gabaɗaya, yana so ya ganta da kayan da suka bayyanar da surar ta, in ya same ta da hijjabi ko riga mai girma sai yaji haushi ya tokare masa ƙirji lokaci ɗaya sai yaji tana bashi haushi, amma da zarar ya ganta a yadda yake so sai yaji babu abinda yake so sama da kasancewarsa da ita.

Jin motsinsa sai ta kalle shi tana zare hijjabin daga jikinta, ajiyar zuciya ya yi ganin rigar jikinta wacce tayi daidai da yadda yake so ya ganta. Iyakar rigar guiwa tana da hannu mai ɗan girma kaɗan amma bata da kauri sannan tana bin jiki. Zama tayi a gefen gado tana kawar da kai dan tun lokacin da ya same ta sau ɗaya bata sake bari hakan ya faru ba.

Murmushi yayi ya ce, “My Love zamu iya fita?.” Kallonsa tayi ta girgiza kai alamun a’a ya ce, “Haba my love, ki amince muje ba jimawa zamu yi ba dawo. Kullum kina gıda, tunda muka zo bakya fita.” Bata ce masa komai ba yazo kusa da ita ya zauna yana ƙare mata kallo, halittarta na burge shi sosai, amma yanzu abinda yake ji a kanta ya ragu da kaso mai yawa, kawai ya san yana son kasancewa da ita bayan wannan babu wani abu a zuciyarsa a kanta.

A hankali ya kai hannu ya fara shafata ya ce, “My love muje mu dawo. Ko kina so mu taje miami mu kalli ball ɗin messi?.”

“Pls Ashraf ka ƙyaleni, babu inda zanje in kai zaka je kaje amma ka daina saka ni ciki” ta faɗa tana kawar da kanta gefe.

“Come on my love” ya faɗa yana yajowata jikinsa lokaci ɗaya yana ƙoƙarin zare rigar jikinta. Da hanzari ta fincike jikinta ta miƙe tsaye ta ce, “kar ka sake wannan kuskuren, wancan ka damu dama a banza a yanzu baza ka samu ba. Ka tashi ka fita ka bani waje bana son ganinka, wallahi na tsaneka, ka fahimi bana so ganin koda fuskar ka ne.”

Kallon ta yake yi jin wai ta tsane shi ya ɗan buɗe idanu tare da taɓe baki ya miƙe shima yana kallonta ya ce, “kin tsane ni kika ce?.”

“Eh natsane ka, bana son ganinka ko kaɗan.”

“Wannan mahaukacin yaron kike so?.” Ba tare da shakka ba tace, “eh shi nake so, ganganar jikina kawai kake tare da ita a nan amma zuciyata tashi ce. In ka sake kuskuren zuwa kusa dani zanyi maka illa babba a jikinka.”

“Wow! Daman ni ai ganganar jikin naki nake da buƙata ba zuciyarki ba Narma. Jikinki nake so kuma na riga na mallaka, ko yanzu nace Ina son wani abu a tare dake baki isa ki hana ni ba. Dan yana riƙe da zuciyarki Ina riƙe da jikinki hakan yayi min daidai. Da ki soni, da kar ki soni ni dai ina son jikinki.” Narma ta bishi da kallo kamar zata yi magana sai ta fasa ta koma gefe ta harɗe hannaye a ƙirji bata ce komai ba.

Ashraf ya ce, “this is the last time da zaki sake yi min maganar sa a nan, ni mijinki ne ko bakya so, in kika sake ambatar wancan shashashan mara hankalin a gabana ranki zai ɓaci matuƙa.” Hararsa tayi ta ce, “Sai na faɗa baka isa ka hana ni ba, kuma kaine shashasha mara hankali amma ba shi ba. I love Faruk! I love him!i love him!! I love him!. In kaga dama ka kashe ni kar ka barni da rai” ta faɗa tana hararsa cike da jin haushi da tsana.

A firgice ya tako inda take ya na zare mata idanu ya ce, “ni kike kira da mara hankali Narma?.”

“Eh na faɗa, baka da hankali…..”bata ƙarasa ba ya ɗauketa da mari mai zafi yana huci. Sai da ta gigice jin zafin marin da yayi mata, in tace tunda take Dad ne kawai ya taɓa dukanta lokacin da Omar yaje gidan su bata yi ƙarya ba, amma kafin nan iyayenta basu taɓa marin ta ba tunda tazo duniya, zata iya cewa babu wanda ya

taɓa marinta a duniya bayan Dad sai shi. Nan da nan idanunta suka yi ja ta kalle shi ta ce, “ni ka mara Ashraf?.”

“Na mare ki, in ki ka sake furta maganar da kika furta wallahi sai na yi miki dukan tsiya a wajan nan.”

“Ni Narma ni ka mara?” Ta amsa faɗa tana kallon sa. Ta ɗaga hannu zata rama ya riƙe hannun tare da murɗa shi baya, tayi ƙara mai sauti tana runtse ido.

Ashraf ya ce, “lallai baki da hankali, ni zaki daka?.” Narma ta ce, “to ka sake ni, bana son aurenka, ka sake ni na koma gida bana sonka.”

“Nima bana sonki amma bazan sake ki ba, zama dake nake so yi ko dan na mallaki jikinki a duk lokacin da nake so” ya faɗa yana jawowa jikinsa da ƙarfi ya fara kissing ɗinta da zafi-zafi cike da mugunta. Da faɗa da dambe da Asharaf ya samu yaje inda yake so yaje a jikin Narma, tun tana fizge-fizge har ta daina ta koma zubar da hawaye cikin ƙunar rai da kuma ƙunar zuciya.

Shi kam Ashraf ko a jikinsa, abinda yake so a tare da ita ya samu yana barin wajan yaji gabaɗaya haushinta yake ji, abinda yake ji a zuciyarsa gabaɗaya ya kau, indai yana jin shauƙi akanta to tabbatar akwai abinda yake buƙata a tare da ita, da zarar wannan buƙata ta gushe shikenan sai yaji ta fita daga ransa gabaɗaya komai tayi baya burge shi. Kallonta ya yi tana kuka yaja tsaki ya fita ya barta a wajan bai ko sake kallon ta ba.

Narma daƙyar ta iya miƙewa ta shiga banɗaki tayi wanka ta fito da zazaaɓi da ciwon kai. Hannu na rawa tasha shan pracetamol sannan ta ɗauki waya hannunta na karkarwa tana neman ticket na Nigeria dan baza ta sake kwana a America ba, gida zata koma duk abinda zai faru sai dai ya faru amma ta gaji.

•••••••••

Nayla ta shirya tana jiran Baba Salisu yazo su tafi tana zaune a falon Hajja, gabaɗaya jikinta babu daɗi ji take kamar tayi ihu bata san dalilin faruwar hakan ba. Hajja ta kalleta ta ce, “gashi ba a siyawa Abban naki gurasa ba, ko zaki jira?.”

“Hajja ki ƙyale shi kawai, ai duk zuwa kina siya masa wannan dan ba a siya ai ba komai.”

Hajja tayi shiru bata ce komai ba amma zuciyar ta bata yi mata daɗi in taga Nayla a wannan yanayi na damuwa. Babu abinda zata iya, ta tambayeta tace babu komai amma ba dan ta amince ba. Tana zaune ba jimawa Baba Salisu ya ƙaraso kamar ko yaushe ta kai masa ruwa ya sha yace ba sai ya huta ba tazo kawai su wuce. Sallama ta yiwa Hajja da Salma ta shiga motar suka tafi gabanta yan faɗuwa bata san dalilin hakan ba.

Tafiyar awa uku ta kai su garin Kaduna har cikin gidan su Nayla. Yana faka motar ta fito tare da jakar kayanta zuwa cikin gidan. Faɗuwa gabanta yake yi abinda bata taɓa ji ba in ta dawo daga Kano, ta saba tana jin zumuɗin ganin yan gidan amma yau ta rasa meyasa take ji haka.

Da sallama ta shiga babban falon Mama ce kawai sai Jalila suka amsa mata ta ƙaraso ta ce, “Mama na dawo.” Mama ta bita da kallo ta ce, “sannu da zuwa, na ɗauka sai gobe.”

“Yaya J ne ya kira ni yana ta faɗa ya ce lallai na dawo yau.”

Gaisawa suka yi da Mama Jalila ta kalle ta ta ce, “Ashe Abiy bai san kin tafi Kano ba? Bayan kin tafi ya dinga faɗa.” Nayla tayi ajiyar zuciya ta ce, “na dawo na bashi haƙuri” abinda tace kenan ta miƙe ta wuce zuwa ciki. Sai da tayi wanka tare da yin sallar azahar, tana idar da sallar Jawad ya shigo ɗakin nata abinda bai saba ba. Da kallo ta bishi ta miƙe tsaye ta ce, “Yaya J Ina yini.”

Harara ya sakar mata ya ce, “Nayla ashe baki da hankali ban sani ba? Ashe ilimin ki bashi da amfani?.” Nayla ta sunkuyar da kai duk a tunanin ta akan son da ta ce tana yiwa Omar yake wannan maganar.

“Yanzu Nayla sai ki saka ƙafa ki bar Kaduna ba tare da sanin Abiy ba? Guduwa kike son yi saboda an hana ki auren ɗan daba ko?.”

Ta girgiza kai ta ce, “ba guduwa nayi ba Yaya J, kuma Mama…” dakatar da ita yayi ya ce, “Mama me? Me maman tayi?. Kin bani mamaki wallahi, kin kuma cuci kanki,

kin cuci rayuwarki, in kai kanki inda zaki sha wahala. Ba dai kin zaɓi ɗan daba akan mahaifinki ba? Kin zaɓi ɗan daba akan mu, kin zaɓi ɗan daba akan iyalan gidan nan gabaɗaya ko?. Shikenan gaki gashi nan sai ki je ki kwaɗa soyayya ki cinye, banza mara hankali!" ya faɗa yana hararta cike da ɓacim rai.

Gaban Nayla ta faɗi tana tunanin yaushe ta zaɓi Omar akan su kuma?. Bata damu da faɗan da yake mata ba duk da karo na farko kenan a rayuwarta, ta kalle shi ta ce, "Wallahi Yaya J ni ban zaɓe shi na barku ba, taya zan zaɓe shi na bar ku?. Ni na haƙura ma fa, na haƙura bazan sake maganar ba in sha Allah."

"Ko kiyi min shiru ko na buge miki baki, haƙurar taki me zata hana faruwarsa yanzu kuma? Ai aikin gama ya riga da ya gama. Tunda haka ki ka zaɓa gaki ga shi nan ai" ya faɗa yana fita daga ɗakin nata.

Jikin ta gabaɗaya ya gama yin sanyi, dana sanin tafiya Kano ya mamaye mata zuciya. Amma Mama ce tace ta tafi ta ɗauka zata yiwa Abiy bayani in ya tambaya. Da wannan sanyi jikin ta fito falo. Gabanta ya faɗi da ta hango Abiy a zaune yana cin abinci, ga Yaya, ga Yaya J, ga Mama, da kuma Jalila. A hankali take takowa zuwa tsakiyar falon ta zauna akan carpet ta ce, "Abiy Ina yini."

Kallonta yayi yana tuna irin abinda ta sake turo masa cikin wayar, ya kasa yarda Nayla yar cikinsa zata iya aikata abinda ta aikata masa akan soyayya, har tana cewa ta zaɓi ta zauna dashi akan shi da ya haifeta. Zafin kalaman yake ji a zuciyarsa sosai, hakan ya saka ya kafa mata ido ba tare da ya sani ba. Sai daga baya ya ɗauke idanunsa ya ce, "Har kin gaji da zaman Kanon?." Nayla ta ce, "Daman ba zama zanyi a can ba."

"Zaman can ya kama ki kam yanzu" ya faɗa yana cigaba da cin abinci.

Shiru falon yayi bai ce mata komai ba itama bata ce ba, sai daga baya ya ce, "naga saƙonki, hala dai ke kika rubuta ko?." Nayla ta ɗaga kai ta ce, "ni ce Abiy. Ka yi haƙuri in na ɓata maka rai." Girgiza kai yayi ya ce, "ɓata min ran me zaka yi Nayla? ke ki ka zaɓi abinda kike so, kuma abinda yake zuciyarki kika faɗa min, Meye zai bata min rai a kalaman ki?. Ai haka ki ka zaɓa ko?" Ya faɗa yana kallonta.

Nayla ta ɗaga kai a sanyaye ta ce, "haka na zaɓa Abiy, kayi haƙuri" ta faɗa kai tsaye tana sunkuyar da kai. Abiy ya girgiza kai cikin tsananin jin zafin amsar da ta

bashi, ya kalle ta zai sake magana sai ya fasa saboda abinda yake ji a cikin zuciyarsa game da ita.

Shiru yayi na wani lokaci yana sarrafa zuciyarsa sannan ya ce, “shikenan tunda haka ki ka zaɓa ai aikin gama ya gama. Ga Maman ki nan, kuje kasuwa tare duk abinda ya kamata a siyawa amarya ki siya, ki zaɓi abinda kike so dan iya yau kawai kike de ita, Gobe zaki tare a gidan mijin ki!.” Wani irin yarrrr Nayla taji jin kalaman Abiy da kuma kalmar mijinta da ya faɗa, ta ɗago ta kalle shi idonta ya ciki da hawaye, Abiy ya ɗauke kai daga kallon ta.

Mijinta? Wanne irin mijinta kuma ake zance?. Ko dai Abiy ya zaɓa mata miji a cikin masu neman aurenta ne kamar yadda ya ce?. Abiy ya katseta ya ce, “ki tashi kije kasuwa.” Mama ta ce, “Abiy siyayya bazata yu a iya yau ba, don Allah ka janye kalaman ka mu zauna a tattauna tukunna. Wannan wanne irin hukunci ne lokaci ɗaya?.” Ya kalli Mama ya ce, “bazan lamunci matar aure ta cigaba da zama a gidana da auren wani a kanta ba.”

“Amma Abiy abin yayi kusa, ko sanar da ita ba a yi ba, bata san abinda ya faru ba ka dinga zancen tariya gobe? Wacce irin tariya ce wannan? Wanne irin aure ne wannan?. Babu wanda ya san an yi a dangi, kuma kawai sai a ɗauketa akai Kano?.”

Abiy ya ce, “Haka nayi niya haka kuma nayi ra’ayi, ita ta zaɓi mijin ita zata zauna dashi ba mutane ba, dan haka ban ga amfanin sanar da mutane biki ko wani abun ba. Taje ta zauna da zaɓinta shine kawai.” Mama ta ce, “amma iya yau ya yi kaɗan a siyayya, ko dan siyayyar ka ƙara mana lokaci don Allah.” Bai ce komai ba yaja kujerar dining ɗin da yake kai yayi baya ya tashi ya hau shiga ɗaki bai sake kallon kowa a cikin su ba.

Nayla dai ta daskare a wajan, wai me hakan yake nufi kenan? Kayan ɗakin wa Abiy yake nufi za a siyo?. Muryar Yaya taji a bayanta ya finciki hannunta ta miƙe tsaye ya ce, “kin cuci rayuwarki, kin lalata rayuwarki, kin ɓata rayuwarki Nayla. Abinda ki ka yi ba kowa kika cuta ba sai kanki, na tabbatar Umma da take kwance a kabari baza tayi alfahari dake akan abinda kike aikata ba.”

Nayla da take a firgice ta ce, “Yaya me ya faru? Me na aikata haka?.” A fusace ya ce, “au baki san abinda ya faru ba? Na ce baki ana abinda kika aikata ba ko!?.” Nayla tana hawaye ta ce, “ban sani ba, wallahi ban sani ba. Ku sanar dani abinda na aikata don girman Allah.”

Yaya ya ɗauketa da mari cike da baƙin cikin da yake ji a zuciyarsa, Nayla ta fashe da kuka mai sauti, ya ce, “in kika sake furta baki sani ba wallahi sai fasa miki baki, ba dai kin zaɓi ɗan daba akan mu ba? Kin yi daidai ai Nayla. Kin ji daɗi kin fusata zuciyar mahaifinmu, to wallahi bara kiji, duk abinda ya faru a tsakaninki dashi kar ki nemi kowa ki yi kuka da kanki, tunda har kin iya tattara kaya ki bar gida saboda ke ga yar soyayya ko?.”

Nayla ta kalli Mama tana kuka ta ce, “Mama me nayi? Mama me na aikata ne haka?. Me su Yaya suke faɗa wanda bana fahimta ba?.” Mama ta bita da harara ta ce, “Nayla kinfi kowa sanin abinda kika yi, kin aikata abinda ya saka ran mahaifinki ɓaci, kin kuma san Abiy bai iya ɓacin rai ba. Sai kije ki shirya kizo mu je ki zaɓi abinda zaki zaɓa, kina ji ya ce gobe ne tarewarki.”

“Tarewata, tarewata kuma Mama? Tare ta a ina kenan?” Ta faɗa cikin fitar hankali tana kallon Mama. Jawad ya ce, “a gidan wanda kika zaɓa mana Nayla, a gidan wanda kika ce shine rayuwarki. Yanzu maganar da nake miki ke matar Omar ɗan daba ce, Abiy yaje har Kano da kansa ya ɗaura miki aure dashi tunda abinda kike so kenan” yana faɗa yaja tsaki ya bar falon, Yaya ma ya fita dan in ya cigaba da zama da Nayla sai ya ɓalla ta.

Wani irin yuuuu Nayla take ji a tsakiyar kanta kamar zata kifa, jiri ne yake ɗaukarta daga tsaye hakan ya saka ta saurin zama ta dafe kai da hannayenta duka biyu, kalaman Jawad suna yi mata amsa kuwa a cikin kunne ta. Aure fa ya ce, an ɗaura auren mata da Omar, abinda taji daidai ne ko kuma dai ba daidai bane, da gaske ne ko wasa yake yi mata?. Sai kuma ta firgita ta kalli Mama ta ce, “Mama da gaske abinda Ya J ya faɗa? Da gaske ne wai ko mafarki nake yi.”

“Da gaske ne, yanzu ke matar Omaar ce Nayla. Jiya mahaifinki yaje Kano ya ɗaura miki aure dashi.” Baya tayi zata kifa Allah ya taimaka ta dafa kujera. “Innalillahi wa’inna ilahir raji’un! Innalillahi wa’inna ilaihir raji’un! Mama meyasa Abiy yayi haka? Meyasa?. Mama dan na tafi Kano? Mama ba ke kika ce min na tafi Kano ba?” Ta faɗa a gigice tana kallonta.

Mama ta ce, “ba a kan zuwan ki Kano yake magana ba, bai yanke wannan hukuncin dan kinje Kano ba Nayla, yana da dalili mai ƙarfi wanda ni ban san dashi ba.” A guje Nayla ta nufi apartment ɗin Abiy dan yadda take jin zuciyarta kamar zata fito dole tayi magana dashi. Mama ta rufa mata baya zuwa ɗakin ta same ta a lokacin da take shiga ta zube akan tiles a gabansa.

“Abiy! Abiy don Allah, don Allah Abiy!” Abinda yake furtawa kenan ta haɗe hannayenta waje ɗaya tana kuka sosai. Abiy da ya kalle ta sai ya miƙe ya ɗauko sadakinta ya buɗe hannayenta da ta haɗe waje ɗaya ya saka mata ya ce, “Sadakin ki na auren masoyinki, kije ki fara shiri gobe zaki tare a gidan sa.” Jin kalaman take yi tamkar saukar aradu, ta saki kuɗin a ƙasa ta riƙe hannun Abiy ta ce, “Abiy don Allah kace wasa kake yi min, Abiy dan na je Kano ka yanke min wannan hukuncin?. Mama…Mam….tasan zan je Kano…” ta juya tana kallon Mama ta ce, “Mama…baki san zanje Kano ba? Ba ke kika ce min na je Kano ba?. Meyasa ki baki faɗawa Abiy ba har ya yi fushi da ni?.”

Mam ta ce, “ni nace ki je Kano Nayla? Yaushe mu ka yi haka dake?. Ke kin san ban taɓa baki umarnin zuwa Kano ba, Abiy ne yake yanke hukuncin lokacin da zaki je da lokacin da zaki dawo, ni na taɓa cewa tafi Kano ki dawo rana kaza Nayla?. Ban taɓa ba, kawai kin shiga ruɗani ne kike tunanin nace miki kije amma bamu yi haka dake ba.” Nayla sakin baki tayi tana kallon Mama jin kalaman da take faɗa ta ce, “Mama ta ya zan shiga ruɗani akan wannan? Wallahi….” Cikin tsawa Abiy ya ce, “Nayla ki tashi ki bar min ɗaki! kije can ki zauna da wanda kika zaɓa, mu da zaki iya barin mu saboda shi ki barmu kije kiyi zaman ki dashi tunda shine zaɓinki. Ki tashi ki fita kafin na saɓa miki!.”

Nayla kuka take yi kamar ranta zai fita magana take so tayi amma ta kasa bakin ta rawa yake yi sosai, jikinta rawa yake yi cikin tashin hankali. Maganar ta maƙale ta kasa furta komai, so take ta kare kanta a wajan Abiy amma ta kasa sai rawar jiki da rawar baki. Abiy kukan ta yake ji har zuciyarsa, baya so ya bata wata gaɓa da zai ji tausayinta, hakan ya saka ya ce, “ki fita na ce!” Jin yadda yayi maganar bata san ta miƙe ba sai ganin ta tayi a bakin ƙofar ɗakin jiki na rawa.

KRB2P023

ArewaBooks@nanahaleema11

Nayla tana fita daga ɗakin Abiy Mama ta ƙarasa wajansa ta ce, "kayi haƙuri ka sassauta wannan ɓacin ran don Allah. Nayla bata kyauta ba na sani, abinda tayi sam bai kamata ba, taci amanar kauna da soyayyar da ka nuna mata, na tabbatar ko mahaifiyarta da take kabari baza taji daɗin wannan abun da Nayla tayi ba. Da me aka rageta dashi a gidan nan? Da ci ko sha ko suttura?Amma ta rasa da abinda zata saka maka sai wannan abun?. Na san dole zaka ji babu daɗi a zuciyarka, amma ka yi haƙuri ka kwantar da hankalin ka komai zai wuce in sha Allah."

Kalaman Mama sake hura wutar ɓacin rai suke yi a zuciyar Abiy, gasgata maganarta yake yi dan tabbas Nayla bata yi masa halacci ba, tunda mahaifiyarta ta rasu bai taɓa bari tayi kukan rashin uwa ba amma da haka zata yi masa sakayya. Tabbas bata kyauta masa ba, ta cutar dashi ta kuma cutar da rayuwarta.

Haka Mama ta dinga lallaɓa Abiy da kalamai masu kwantar da hankali tare da kai suka ga abinda zai saka ya sake yin fushi da Nayla. A haka ta samu ya ɗan sauka ya ce ta bashi waje bacci zai yi ta fito daga ɗakin.

Nayla kuwa lokacin da ta fita daga ɗakin daƙyar ta iya ƙarasawa dakinta tana kuka mai tsuma zuciya. Ta jima tana wannan kukan babu mai rarrashinta, babu mai bata shawara, babu mai faɗa mata laifin da ta aikata. Tun tana kukan cikin daɗin rai har kanta yayi bala'in yin nauyi, zuciyarta kam kamar dutse haka take ji saboda nauyi. Lokaci ɗaya take ji kamar ana zare mata son Omaar ɗin daga zuciyarta, bata sani ba ko dan bata nutsuwar ta ne, amma gabaɗaya ya fita daga ranta cikin ƙaramin lokaci.

"Aure fa, aure fa da Omaar Abiy yayi min. To meye dalilin hakan? Me na aikata masa ya yanke wannan hukuncin a kaina?. Wa zan tambaya ya bani amsa?" Ta faɗa hawaye na ganganarowa daga idanunta.

Sautin buɗe ƙofa taji ta juya taga Mama ce ta shigo ta ƙaraso inda take ta miƙa mata kuɗin ta ce, "yace na tabbatar na baki sadakin auren ki, sannan ki bani number Yayar Omaar ɗin Ina so zan tambaye ta a gidan da zasu ajjiye ki. Na saka za a kawo kaya gobe ban sani ba ko zasu burge ki, kawai na zaɓa ne saboda babu lokaci."

Nayla ta bi kuɗin da kallo ta miƙe tsaye tana kallon Mama ta ce, "Mama me na yiwa Abiy ya yanke min wannan hukuncin?."

"Nayla nima ban sani ba, abinda na sani ya dawo jiya ya ce min ya aurar dake ga Omar. To me zan ce masa? Shine ya haife ki Ina da magana akan haka ne?."

Nayla ta ce, "Mama amma ke kika ce naje Kano ko? Meyasa baki faɗawa Abiy ke kika tura ni ba?."

"Na tura ki Kano dan a samu mafita ki auri wanda kike so ne ba dan ran mahaifinki ya ɓaci ba, abinda na lura ba zuwan ki Kano ne ya ɓata masa rai ba, akwai wani abun a ƙasa da ya saka ransa ya ɓaci." Nayla ta dafe kai ta koma da baya ta zauna ta ce, "me na yiwa Abiy haka? Bai taɓa fushi dani kamar yau ba, me na aikata masa ni Hauwa?" Ta faɗa cikin rawar jiki dan zazzaɓi ne yake neman kamata.

Mama ta ɗauki wayar Nayla ta buɗe ta nemo number Didi ta ɗauka a tata wayar sannan ta ajjiye mata wayar kana ya ce, "to wai meye na wannan koke-koken? Naga burinki ne na son auren Omar ya tabbata ko? To meye na kukan ke da ya kamata ace kina farin ciki?."

"Mama Abiy fushi yake yi dani, kuma ni ba ta wannan hanyar nake son samun farin cikin ba. Meye abin farin ciki bayan mahaifina ransa yana "ɓace? Meye abin farin ciki bayan kowa haushina yake ji?. Ban san me na aikata ba, ban san me nayi ba!."

"Aikin gama ai ya riga ya gama Nayla, yanzu ke matar Omar ɗan daba ce, akwai igiyoyin aurensa guda uku chas akan ki. Dan haka kawai ki yi tawakalli ki karɓi ƙaddara komai zai warware."

Wani haushin Mama taji a zuciyarta abinda bata taɓa ji a zuciyarta ba, ta kawar da kai gefe Mama ta fita daga ɗakin ita kuma ta cigaba da aikin tunani. Ko Twiny da Salma ta kasa faɗawa, gani take wannan ba abinda za a faɗa bane gwara kawai taja bakin ta tayi shiru.

Washe gari Ranar Sunday da safe Mama ta siyi kaya aka kawo aka dinga shigo da kwalaye na gado da kujeru. Nayla na sama ta kasa fitowa saboda zazzaɓi da ya

rufeta ga azabar ciwon da kanta yake yi. Jalila ce ta shiga ɗakin ganin yadda take ya saka ta fito da sauri ta samu Abiy da Yaya Jawad a tsaye fitowar Abiy ɗin kenan ta ce, "Abiy Anty Nayla bata da lafiya." Abiy ya nufi ɗakin shida Jawad, ganin yadda Nayla take rawar jiki Abiy ya matsa kusa da ita ya taɓa goshin ta yaji yadda yayi zafi sosai.

Jawad ya kalla ya ce, "kira Dr yazo ya duba ta, ka faɗa masa zazaabi ne da ciwon kai kuma kuka ne ya kawo shi. Sai ya san da abinda zai zo." Jawad ya amsa yana kallon Nayla nan take sai ta bashi tausayi, yaji tausayinta ya maamaye masa zuciya. A kasalance ya ɗauki waya ya kira Dr aka yi sa'a yana kusa ya ce gashi nan zuwa. Suna zaune a ɗakin har Yaya ya shigo da Jalila da Mama, Dr yayi waya ya ce gashi yazo Jawad yaje ya shigo dashi.

Ƙarasowa ya yi suka gaisa da mutanen ɗakim kafin ya taɓa jikin Nayla. Jin zafin sai da ya tsorata shima, ya haɗa allura yayi mata ganin yadda take ta juya kai alamun ciwon kan yake mata sai ya saka mata har da ruwa. Kallon Abiy yayi ya ce, "in ta farka taci abinci ta sha wannan maganin, in sha Allah zata dawo daidai." Abiy ya karɓi maganin yayi masa godiya ya fita.

Nayla ta kalli Abiy da yake kallonta cikin jajayen idanunta ta ce, "Abiy kayi haƙuri, kayi haƙuri Abiy. Na fasa aurensa, na amince ka aura min wanda kake so."

Tausayi ta bawa Abiy amma har lokacin bai yi dana sanin abinda yayi mata ba, dan shi kaɗai ya san abinda ta turo masa da kalaman da ta furta akan Omar, auren shine daidai ko a wajan Allah bashi da laifi. Jawad ya ƙaraso ya riƙe hannunta ya ce, "ki nutsu ki samu bacci, ki daina magana."

Cikin rauni ta ce, "Yaya J Abiy fushi yake dani, ban san me nayi masa ba. Ka bashi haƙuri kar na mutu yana fushi dani, kuma ku yi hakuri,

Yaya ka yi haƙuri" ta faɗa tana kallonsa da yake tsaye. Shi kansa ta bashi tausayi sosai ya daure ya ce, "ki daina magana kinji Nayla, ki yi bacci." A hankali idanunta ya fara rufewa hannunta na cikin na Jawad har tayi bacci.

Tare suka fito falon gabaɗaya suka samu Mama tana waya Abiy ya wuce ta su kuma suka tsaya suna so ta gama wayar. Tana yanke wayar Jawad ya ce, "Mama wai wanne kaya ne haka ake ta shigowa dasu?."

"Kayan auren Nayla mana, baka ji mai mahaifinku ya ce ba?." Jawad ya ce, "Amma Mama sai na ga kamar murna ma kike yi da auren nan. Gabaɗaya hankalinki yana kan siyan kaya gata can a kwance babu lafiya." Mama ta ce, "umarnin mahaifinku na ke cikawa, shi ya ce na tabbatar yau an siyi komai dole na mayar da hankali." Yaya ya ce, "Amma ko shi Abiy a yanzu bazai saurare maganar kaya ba, don Allah ki bar maganar nan ki bari ta samu lafiya tukunna."

Mama bata ce komai ba ta wuce ɗaki ta nemo number Didi da ta ɗauka a wayar Nayla ta kira. Bata jima tana ringing ba aka ɗauki wayar, da sallama Mama ta amsa ta ce, "Ina magana da Aisha ne?." Didi ta ce, "itace."

"Nice Maman Nayla, daaga nan Kaduna."

"Lah Mama, barka da safiya" ta sake jaddada gaisuwarta saboda girmamawa. Mama ta sake amsawa kafin ta ce, "Mahaifin Nayla ya saka na kiraki, yace na tambaye a ina za a ajjiye kayan Nayla na aure?." Sai da gaban Didi ya faɗi, ta ɗan yi shiru kafin ta ce, "Wallahi Mama bana ce ba, ni gabaɗaya a rikice nake da wannan lamari na rasa abinda zanyi."

Mama ta ce, "mu ma nan duk a haka muke, amma ya zama dole na tambaya saboda ya saka a siyi kayan ɗaki. Ya ce da a yau ma zata taho Kano, to saboda rashin kayan ne zai saka a ɗaga." Didi ta ce, "To Mama zan tambaya naji."

"Yauwa ki tamabaya, ki faɗa min adadin ɗakukanan, in ɗaya ne to, in biyu ne ma dai duk daya. Bana so ya sake tambayata nace ban yi ba."

"In sha Allah Mama zaki ji ni."

"Yauwa na gode" ta faɗa tana yanke wayar. Sai kuma tayi dariya ta ce, "to kayan ɗakin ma suka wuce ɗaki daya ko biyu? Ina yake da wajan da za a ajjiye kaya na alfarma? Me ya ke dashi me ya tara?. Tunda dai an ɗaura auren ni burina ya gama cika wallahi" ta faɗa tana ajjiye wayar tare da shiga toilet.

••••

Didi lokacin da ta yanke wayar ajiyar zuciya tayi mai ƙarfi cikin rashin sanin abinda zata yi. AbdulHamid da yake bayanta ya ce, "Lafiya dai?." Didi ta kalle shi ta ce, "Maman Nayla ce." Ya kalle ta cikin rashin fahimta ya ce, "wacece Nayla?."

"Yarinyar da aka aurawa Omar ita mana."

"To meye ya faru?."

"Tana magana akan gidan da za a ajjiye Nayla, dan suna siyan kayan ɗaki ne. Ni wallahi ban san me zance, ban san me zan aikata ba gabaɗaya kaina ya gama kullewa" ta faɗa tana zama akan kujera tare da dafe kai. Ya ce, "da Omar ɗin ya kamata ki fara magana, ko kuma ki san gidan da zata zauna ɗin ki faɗa musu dan su naga da gaske suke yi."

Didi ta ce, "Na faɗa maka akwai gidan a ƙasa, amma babban tashin hankalina Omar wallahi. Tijarar da zai yi akan auren nan shine bana so, ran kowa sai ya ɓaci wallahi, ya ɓata nasa ran ya ɓata na mutane." AbdulHamid ya ce, "to ya za ayi? Haka Allah ya ƙaddara aurensa

haka zai zo. Ni kuma sai nake ganin kamar zai karɓi auren."

Didi ta kalle shi tana girgiza kai ta ce, "baka san waye Omar ba ne shiyasa kake faɗar haka. Tun asali haushin Nayla yake yi, saboda itace mace ta farko da na taɓa yi masa faɗa a gabanta. Yayi mata tsawa, ya hararеta, ya razanata duk akan na taɓa yi masa faɗa tana wajan. Babu kalma mai kyau da ta taɓa haɗa su, kullum a cikin jin haushinta yake. Kwatsam sai naje masa da labarin itace matarsa? Kana ganin zai amince cikin sauƙi?."

AbdulHamid ya ce, "Wannan duk ba abin damuwa ba ne, indai zai karɓi auren ai shikenan. Ni yarinyar ma nake jin tausayi wallahi, na farko baya sonta, na biyu ga yanayin halinsa, na uku bai ma san da auren ba, na huɗu bazata ta taɓa jin daɗin zama dashi ba. Kiyi haƙuri, amma wallahi wahala zata sha a zama tare da Omar, ban san meye dalilin mahaifinta na aura mata shi ba amma ya dakusar da rayuwarta, ba dan Omar bai cancanta ba sai dan yadda auren yazo."

Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "meye na bani hakuri? Gaskiya ka faɗa, ni kaina na san da haka. Ni kaina tausayin Nayla nake ji, yarinya yar gata, yarinya kyakykyawa, yarinya mai ilimi da wayewa ta ƙare a auren Omaar. In ba ƙaddara ba meye zai kawo haka?."

AbdulHamid ya murmusa ya ce, "ilimi, wayewa, kyau, gata ko kuɗi duk ba shi bashi ne damuwar ba. Inda ace zai karɓi auren hannu biyu duk abinda ki ka lissafa baza suyi tasiri ba, rashin karɓar da bazai yi ba ya fi komai illa a rayuwarta. Koda ya karɓa baza taji daɗi ba, kinga an dakusar da rayuwarta an lalata mata ƙuruciya."

Didi ta kulle ido ta buɗe ta ce, "bara na kira Kawu naji batun gidan sannan na san abinda zanyi akan batun Omar." Tashi yayi ya ce, "zan je na gaishe da Hajiya, in zaki fita wajan Omar ɗin kije sai ki yi min waya." Amsa masa tayi ya fita ita kuma ta kira Kawu akan maganar gidan kamar yadda ya ce.

A gidan Hajja suna zaune kamar Kullum ita da Salma Daddy yayi sallama ya shigo bayansa ƙanensa ne guda biyu Abba da Baba. Suka amsa Salma ta gaishe su suka amsa mata kafin su zauna su gaishe da mahaifiyarsu. Hajja ta amsa ta ce, "yau ku ne tare gabaɗaya?." Daddy ya ce, "eh Hajja, mu ne a tafe."

Hajja ta ce, "Allah ya sa dai Lafiya, dan nasan baku cika zuwa tare ba sai wani abun ya tashi." Abba ya ce, "Gaskiya Hajja ba lafiya ba." Hajja ta ce, "to me ya faru?." Daddy ya ce, "Alhaji Abdullah ne ya kirani, mahaifin Nayla kenan. Shine yayi min waya yana sanar dani yayi mana laifi, Nace laifin meye ya ce ya aurar da Nayla a shekaran jiya juma'a." Hajja cikin mamaki ta ce, "Ya aurar da Nayla kuma? Wanne irin ya aurar da ita ban gane ba?."

Baba ya ce, "mu ma bamu gane ba Hajja,

Mamaki muke yi wanne irin aure ne haka lokaci ɗaya?." Daddy ya ce, "Na tambaye shi na ce wanne irin ka aurar da ita kuma, ya ce min eh da gaske ya aurar da ita yanzu haka matar aure ce. Na ce lafiya wani abu ya faru ne? Ya ce ya faru, shiyasa ya yanke hukuncin aura mata shi." Hajja ta tafa hannu tana salati ta ce, "Waye shi to? Meye dalilin auren kuma?."

"Hajja bai faɗa min dalili ba, amma a yanayin maganarsa na tabbatar da bata daɗin rai ya aurar da ita ba, duk yadda aka yi ɓacin rai ne."

Hajja ta ce, "to ɓacin rai sai ya saka ya aurar da yarinya budurwa lokaci ɗaya haka?. Waye wanda ya aurawa ɗin?." Daddy ya sauke numfashi ya ce, "yaron nan maƙocin ku, ban san asalin sunansa ba amma Tiger ake ce masa." Salma da take ji tana faga tsaye ta wara ido tare da dafe ƙirji ta ce, "Tiger Daddy!?." Babu wanda amsa mata Hajja tayi shiru kafin ta ce, "Wai Omar ƙanin Aisha ta nan kusa damu?." Daddy ya ce, "Shi fa."

Hajja ta ce, "Omar ya aura mata? Abdullahi ya aurawa Hauwa Omar?. To akan me? Omar ɗin ne yaje neman aurenta ko me?."

Daddy ya ce, "Wallahi ban sani ba Hajja, iya abinda na sani kenan na faɗa miki. Shiyasa muka zo gare ki dan ki sani, amma gaskiya bai yi kyauta mata ba, duk da ban sani ba ko da sanin Nayla ɗin." Abba ya ce, "Koda sanin nata aure haka lokaci ɗaya haka kamar auren yaƙi? Kuma a rasa dawa za a ɗaura mata auren sai wannan taqadarin yaron?. Haba ai matsayin sa na mahaifin bai zaɓa mata miji na gari ba wallahi, bai sauke haƙƙin da Allah ya ɗora masa ba."

Hajja ta girgiza kai take yi cike da mamakin wannan lamari mai ɗaure kai ta ce, "A yadda Abdullahi yake matuƙar son Nayla bana tunanin haka kawai zai bata auren Omar, akwai dalilin da yasa ya aikata hakan, amma meye dalilin? Meyasa bai yi shawara da kowa ba ya yanke hukunci haka?."

Abba ya ce, "Hajja ni banga dalilin da zai saka ya ɗauki ɣar cikin sa ya aurawa wannan yaro ba, duk laifin da tayi ai shi ya haifeta, yana da ikon da ita, yana da ikon da zaiyi mata hukunci amma ba ta wannan hanyar ba. Me ye ma ya kawo Omar cikin rayuwarta? Wanne laifi zata yi masa kawai yaji a ransa shi zai aura mata?. Sai dai in akwai wani abun a ƙasa, tabbas Omar ɗin ya shiga rayuwarta ne shiyasa ya yi haka. In ba haka ba haka kawai bazai aura mata shi ba ba tare da dalili ba."

Hajja ta kalli Salma ta ce, "Salma na san kin san komai, Faɗa mana me ya faru?." Salma ganin iyayenta maza sun tsare ta da ido sai ta ruɗe ta ce, "Hajja ni ban san komai ba, yanzu naji labarin auren."

"Ai ba labarin aure na tambayeki ba, meye alaqar Omar da Hauwa?." Tayi shiru bata amsa ba ƙirjinta na bugawa. Baba ya ce, "ba magana akeyi miki ba ne?."

Salma ta ce, "Daman gaskiya Nayla ta jima tana son Omar, duk wannan damuwar da take shiga ana tambayarta meye taƙi faɗa duk akan sonsa ne. Amma babu wanda ya sani daga ni sai ita sai kuma Jidda." Hajja ta sauke numfashi bata ce komai ba cikin ruɗani. Abba ya ce, "iya son da take masa bai isa ace shine ya jawo ya aura mata shi ba, kodai akwai wata alaqa da ta taɓa haɗa shi da Nayla Salma?. Nayla ta bashi kanta ne?."

Salma ta wara idanu tana girgiza kai ta ce, "Wallahi Abba bata taɓa ba, ko magana ma basa yi wallahi, kuma bai ma san tana sonsa ba." Abba ya kafawa Salma ido yana kallo kafin ya ɗauke ido daga kanta. Hajja ta ce, "Bana wannan tunanin akan Nayla Ali, na san bazata taɓa watsar da kanta a waje ba, akwai dalilin mahaifinta na yanke wannan hukuncin ba iya dan tana sonsa bane."

Abba ya ce, "ni fa Hajja banga laifin da zata yi har ya saka shi ya yanke wannan hukunci akanta ba, dan tana sonsa ba hakan yana nufin zai aura masa ita bane, kawai yayi aiki da zuciya ne shiyasa hakan ya faru. Yazo a zauna gabaɗaya, dan gaskiya in akwai damuwa akan auren a saka yaron ya sake ta, bazai yu a cutar da ita dan mahaifiyarta bata raye ba."

Hajja ta ce, "yanzu ya ake ciki?."

"Ya ce zai zo har nan, wai kunyarki yake ji akan abinda ya aikata." Hajja ta ce, "to sai yazo, zan ji dalilinsa na yanke wannan hukunci. Dan Nayla na son Omar ba hakan yana nufin a aure mata shi gabagaɗi ba. Itama sanin akwai tazara tsakaninsu dashi ne ya saka ta ɓoye son da take masa. Ina da tabbacin babu wata mummunar alaqa da ta haɗa shi da Nayla, kamar yadda Salma tace ko magana na san basa yi. Inda ace wani abun ya faru tsakaninsa da ita sai ace shine dalilin Abdullahi, to ni na tabbatar da babu komai."

Salma ta kalli Hajja cikin rauni ta ce, "Hajja don Allah zan je Kaduna yau, Ina so naje naga halin da Nayla take ciki." Hajja ta ce, "kije ki shirya, sai a kai ki ai lokaci bai ƙure ba." Daddy ya ce, "in ta tafi ta barki da wa Hajja?."

Hajja ta ce, "ni kaɗai zan iya zama."

"A'a gaskiya, sai dai in zamu tafi gida tare dake, in yaso duk lokacin ta dawo sai ki dawo."

Hajja ta ce, "to me zai ci ni dan na zauna ni kaɗai? Naga Salma nan gaba kaɗan aure zata yi ko?. Kuma ko bata yi aure ba takardun makarantarta na fitowa aiki zata fara, gwara na fara sabo da zama ni kaɗai ɗin." Abba ya ce, "duk tarin yan matan da muke dasu? Ai sai wacce ki ka ce kina so tazo ta zauna da ke Hajja. Amma yanzu indai har zata je Kaduna to sai dai ki bar gidan nan gaskiya." Hajja ta yi shiru kawai bata ce komai ba tana tunanin wanne irin hukunci Abiy ya yanke haka?.

Salma dai kaya ta haɗa har na kwanaki ta ɗauki duk abinda ta san zata ɗauka ta fito. Tana fitowa aka kira mata drivern Hajja ya tabbatar da motar

lafiyar lau ta yi musu sallama ta fita dan gabaɗaya hankalinta yayi kan Nayla, so take taji abinda ya faru ta kuma ga halin da yake ciki.

KRB2P024

ArewaBooks@nanahaleema11.

Tafiyar Salma ba jimawa Didi tayi sallama ta shigo falon Hajja. Hajja ta amsa da murmushi ta ce, "Aisha sannu da zuwa." Didi ta ƙaraso ta durƙusa ta gaishe ta amsa ta ce, "ya mai gidan naki?."

"Lafiya lau Hajja. Ina Salma?." Didi ta ce, "Salma ta tafi Kaduna wajan Nayla ɗazu. Kin san ta koma jiya." Didi ta ce, "Allah sarki, Allah ya kiyaye hanya."

Hajja ta ce, "Amin. Kin yi sa a AbdulHamid baya yi miki kulle yana barin ki fita, in ba haka ba ranar juma'a ma fa kinzo." Didi tayi dariya ta ce, "dole ce ta saka ni na fito yau ɗin ma Hajja." Hajja ta ce, "Amma dai lafiya ko?." Didi ta ce, "eh lafiya zance, nazo wajan Omar ne na tarar baya nan, gidan ma a kulle yake shiyasa zan zauna a nan na jira shi." Hajja tayi murmushi ta ce, "Malam Omar kenan, carbin ƙwai janka sai mai nutsuwa."

Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "Hajja ban sani ba ko kin ji labarin abinda ya faru, amma jiya yanayin ki ya nuna min kamar baki sani ba." Hajja ta murmusa ta ce, "eh ban sani ba, ɗazu ake sanar dani abinda ya faru."

"Hajja meyasa Abiy ya yiwa Nayla haka?."

"Babu wanda ya san dalilinsa, dan yanzu haka ma ya saka ana ta siyan kayan gida."

Didi ta ce, "Ɗazu Mamanta da kanta ta kirani tana tambayar inda za a kawo kaya da kuma adadin ɗakunan gidan, wallahi Hajja ni gabaɗaya kaina ya kulle na rasa abinda zanyi, wanne irin aure ne wannan ya yiwa Nayla? Ta sani ko bata sani ba duk bamu da tabbas a kai."

"Wannan dalilin ya saka Salma tace zata je Kaduna gano yanayin Nayla ɗin. Amma ke kin san daman tana son Omar?."

Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "na sani Hajja. A ranar ɗaurin aurena kin san yarinyar nan Narma ta Abuja tazo, to a ranar bayan ta tafi na taho nan na bar su a can suke hirar su uku, ita da Jidda da Salma. A lokacin naji komai na kuma tausaya mata domin soyayya bata yi mata adalci ba, Ina ita Ina Omar? Ba sa'ar auren Omar ba ce ita kanta ta sani, sannan Omar ba mutum ne kamar kowa ba, ko wanne uba ne zai bashi auren ɗarsa ba."

Hajja ta ce, "ni babban abinda yake bani mamaki dalilin yin auren da gaggawa haka, meye ra'ayinsa akan wannan auren har ya aikata haka?." Didi ta ce, "wallahi ban sani ba, nima shine abinda yake damuna."

Hajja ta ce, "yanzu Omaar ɗin ya san batun auren?." Kamar zata yi kuka ta ce, "Wallahi Hajja bai sani ba, babban tashin hankalina ma bai wuce tunkararsa da maganar nan ba. Kin san halinsa Hajja, kin san abinda zai yi da wanda bazai yi ba, yadda zan tunkare shi da maganar nan shine abinda yake ɗaga min hankali."

Hajja ta ce, "tabbas zaiyi, zai yi abinda ba ki tunani ba ma dan Omat ya wuce tunanin mu gabaɗaya.." Didi ta ce, "To Hajja wannan ai kin ga akwai rashin kyautawa ita Nayla ɗin, sannan akwai zubar da mutuncinta na ɗa mace. Ace an ɗaura mata aure da wanda ake tunanin zai karɓi auren ko bazai karɓa ba, kinga kamar ba'a kyauta mata ba."

Hajja ta ce, "babu wanda ya san dalilin mahaifinta na aikata haka, ban sani ba ko ita Nayla ɗin ta san zai ɗaura mata aure dashi oho? Amma yanzu me ki ka yanke?."

"Wallahi ban sani ba, ga dai gida Kawu ya bayar kyauta, ya kuma ce min don girman Allah kar na bari Omar ya san shine ya ba da gidan. ni ko zuwa ban yi na duba gidan ba."

Hajja ta ce, "nima a shawarata kar ki faɗa masa yanzu, ki bari komai ya daidaita tukunna sai ya sani."

"Hajja kar yazo yana ɓatawa mutane rai fa."

"Ki ƙyale shi, ki bari sai nan gaba. Ko da ace ma Nayla ta tare a gidansa ki bari sai zaman yayi nisa sannan ki faɗa masa." Dogon numfashi Didi taja ta ce, "Hajja anya haka baganganci bane? Omar fa?." Hajja tayi dariya ta ce, "kar ki damu, komai zaizo da sauƙi in sha Allah. Ni a jikina nake jin shine mijin Nayla, wannan auren nasu aure ne na har abada. Karki damu mu cigaba da yin addu'a kawai." Didi ta ce, "To Hajja, Allah ya sa haka shine mafi alkhairi" ta faɗa kawai ba dan har zuciya ba. Hajja ta amsa da Amin.

•••••••

Ashraf yana tsaye a falo yaji an danna door bell daga ƙofar falon, ya ƙarasa ya buɗe da mamaki yake kallon wanda suka zo. Mum ce sai kuma Najwa ya basu hanya tare da murmushi ya ce, "Mum sannu da zuwa." Murmushi tayi ta ce, "Yauwa Ashraf, mun zo babu notice ko?." Ashraf ya murmusa ya ce, "Haba Mum babu komai, have a seat." Mum ta zauna Najwa ma ta zauna.

Mum ta kalle shi bayan ya zauna ya ce, "Good morning Mum."

"Morning Ashraf, ya kake?."

"Am fine Mum. Ya hanya?."

"Alhamdu lillah. I hope komai yana lafiya tsakaninka da matarka?."

"Yes Mum, Alhamdu lillah."

"Glad" Mum ta faɗa da murmushi.

Najwa ta kalle shi bayan sun gaisa ta ce, "where is she?." Ashraf ya ce, "Tana ciki." Najwa ta miƙe ta shiga cikin bedroom ɗin wajan Narma.

A kwance ta hangi Narma ta rufe kanta da blanket ta ƙarasa ta buɗe fuskarta. Ganin yadda fuskarta tayi ja ya bawa Najwa mamaki, ta taɓa fuskar ta tana mamakin me ya kawo wannan jan. Narma da ta fara bacci tashi ana shafa fuskarta ta fusata ta bige hannun tare da zabura ta ce, "Ashraf stop it, how dare you to touch me?."

Najwa ta ce, "easy Sis! It's me, Najwa." Narma ta kalli Najwa da take kallonta ta ce, "Najwa!." Najwa ta ce, "yes Sis." Sai ta miƙe zaune ta riƙe hannunta ta ce, "Najwa yaushe kika zo?."

"Yanzu, nida Mum ne, tana falo...." Bata ƙarasa ba Mum ta shigo ɗakin. Narma ganin Mum ta shigo sai ta miƙe da sauri ta ƙarasa ta rungume Mum. Mum ta yi hugging ɗin itama tana shafa bayanta ta ce, "My daughter, I missed you."

"Likewise Mum." Mum ta ɗagota tana kallon fuskarta ta ce, "meya faru naga fuskarki tayi ja haka? Are you okay?."

Narma ta ce, "Mum I'm not okay, bana son zama a nan ko kaɗan." Mum ta ce, "stop crying mana, just calm down and let me know what is happening to you." Narma ta ce, "Mum Ina Dad?."

"Dad yana Nigeria. Na taho ne dan na ganki, na damu da rashin ki shiyasa muka zo." Narma ta ce, "na nemi flight nima ban samu ticket ba, da tuni na dawo gida."

Mum kallon fuskar ta take yi ta ce, "So faɗa min me ya faru be?." Narma ta ce, "Mum I hate him, I don't want to see him."

"What are you saying Narma? He's your husband fa." Narma ta ce, "Mum baya sona, he raped me again!" Ta faɗa tana kwanciya a kafaɗar Mum tana kuka.

Riƙeta Mum tayi suka zauna a kan gado ta ce, "ya sake raping ɗinki?." Ta ɗaga kai alamun eh ta ce, "Bana son shi, gida nake so na koma. Ihu yake yi min yana yi min shouting, Sannan ya ce shima baya sona." Mum ta bita da kallo cikin mamaki da ɓacin rai, Narma ta kuma cewa, "Mum ni dai bana sonsa, zan dawo gida kawai." Ashraf ne ya shigo ɗakin Mum dai bata yi magana ba ta bishi da kallo har ya ƙaraso ya ce, "Mum ga takeaway."

Mum ta kalle shi ta ce, "Aheaf me yake faruwa ne? Kalli face ɗin Narma me ya same ta haka?." Ashraf ya kalli Narma da take hawaye ya kalli Mum ya ce, "Mum bata manta da shashashan ɗan daban nan ba, always she'stalking about him,

I'm so jealous when she mentions him." Mum ta kalli Narma ta ce, "Narma why?." Narma ta ce, "Mum ni Nigeria zan koma, na gaji da zama a nan, na gaji bazan zauna ba."

Mum ta ce, "is okay" Mum ta faɗa tana miƙewa tana riƙe da hannun Narma har falon. McDonald yayi musu order Mum bata ci ba, ta dai ci chips ɗin daga nan bata sake cin komai ba. Gabaɗaya tunani take yi akan zaman Ashraf da Narma, kana ganinsu ka san basa zaman lafiya kowa da abinda yake ɓoyewa a zuciyarsa. Kallon Narma tayi ta ce, "Zamu koma hotel, kwana biyu zamuyi zan koma. Don't worry in anjima zamu tattauna abubuwan da suke faruwa, yanzu na gaji, I need rest."

Narma ta ce, "Mum zanje."

"No Narma, ki zauna a nan zan dawo. Kar ki damu komai zai zama daidai" ta faɗa tana shafa fuskarta. Narma ta ɗaga kai suka fita, ko fita raka su bata yi ba shine dai ya rakasu.

Yana dawowa ya kalleta ya ce, "har kina da bakin cewa kin gaji da zama dani?." Banza tayi masa bata amsa ba, yayi tsaki tare hararta ya bar wajan dan haushinta yake ji bai san meyasa ba, duk tarin soyayyar da yake yi mata gabaɗaya ta gushe yanzu baya jin ko kaɗan akan abinda yake ji a ba

Nayla tana kwance a ɗaki taji an dafata, ta buɗe ido ganin Salma sai ta zabura ta ce, "Salma!." Sai kawai ta rungume ta tare da fashewa da kuka. Salma ta ce, "ki daina kuka Nayla, ki nutsu jikinki akwai zafi." Nayla bata daina kuka ba ta ɗago daga jikin Salma ta ce, "Salma Abiy yana fushi dani, ban sani me na yiwa Abiy ba Salma. Salma wai Abiy ya aura min Omar, Meyasa Abiy yayi haka?."

Salma ta ce, "shiyasa nace ki nutsu ki dawo hankalinki sai muyi magana. Amma yanzu kin ci abinci?." Ta girgiza kai alamun a'a Salma ta tashi ta fito ɗaga ɗakin. Falo ta fito wajan Mama ta ce, "Mama akwai abinci?." Mama ta ɗauka ita zata ci ta ce, "akwai mana Salma, duba ki zuba abinda zaki ci." Da to ta amsa ta ƙarasa ta zuba abincin har da tea ta haɗawa Nayla sannan ta koma ɗakin.

Daƙyar ta lallaɓata tasha tea ɗin, ta bata maganin da ta gani a gefenta sannan ta riƙe hannunta bata ce mata komai ba. Sai da taga ta nutsu tana ajiyar zuciya sannan ta ce, "ya akayi haka ya faru?." Girgiza kai take yi alamun bata sani ba. Salma tayi ajiyar zuciya ta ce, "ke kika faɗawa Abiy kina son Omar?."

"Mama ce" ta bata amsa murya na rawa.

"To meyasa ya yanke wannan hukuncin? Ko daman ya ce zai aura miki shi ne?."

"A'a Salma, Abiy baya so, ya ce min na cire Omaar daga raina. Mama ce taka bani ƙarfin guiwa akan zai amince min na cigaba da haƙuri. Ni dai na san na tafi Kano ban tambaye shi ba amma daga nan ban san me na aikata ba. Kuma Mama ce ta saka na tafi, na nuna bazan je ba tace naje zan fi samun hutu." Salma tayi ajiyar zuciya ta ce, "To ki daina kuka, tunda ke kin san baki yi komai ba ko ma meye zai bayyana in sha Allah."

Nayla ta ce, "Salma Abiy fushi yake yi dani."

"Zai daina in sha Allah."

"Ya aura min Omar, ya aurar dani ga wanda baya so, ya aurar dani ba tare da sanina ba."

"Shi Omar ɗin ya sani?."

"Wallahi ban sani ba, ban sani ba Salma. Ban san Ina zan saka kaina na ji daɗi ba." Salma ta ce, "is okay, ki daina damun kanki kinga baki da lafiya."

Ɗan buga ƙofar akayi tare da shigowa. Abiy ne ya shigo da kansa ganin Salma sai ya yi murmushi ya ce, "A'a Salma, saukar yaushe?." Salma ta gaishe shi ya amsa yana tambayarta su Hajja ta amsa masa kafin ya ce, "Ya jikin Naylan?." Salma ta ce, "har yanzu da zafi a jikinta Abiy."

"Zata warware in sha Allah. Kin zo a kai amarya Kano dake kenan, ai kin kyauta." Salma ta kalli Nayla da itama ita take kallo.

Abiy ya kalli Nayla ya ce, "me yake damunki?." Maimakon ta bashi amsa sai ta fashe da kuka. Abiy ya ce, "ba kuka nace kiyi min ba, me yake damunki?." Nayla ta goge ido ta ce, "ciwon kai."

"Ki daina kuka shima zai daina." Kai ta ɗaga alamun to ya buɗe ƙofar ya fita.

Nayla ta ce, "kinji ko? Wai kinzo a tafi dani Kano ya ce, Salma na shiga uku!." Salma ta ce, "baki shiga uku ba Nayla, ko meye zaizo da sauƙi in sha Allah. Ki kwantar da hankali ki komai zai warware, ki cigaba da addu'a komai zaizo da sauƙi." Rarrashinta Salma ta dinga yi har ta ɗan saki jiki suna hira hakan ya yiwa Salma daɗi a haka har dare yayi.

Washe gari.

Saboda rashin lafiya Nayla bata iya tashi da azumi ba duk da ta saba duk sati amma baza ta iya ba. Salma ce ta ke tsaye akanta akan cin abinci da shan magani ita kam gabaɗaya ta zama wani iri. Jawad ma ya sakko yana bibiyar lamarinta da jin ya ta kwana, ita kam gabaɗaya bata su take yi ba, fushin da mahaifinta yake yi da ita ya fi komai ɗaga mata hankali.

Suna zaune a falo Abiy ya fita ita da Mama da Salma da kuma Jawad. Mama ta ɗauki waya ta kira Didi bayan ta ɗauka sun gaisa ta ce, "Aisha Ina ta jiran kiran ki, ya maganar mu?." Didi ta ce, "kiyi haƙuri Mama, sai dare naje na duba gidan ne shiyasa. Falo ne guda biyu, babba ɗaya sai ƙarami ɗaya, sai bedrooma guda biyu."

Mama ta maimaita abinda Didi ta ce sannan ta ce, "kitchen fa?."

"Akwai kitchen da store, kitchen ɗin babu laifi yana da ɗan girma."

"To ma sha Allah, zan fara aiko da kayan in anjima, zan bawa driver number ki sai kiyi musu kwantace a kai gidan. Zan aiko da masu ɗaura kayan duk sai ki yo musu bayani."

Didi a sanyaye ta ce, "to Mama." Mama ta ce, "Sai sun zo" ta faɗa tana yanke wayar. Nayla da Salma duk suna jin abinda yake faruwa, Nayla ta miƙe ta hau sama Salma ma tabi bayanta. Jawad ya kalli Mama ya ce, "Mama don Allah meyasa kika fi mayar da hankali akan kayan ɗakin Nayla? Auren nan kowa ba so yake yi ba, amma hankalinki gabaɗaya yana ga a kai kayan Kano."

Mama ta ce, "umarnin mahaifinku ne, zan canja hakan ne?."

"Amma Mama shi kansa Abiy ɗin ya ɗan sauka saboda rashin lafiyar Nayla, amma gabaɗaya ke ta ta kayan ma kike yi." Mama ta kalle shi kamar zata yi magana sai ta fasa kawai ta tashi ta shiga ɗaki.

Nayla kuwa bayan sun shiga ɗaki kallon Salma tayi ta ce, "Wai kayan aurena ake zance Salma, wallahi komai ya fita daga raina, son Omar ɗin ma na neme shi na rasa." Salma ta ce, "ki yi haƙuri ki cigaba da jurewa. Amma sai naga kamar Mama murna take yi da auren nan. Ki yi haƙuri ina faɗar hakan a kanta, amma daga jiya zuwa yau na fahimci kamar ita so take yi."

Nayla ta ce, "meyasa zata so? Kawai umarnin Abiy take cikawa." Salma ta yi shiru bata ce komai ba amma a zuciyar ta gabaɗaya bata amince da Mama ba, gani take yi kamar da biyu take yin abinda take yi. Duk da ta san Maman bata da wani aibu da hali mara kyau, amma zuciyarta ta dasa mata ayar tambaya akanta.

••••••

Abiy kai tsaye da ya shiga Kano gidan Daddy ya nufa kamar yadda yayi masa waya ya sanar dashi yana hanya. Daddy ya karɓe shi hannu biyu da girmamawa aka tarbe shi da ruwa da kuma abinci. Ya sha dai ruwa amma bai ci komai ba yana zaune a falo shi kaɗai an barshi ya huta. Sai da ya ɗan jima da zuwa sannan Daddy da Abba da Baba suka shigo a tare gabaɗaya.

Sake gaisawa aka yi kowa yana tambayar iyalan kowa kafin Daddy ya ce, "Alhaji Abdullahi mun ji batun aure kwatsam babu shiri, hankalin mu gabaɗaya ya kasa kwanciya musamman da kace zaka zo kayi mana bayani." Abiy ya ce, "ni kaina ban shiryawa auren ba, yazo ne lokaci ɗaya dole na karɓe shi."

Abba ya ce, "Amma me ya kawo shi?." Abiy ya ce, "Nayla tana son yaron, son da take masa ne ya saka ta koma kamar ba ita ba, kullum a rashin lafiya take, kullum a cikin damuwa. Da fari ban fahimta ba, amma daga baya da aka sanar dani sai na fahimci hakan. Na kira Nayla akan hakan ta tabbatar min da tana sonsa. Ni na faɗa mata ban damu da kuɗin namiji ba, abinda nake nema a ko yaushe hali na gari da kuma inda yaro ya fito. A take da na kirata na yanke alaƙar batun yaron, na ce ta cire daga zuciyarta, sannan a cikin masu neman aurenta tabbatar da ta fitar da guda ɗaya."

Abiy ya ce, "ta amsa min kamar da gaske take, na sake maimaita abinda nace amma sai na wayi gari Nayla ta taho Kano. Duk da ban sani ba kuma bata taɓa fita wajan Kaduna ba tare da na sani ba balle tazo Kano, ko aiki zata taje sai ta faɗa min saboda haka tsarina yake a haka suka tashi. Na yi mamaki da naji labarin bata nan amma nuna ba na share ta. Ina nan zaune sai ga wannan saƙon ya shigo wayata Nayla ta turo min" Abiy ya faɗa yana ɗauko waya ya shiga number Nayla ya miƙawa Daddy.

Sai da ya jira ya gama karantawa kaf ya bawa Abba da Baba duk suka karanta duka messasges ɗin sannan Abiy ya ce, "raina ya ɓaci gaskiya akan hakan sosai, ban kuma yi tunanin zata aikata haka ba. Nan take na yanke hukuncin aura mata shi tunda haka ta zaɓa, kuma tunda har take irin wannan furucin akansa aura mata shi shine mafita kar a zo a haifar da ɗa mara ido. Wannan dalilin ne ya saka na aura mata shi a lokacin da nake tsakiyar ɓacin rai, daga baya naji kamar ban kyauta mata ba amma na riga da na aikata."

Daddy ya girgiza kai ya ce, "Tabbas Nayla bata kyauta ba, ko waye a matsayinka dole ransa ya ɓaci ya aikata fiye da abinda ka aikata saboda abinda ta aikata. Amma Alhaji Abdullah anyi aikin gaggawa, Nayla yarinya ce ƙarama, soyayya zata iya sakawa tayi wannan furucin ba tare da ta sani ba. Wataƙila da ka sake bata dama da hakan bai faru ba."

Abiy ya ce, "Eh to ba nace ba, ni a wajena hakan da nayi shine daidai tunda shi ta zaɓa take ganin zata iya zama dashi, ni a wajena na bata shi a matsayin wanda take son kuma zaɓinta." Baba ya ce, "ni babban abinda yake damuna akan auren nan ba komai ba ne face halin yaron, inda ace mutum na gari ne kamar kowa sai mu yi fatan Allah ya sanya alkhairi tunda kowa yasan matar mutum kabarinsa. Amma kowa ya san sunansa ba ta hanyar kirki ba, in na tuna hakan sai naji komai Nayla zata aikata bata cancanci a yanke mata wannan hukunci ba gaskiya, Alhaji Abdullahi."

Abba ya ce, "Shi yaron ya san da auren?." Abiy ya ce, "ban sani ba ko yanzu ya sani." Ya girgiza kai ya ce, "Mahaifinta ne kai kana da ikon yanke hukunci a kanta fiye da kowa, amma duk da haka baza mu fasa faɗa maka gaskiya ba, koda ba Nayla ka yiwa haka ba in muka ji labari zamu faɗa maka tunda an zama yan uwa. Ba dan muna yayyen mahaifiyarta muke faɗar baka kyauta ba, muna faɗa maka ne

a matsayin ɗan uwan mu. Gaskiya ka yanke hukunci cikin fushi da ɓacin rai, in da an bi wata hanyar ba wannan ba da wataƙila hakan bai faru ba."

Abiy yayi ajiyar zuciya ya ce, "Haka Allah ya shirya, amma har zuciyata a yanzu bana jin ban kyautawa Nayla ba." Daddy ya ce, "Shikenan Alhaji. Amma yana da kyau a zauna da yaron aji shi yana da ra'ayin zama da ita, in yana dashi shikenan tunda tana sonsa sai mu ce Allah ya basu zaman lafiya, in kuma bashi da ra'ayi zata sha wahala a zama dashi gaskiya. Kuma ga yanayin da muke ciki a wannan zamani na cututtukan da ake ɗauka, ana gwajen-gwajen jini yanzu kafin aure dan tabbatar da lafiyar su shida ita, haka za'a kaita ba tare da a san matakin jininsa da abinda yake ciki ba?."

"Na bar mu ku komai a hannunku akan wannan, ku yi duk abinda ya kamata, koda auren ku ke ganin za'a samu matsala wuƙa da nama yana hannunku, ku yanke hukunci ba sai an sanar dani ba." Abiy ya faɗa tana kallon Daddy.

Daddy ya ce, "ai aikin gama ya gama Alhaji Abdullah, amma duk da haka zamu ƙoƙarta mu gani. Allah ya shige mana gaba." Aka amsa da amin suka cigaba da tattauanwa kafin yayi sallama ya wuce dan Kaduna zai koma.

KRB2P025

ArewaBooks@nanahaleema11.

Bayan fitar Abiy su uku suka cigaba da tattaunawa akan lamarin Nayla, amma basu da abinda zasu yi tunda shine mahaifinta yana da ikon yanke hukunci a kanta a duk lokacin da ya so ya kuma ga dama. Kasancewar Hajja tana gidan Daddy gabaɗaya suka shiga suka same ta, a wajan Hajja suka samu ƙanwar su Mama Sa’adatu a tare da Hajjan.

Hajja ta kalle su ta ce, “Har ya tafi?.” Daddy ya ce, “ya tafi.”

“To ya aka yi?.” Basu ɓoye masa komai ba suka sanar da ita Daddy ya ce, “Kuma baya dana sanin aura mata shi ya ce har yanzu. Abinda na lura dashi ransa ya ɓaci sosai, ya yanke hukunci cikin fushi da ɓacin rai, kuma itama Nayla bata kyauta ba ban yi tunanin zata aikata haka ba. Amma mun sanar dashi zamu zauna da yaron,

in ba a zauna dashi a san yana sonta ko baya sonta ba zaman gidansa bazai yi mata daƈi ba. Ya ce ya bar komai a hannun mu, mu yiabinda muke ganin ya dace.”

Mama Sa’adatu ta ce, “Gaskiya Nayla bata kyauta ba, amma ni ban ga abinda zai saka ayi mata aure irin wannan a maganar nan ba.” Hajja ta ce, “Koma dai meye shine ya haifeta, duk abinda zamu ji akan Nayla bayan a sa ne. Ku bar shi da hukuncin da ya yanke kawai, abinda zai faru mu yi mata addu’a kawai zai fi.”

Mama Sa’adatu ta ce, “Hajja aure lokaci ɗaya haka? Babu sanarwa, babu kuƈin aure ba lefe?. Kuma mijin ma ba wani na kirki ba, ai sai ace dan mahaifiyarta bata raye ne ya saka muka zuba ido akayi mata wannan auren. Yanzu in da ace tana da rai hakan zai faru ne?.”

“Koda tana da rai hakan zai faru tunda Allah ya rubuta, kawai a bar maganar nan mu yi mata addu’a. Yana girmama mu sosai, kar yaga kamar mun cika zaƙewa akan lamarin iyalansa. Mu yi mata fatan Allah ya sa hakan ya zama alkhairi.”

Duk suka amsa da amin ba dan hakan yayi musu daƈi ba sai dai babu yadda zasu yi ne, amma da suna da iko Nayla baza ta zauna da Omar matsayin mijita ba ko kusa.

Bayan Kwana biyu.

Har ranar laraba Omaar bai san da wannan labari ba, harkokin gabansa kawai yake yi domin kuwa Allah ya dafa masa a sana’ar da ya saka a gaba, sosai yake ganin alkhairi da kuma cigaba fiye da tunaninsa. Shiyasa ya mayar da hankali ya ke kuma ƙaro sani akan abinda yake yi.

Kamar yadda Mama tace ta turo da kayan gidan Nayla a gama ɗaura komai, hatta kayan kitchen a cikin kwana biyu an zuba gida ya fito yayi tar kana kallonsa ka san gidan amarya ne. Mama ce kawai take shagalinta a wannan ɓangare amma ko Abiy ɗin baya bi ta kai balle kuma Nayla da ta koma kurma saboda bata son magana.

A daren ranar larabar suna zaune ita da Jidda da ta zo Kaduna saboda maganar, ita Salma suna hira a kusa da Nayla, Nayla dai bata saka musu baki su ne suke hirar su ita kam abinda take tunani daban. Mama ce ta shigo falon da sallama suka amsa sallamarta, ta kalle su ta ce, “ya kamata ace an yiwa Nayla gajeren gyaran jiki, dan haka gobe mai gyara zata zo zata yi mata abinda ya samu, sannan zata yi mata ƙunshi tunda jibi ne tafiya Kano.”

Gaban Nayla ya faɗi har sai da ta runtse idanu bata kalli Mama ba. Jidda ta ce, “Haba Mama! Wanne irin gyaran jiki a cikin wannan yanayi?. Don Allah Mama ki bar faɗin haka wallahi bana son ji kwata-kwata. Ba ma fatan auren nan ya tabbata balle a dinga tunanin wani gyaran jiki ko ƙunshi.” Mama ta kalli Jidda ta ce, “ai kam dole za a yi, tafiya Kano ranar juma’a babu fashi ranar zata tare a gidanta. Haka za’a kaita babu wani gyara?.”

Jidda ta ce, “Haba Mama don Allah, ki daina faɗar haka mana. Auren nan fa ba so muke yi ba.”

“Kece bakya so, amma Nayla tana matuƙar son mijinta ko Nayla?” Ta faɗa tana kallon Nayla. Nayla bata iya buɗe ido ba saboda haushin Mama da ta fara ji a zuciyarta, tunda daga abinda tayi mata akan Abiy shikenan ta fara jin wani abu akanta wanda bata san meye ba.

Mama ta sake cewa, “ku dai shirya gobe zata zo” tana faɗa ta fita daga falon. Bayanta Jidda ta bi sai suka haɗu da Jawad ya taho duba Nayla ya kalleta ya ce, “ke kuma ina zuwa?.” Jidda ta ce, “Wajan Mama zan je Yaya J, abinda take yiwa Nayla gabaɗaya bai kamata ba, ana cikin wannan yanayi amma Mama tana zancen wai zata kira mai ƙunshi da gyaran jiki ta yiwa Nayla?. wallahi ban ji daɗi ba, sai ta dinga ganin dan ba itace ta haifeta ba shiyasa take faɗar haka.”

Jawad ya ce, “ke ni fa na lura kamar Mama murna take yi da auren nan, gabaɗaya itace abin bai dame ta ba.” Jidda ta ce, “nima dai na lura daga zuwana gidan nan zuwa yanzu, ko ba murna takeyi ba bata nuna ta damu akan hakan.”

“Ki ƙyaleta karki bita, kije ku cigaba da rarrashin Nayla ɗin a hankali.”

“Amma Yaya Jawad wallahi ban ji daɗi ba, Nayla ta kasa magana gabaɗaya, kuma ga cousin ɗinta Salma, zata ga kamar Mama ce take son auren nan.”

Jawad ya ce, “ki ƙyaleta ki je kawai, zan san abinda zan yi.” Jidda ta koma ciki jiki a sanyaye ta zauna kusa da Nayla da kanta yake kafaɗar Salma tana hawaye. Dafata tayi ta ce, “Twiny don Allah ki yi haƙuri da abinda Mama ta ce.” Nayla ta kalleta ta ce, “Twiny me Maman tayi?.” Zata sake magana ta ce, “ki bari bana so, komai Mama tayi tana yi ne matsayinta na uwa a gare ni, Don Allah karki sake cewa komai.”

Jidda ta ce, “Yanzu haka zamu zuba ido a kai ki gidan Omat ba tare da soyayyarki a zuciyarsa ba?. Ni bani da tabbacin ma ya san da auren nan, in ya sani ya karɓe ki ko bai karɓa ba?.” Salma ta ce, “abinda yafi komai tsaya min a rai kenan.” Nayla bata iya cewa komai ba idanunta na kulle fuskar Omar na gilma mata a ranar ɗaurin auren Didi da yake tsokanar Didi.

Washe gari ranar alhamis da safe suna zaune gabaɗaya a falo ana breakfast saɓanin Nayla da take a gefe a rakuɓe. Abiy ya kalle ta ya kalli Jidda ya ce, “kin gama shirya mata kayanta? Gobe zata tafi gidan mijinta in sha Allah.” Jidda ta kalli Abiy a sanyaye ta ce, “Don Allah Abiy ka sake bata lokaci, ko zuwa nan da bayan sallah ne sai ta tare. Amma yanzu ba a shirya komai ba ace zata tare a gidan wani?.” Abiy ya kalle ta ya ce, “Haka ta ce miki?.”

“Ko bata faɗa ba na san hakan ne a zuciyarta Abiy.”

“Ke dai haka ki ke tunani, amma Nayla ba haka take so a zuciyarta ba. Ki barta taje gidan mijinta tayi ibada, zata fi samun lada a watan Ramadan ɗin a can.”

Nayla ta ɗago ido ta kalli Abiy suka haɗa ido sai ta mayar da kan ƙasa bata ce komai ba. Abiy ya ce, “Ku shirya komai, gobe daga nan za a kaita gidan Hajja, daga nan Hajja ta kai ta gidan mijinta. Na sauke nauyin da yake kaina a matsayina na mahaifinta.”

Jidda tayi ajiyar zuciya, ta kalli Mama ta ɗauka zatayi magana sai taga abincin ta ma take ci hankali kwance. Sai daga baya Mama ta ce, “jiya nayi magana da Zaliha da take Kano, tana tambayata ya aka yi haka ya faru na ce ta tambayeka. Amma ta ce zata kasancewa a gidan Hajja a kai amarya da ita.”

Abiy ya ce, “Su Yaya Ashiru da su Kawun Zaria suna tayi min waya ban san waye ya faɗa musu ba, na ce duk na hutar da ku hidimar biki bana buƙatar ayi komai amarya kawai nake so a kai.”

Jidda ido ta ya ciko da hawaye ta ce, “don Allah Abiy ka amince ko walima mu yi a goben.” Ya kalli Jidda ya ce, “lokaci ya ƙure, inda kin san kuna da wannan shirin da kin sanar dani da wuri, gobe har yaushe aka gama walima aka tafi Kano? Kin san bana son tafiya in dare ya yi.”

“To Abiy a ɗaga tafiya zuwa ranar Sunday.”

“Ke Jidda! Ya Isa, kar na sake jin wannan maganar a bakin ki kin gane?” Ya faɗa yana kallon ta a tsawace. Kai ta ɗaga tana goge hawaye. Ta kalli Nayla da har lokacin kanta yake a ƙasa kafin ta miƙe ta hau sama. Jidda ma bin bayanta tayi dan bata ga amfanin zama a falon ba.

Nayla kasa kukan ma tayi ta zauna akan stool ɗin madubi tayi shiru. Jidda ce ta shigo ta dafata ta ce, “Nayla ki yi haƙuri, wataƙila wannna auren alkhairi ne a gare ki da rayuwarki shiyasa yazo a haka.” Ta kalli Jidda da idanunta da suke a kumbure ta ce, “ta ya zai zama alkhairi bayan mahaifina baya son auren nan? Ta ya zai zama alkhairi bayan mahaifina yan fushi dani?.” Salma ta ce, “Allah bazai kama ki da laifi ba, tunda ke kin san baki yiwa Abiy komai ba.”

“Ku ka sani ko na aikata ɗin ban san nayi ba?.” Jidda ta ce, “Rashin sani ne, in ma kin aikata ɗin baki sani ba Allah bazai kama ki da wannan laifin ba. Ki karɓi wannan jarabawarki sai ki ga abin yazo ya wuce inda mu ke tunani.” Knocking ƙofar aka yi tare da turowa, duk suka kalli ƙofar suka ga Jalila ce da wata mata a bayanta.

Jalila ta ce, “Ya Jidda Mama ce tace na rako ta ɗakin nan, wai mai ƙunshi vc.” Nayla duk suka kalla kafin su yi magana Nayla ta ce, “bana buƙatar komai, ki ƙyale ni kawai” ta faɗa tana tashi ta shiga banɗaki zuciyarta kamar zata fito. Jidda ce ta sallani mai ƙunshi dan basa tare da farin cikin yin wani abu ƙunshi. Gabaɗayan su suna cikin damuwa, ɓoyewa suke yi suna ƙoƙarin ganin sun fitar da ita daga damuwar.

••••••

Omar yana zaune da yaransa a falo ana tattaunawa akan sabon machine ɗin da suka siya. Bashir ya ce, “Tiger ana samun customers sosai daga Lagos, kuma alhamdulillah kaya in suka tafi basu taɓa dawowa ba.” Omar yayi ajiyar zuciya ya ce, “haka muke so.” Tk ya ce, “Amma Boss wannan couples design ɗin da za’a samu mace da namiji da zasu dinga sakawa a ƙafar su ana yin hoto ana watsawa a dnoya zai fi ɗaukar hankali. Haka naga anayi dana je Lagos kai kaya.”

Bashir ya ce, “Hakan zai yi kyau kuma zai ɗauki hankali, lokaci ɗaya za a fi fahimtar na mace da namiji ne iri ɗaya. Kuma Tiger da zaka amince ƙafarka ma zatayi kyau da hoton.” Kallon ƙafar tasa ya yi da take a bayyane dan three quater ne a jikinsa.

Omar ya ce, “kawo mu ga.” Yana faɗa ana miƙo masa takalmi guda ɗaya ya saka a ƙafarsa ta haggu wacce take ɗaure da baƙin abun da yake ƙarawa ƙafarsa kyau. Bashir ya ce, “na rantse da Allah Boss yayi maka bala’in kyau.” Cirewa yayi ya ce, “zamu san abinda zamu yi a akan hakan.”

“Allah ya biya Tiger na mu” ya faɗa yana duba wayarsa da take ƙara.

Ɗauka yayi suna magana akan takalman da ake so yana yanke wayar ya ce, “Tiger harkar social media ɗin nan tana yi sosai, yanzu haka daga Abuja ne ana son ƙafa ɗari biyu da hamsin. sun yi min magana a can ba kula ba sai aka kira ni.” Omar ya ɗaga kai kamar baya son magana ya ce, “ayi abinda ya kamata. Ina Goje?.”

Tk ya ce, “yana inda ka tura shi ƙaro ilimi akan harkar nan.”

“Yayi kyau, ku je a cigaba da aiki.” Tk ya miƙe ya ce, “Boss nan gaba fa shagon nan kaɗan zai yi mana wallahi, a haka ma shago uku aka haɗe amma kayan matsewa suke yi.” Bai kula shi ba sai ɗora ɗafa kan ɗaya da yayi bai ce komai ba.

“Assalamu alaikum” aka faɗa daga bakin ƙofa ana shigowa. Duk kallon ta suka yi suka haɗa biki wajan gaisheta ta amsa ta ce, “ya kasuwa?.” Suka amsa kafin su fita. Kallon ta Omar yayi ya ce, “kwana biyu me kike zuwa yi ne? Baki yi sati da zuwa ba fa.” Ta zauna tana kallon sa ta ce, “ana yiwa mutum iyaka da zuwa gidan su ne?.”

“Shi mijin naki ne yaga zai iya da yake barin ki yawo a kan titi.”

“Laifi ne hakan?.”

Bai ce komai ta kalle shi ta ce, “Magana nazo mu yi.” Ya sauke ƙafa ya kalleta ya ce, “maganar meye da ta saka ki fitowa yanzu?.” Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, “magana ce mai mahimmaci Omar.”

“Ina ji.” Ta kalle shi ta ce, “Akwai abinda zai faru gobe, don girman Allah Omar kar ka bani kunya, don girman Allah, dan darajar iyayenmu kar kayi abinda zai ɓata min rai.”

Jin yadda take masa magiya ya ɗaga idanunsa ya kalle ta ya ce, “meye shi?.” Didi ta ce, “ko meye zaka ji goben, amma don Allah kayi min alqawarin duk abinda zai faru zaka tsaya ka fahimta baza ka yanke hukunci cikin fushi ba.” Da mamaki yake binta da kallo yana girgiza kai ya ce, “to akan me zanyi alqawari akan abinda ban sani ba Didi?.” Didi ta ce, “Baka yarda dani ba ne?.” Bai amsa mata ba dan a ganinsa ta san amsar basai ya faɗa ba.

Didi ta ce, “ka san bazan cutar dakai ba, bazan yi abinda rayuwarka zata shiga wani hali ba, haka zalika bazan yi abinda zai taɓa zuciyarka ba.” Ya jingina da kujera ya ce, “shiyasa nace me ye ya faru? Tunda har kike min wannan magiyar kin san abinda ya faru, meye shi to?.” Didi tayi ajiyar zuciya tana kallon sa kamar yadda yake yawo da idanunsa akanta ta ce, “eh na sani, amma kai bana so ka sani sai a goben. Kayi min alqawari baza kace komai ba, sannan kuma duk abinda nace maka zaka yi, koda gidan nan nace ka bari ka koma wani zaka koma.”

Ɗan taɓe baki yayi dan maganar bata wani ratsa shi ba ya ce, “Didi bazan iya alqawari akan abinda ban san meye ba.” Didi ta ce, “amma ai na faɗa maka bazan cuce ka ba ko?.”

“Nima ban ce zaki cuce ni ba, amma bazan iya yi miki alqawari akan abinda ban san meye ba. Wataƙila bazan iya cika miki shi ba, tunda naji kina yi min magiya akan yarda na tabbatar da ko meye kin san bai yi daidai da ra’ayina ba. Sannan meye ya kawo maganar barin gidan nan?.”

Wallahi kamar tsoro yake bata, har fargabar gobe take yi da abinda zata haifar, hakan ya saka ta kafa masa idanu sai da ya kai ƙarshen maganarsa sannan ta ce, “Omar don Allah ka amince da ni, bazan cuce ka ba ai ko?.”

Ya dafe kai ya ce, “Sai maimaita magana ɗaya kike yi, na ce eh nasan baza ki cuce ni ba amma meye na maimaita min hakan?. Wanne abu ki ka shirya ban sani ba?.” Didi ta ce, “ban shirya komai ba, in na na shirya ɗin ma gobe zaka gani.”

“To nidai bazan iya yin alƙawari ba gaskiya, ki jira zuwa goben ki gani, in zan iya shikenan in bazan iya ba ma kin san sauran.”

Didi a sanyaye ta ce, “Omar….!” Dakatar da ita yayi ya ce, “Didi don Allah! Bazan yi alqawari akan abinda ban sani ba, ki jira Allah ya kaimu goben mu ga ni, in zan iya to in bazan iya ba shikenan. Akan me zaki turke ni akan sai nayi miki alqawari a kan abinda ban san meye?.” Didi ta sauke numfashi ta ce, “Shikenan naji, kayi min alqawarin baza ka bani kunya ba.”

“Shima bazan yi ba, tunda baza ki faɗa min abinda ya faru ba ki bar maganar kawai” ya faɗa yana fashi tsaye ya bar mata wajan.

Didi ta bishi da kallo zuciyar ta cike da matsanin tsoro akan abinda gobe zata haifar, taya zata ce masa ai gobe matarka zata tare an ɗaura maka aure? Ita kanta ta san ta taro aradu da ka indai Omar ne, baya ɗaga ƙafa akan ra’ayinsa, ko ita ɗin ce baya sassauta mata sai ya kai aya yake tsayawa ya lura da itace a gabansa. Tabbas ta san kafin ya amince da yaji maganar ya gama ɓata mata rai da maganganunsa mara control ta yadda bazata iya kuma cewa komai ba. To yanzu ya zata yi? Ta faɗa masa ko kuma ta ƙyale shi?.

Motsin fitarsa daga falon taji ta sake kallonsa taga har ya fice ta kawar da kai tana jin zuciyarta gabaɗaya babu daɗi, ji take kamar ta yiwa Nayla kuka, dan wallahi zama da Omar a wannan yanayi zata sha matuƙar wahala dashi kafin ya saba.

Fans Omar zai karbi auren nan kuwa?.

KRB2P026

ArewaBooks@nanahaleema11.

Narma tana zaune a ɗaki kwana biyu da su Mum suka zo ta sake sosai suna yawo a ƙasar, amma tunda suka wuce gabaɗaya komai ya fitar mata daga rai. Tana zaune a agefen gado tana shan tea a nutse Ashraf ya shigo yana binta da mayen kallon da ya saba. Kallonsa tayi suka haɗa ido ta ɗauke kai ya zauna a kusa da ita ya ce,

"Haba my baby, meyasa ki ke min haka ne?. Yanzu saboda Mum ta tafi shine ki ka shiga damuwa haka?."

Bata ce masa komai ba ta miƙe ta shiga bathroom ya bita da kallo. Numfashi ya sauke yana jan tsaki, ya gaji da iskancinta wallahi, ya gaji da pretending yana lallaɓata, ubanta zai fara ci ya lura bata da kirki zuma ce sai da wuta. Yana nan zaune ta fito ɗaure da towel da alama wanka tayi fuskarta a ɗaure tamau. Yawu ya haɗɗɗye ganin kyawawan kafafunta a bayanne har cinyiyonta. Sannan daga saman towel ɗin ya ɗan zame ana iya hango saman kirjinta.

Muguwar sha'awarta da yake dannewa kwana biyu yaji tana fizgar sa gareta, miƙewa yayi ya tako ya zo inda take ya tsaya a bayanta yana kallo ta ta madubi. Haɗa ido suka yi ta ɗauke kai ta ɗauki body lotion zata shafa ya karɓa daga hannunta. Yunƙurawa tayi zata bar wajan ya riƙe ƙugunta ya haɗa da jikinsa ya ce, "Easy my Baby, Zan shafa miki man ne." Ya faɗa yana matsa man a hannunsa ya fara shafa mata daga wuyanta zuwa ƙirjinta da kafaɗunta.

Yadda yake shafa mata man sai da ta lumshe idanu ta buɗe suka hada ido ya ɗaga mata gira, gabaɗaya fuskarsa sai ta koma mata ta Omar, tunda shima ɗaga gira sararsa ce sosai, bai cika bata amsa in tayi magana ba sai dai ya ɗaga gira. Ganin ga koma mata masoyinta ya saka ta sakin murmushi tana sake ƙarewa fuskar kallo cikin so da shauƙi. Ganin tayi murmushi ya saka Ashraf jin daɗi a zuciyarsa, ya fara zame towel ɗin zuwa ƙasa yana cigaba da sha mata man cikin salon da zai zautar da ita lokaci ɗaya.

Ganin yadda ta rufe ido ruf ya kai bakinsa kunnenta ya ce, "I love you my Baby, I so much love you." Buɗe ido tayi ta kalle shi, man da yake shafa mata ne ya faɗi ƙasa sai ta ɗan firgita ta dawo hankalinta tuna ba fa Omar ɗinta bane Ashraf ne. Kwace jikinta tayi bayan ta riƙe towel ɗin da yake a cikin ta dan ya sauke shi daga ƙirjinta. Mayar dashi tayi ta rufe jikinta ta ce, "zaka iya bani waje please?." Kallonta yayi cikin tsananin buƙatuwa ya ce, "Haba my baby, kar ki yi min haka kin ji?."

Kallonsa take yi dan gabaɗaya zuciyarta bata ƙaunarsa, tsanarsa take ji a zuciyarta mai yawa baza ta sake mallaka masa kanta ba sai dai duk abinda zaiyi yayi mata. Sake nuna masa ƙofa tayi ta ce, "ka bani waje bana son ganinka."

Takowa yayi zuwa inda take ta zaburata yi gefe ta ce, "na ce ka bani waje ko? Kar ka sake kuskuren taɓa min jiki wallahi." Jin yadda tayi magana da tsawa ya saka ya buɗe janayen idanunsa ya kalle ta itama shi take kallo ta ce, "kar ka matso inda nake, ka fita ka bani waje bana ƙaunar ganin ka."

Sake takowa ya ke zuwa inda take tana ja baya, da hanzari ya damƙo hannunta tayi ihu ta ce, "Wallahi baza ka sake mallakar jikina ba Ashraf, bana sonka, bana ƙaunarka ka ƙyale ni." Jin abinda tace sai ya ɓata masa rai ya kalleta ya ce, "ni kuma zan nuna miki jikinki nake aure ba ke ba" ya faɗa yana riƙeta da ƙarfin gaske ya fizge towel ɗin jikinta ya jefa ta kan gadon, zata miƙe ya saka ƙafa ya taketa ya danne ta yadda baza ta iya koda motsin kirki ba.

Kuka take tana faɗin, "bana sonka, bana ƙaunarka, na tsane ka." Ya kalleta ya ce, "nima bana sonki, amma Ina son jikinki. Baki isa ki hana ni mallakarsa ba tunda kina amsa sunan matata." Kuka take tana juya kai amma ya riƙeta tamau babu ta yadda zata iya ƙwatar kanta. Tana ji tana gani ya sake yi mata fyaɗe kamar yadda take faɗa, bai ƙyale taba sai da ya tabbatar bakin cewa bata sonsa ya mutu sannan ya tashi.

Sai numfashi take saukewa na wahala saboda azabar da ya gana mata, shi kansa ya wahala amma saboda ya nuna mata ruwa ba sa'an kwando bane shiyasa yayi mata haka. Wanka yayi ya fito ya kalleta a baje a kan gado tana sauke ajiyar zuciya. Hararta yayi ya ce, "daga yau irin halin da zaki dinga shiga kenan indai zaki dinga cewa zaki yi min gardama, wallahi na daina binki da rarrashi, Igiya zan siyo na dinga ɗaureki nayi abinda nake so na tsallake na ƙyale ki tunda haka kika zaɓa."

Kallon sa tayi murya a shaƙe ta ce, "bazan sake kwana a Texas ba, na faɗawa Mum zan bita taƙi tafiya dani, amma yanzu bazan sake kwana ba." Baice mata komai ba sai bayan ya shirya ya ƙaraso inda take ya ɗauke wayarta, ya koma inda kayan su yake ya ɗauke passoport ɗinta ya nuna mata ya ce, "wallahi babu inda zaki je, babu ke babu amfani da waya sai lokacin da na ga dama. Ban gama morarki ba har yanzu balle ki ce zaki koma nigeria" ya faɗa yana ficewa ita kuma ta fashe da kuka.

Yana fita ƙofar da zata fitar da kai shi compound na gidan ya canja passoword ɗin ƙofar saboda kar ma tayi tunani guduwa, dan bai gama fanshe wahalar da ta bashi ba, ta tara masa sha'awarta mai yawa tun kafin ya aureta, baza su haɗu su rabu ba sai ya shiga mugun yanayi ba saboba shigar jikinta. Balle in ta kwanta a jikinsa

kusan rasa hankalinsa yake yi. Dan haka sai ya gama fashewa son ransa sannan zai ƙyaleta.

•••••••••

Didi har dare tana gida, Omar tunda ya fita ya bar gidan bai dawo ba, ji take ina ma zata iya hana zuwan gobe da tabbas ta hana zuwanta saboda abinda zata tarar a wajan Omar. Gabaɗaya a sanyaye take yin komai har ta yi masa girki ta ajjiye masa.

Bayan sallar magriba ya dawo gidan yayi mamaki da ya ga gidan a buɗe dan bai ɗauka Didi tana ciki ba. Har ya shigo falon bata sani ba ta shiga duniyar tunani, ya zauna ya ce, "Didi tunanin me kike yi?." Kallon inda taji maganarsa tayi ta ganshi a zaune ya zuba mata idanu ta ce, "yaushe ka shigo?."

"Na shigo kina aikin tunani.Wai me yake faruwa ne don Allah?." Tayi ajiyar zuciya, "Sai gobe zaka ji. Ni dai burina kar ka bani kunya Omaar."

"Ko dai AbdulHamid ɗin yake yi miki wani abun da bakya so?." Ta kalle shi ganin yadda ya kafa mata idanu yana kallonta yana jiran amsar ta ce, "Ko ɗaya."

"To meye?" Ya tambaya cike da damuwa da kuma gajiya da maganar.

Didi ta ce, "na faɗa maka zaka ji gobe, amma don Allah....." dakatar da ita ya ce, "zan baki kunya kuwa indai aka yi min abinda bai min ba, bazan yi miki alqawari akan abinda ban sani ba dan haka ki daina roƙona. Wallahi bazan yi alqawari ba kin ji na rantse, haka in aka yi min abinda bai kwantan min ba zan baki kunya" ya faɗa tana kallonta. Ya yi ƙaramin tsaki ya ce, "bazan sake tambayar damuwarki ba, tunda ban kai matsayin na sani ba ki riƙe kayar ki."

Jikin Didi ya sake yin sanyi jin harda rantsuwa, ta san kuma indai ya rantse magana ta ƙare, baya taɓa karya rantsuwa balle ta saka ran zai yi kaffara. Ta zuba masa ido tana kallo cikin rashin sanin abinda zata yi. To da wa zata haɗa Omaar wanda yake jin maganarsa...? Babu kowa a duniyar nan, mutum ɗaya ne tal kuma baya duniya, baya shi babu wani da Omar yake ganin darajarsa, ita ɗin ce kawai kuma gashi da alama za a kai ruwa rana dashi.

Tashi yayi ya fita ya barta a wajan yana mamakin abinda zai faru goben wanda shi bai san dashi ba kuma ta kasa faɗa masa. Har aka yi sallar i'sha tana nan, ya dawo cikin gidan tana zaune ganinsa sai ta miƙe ta ce, "nayi maka girki, ni zan wuce sai gobe."

"Ke kaɗai zaki tafi?."

"A'a, yazo zamu wuce." Kai ya ɗaga mata kawai ya wuce kitchen ta fita jikina matuƙar sanyaye.

Shi kansa Omar ɗin da tunani ta barshi, bayan ya gama cin abincin tunanin abinda zai faru goben yake yi, duk yadda ya kai ga son ganowa ya kasa dan gabaɗaya tunaninsa ya tattara akan wani abun ne akan danginsu ko kaɗan bai yi makamancin tunanin abinda yake faruwa ba. A haka ya gama cin abinci ya ɗan zauna yana danne-dannen waya saboda yanayin sana'ar ta su sannan ya tashi ya fita ya kwanta.

Washe gari.

Nayla tun asuba yanyinta ya sake canjawa, ko magana bata iya yi sai dai ta bisu da ido, a haka take zaune ko bacci bata iya komawa ba saboda fargabar da take ciki. Gari yayi haske sosai, a lokacin ƙarfe tara na safe ta jiyo muryar Abiy a kusa da ɗakinta. Miƙewa tayi daƙyar ta kalli Salma da take kallonta tashin ta daga bacci kenan, ta kalli Jidda da take bacci dan a wajena ta suke kwana basa iya barin ta ita kaɗai.

Fita tayi tana fitowa falon suka haɗa ido da Abiy. Ƙarasowa inda yake tayi ta zube a ƙasa ta ce, "Abiy ina kwana."

"Kin tashi lafiya? Ya jikin?."

"Da sauƙi" ta furta a sanyaye ya kalli Mama da tazo wajan ya ce, "kiyi hanzari ki shiryata bana so lokacin sallar azahar ya yi ba ku wuce ba. Nan da sha ɗaya nake so ku wuce gidan Hajja" Abinda ya ce kenan y bar wajan Nayla ta kasa koda motswa.

Mama ce ta ƙaraso ta ɗagota ta rungume a jikinta ta ce, "mahaifinki baya fushi dake Nayl, ya kamata ki fahimta ki daina asarar hawayenki haka, baki da lafiya koda dan lafiyarki ki nutsu don Allah." Nayla bata ce komai b, a lokacin Jidda da Salma suka fito falon Mama ta kalle su bayan su gaisa ta ce, "Ku kawo mata abinda zata ci." Jidda ce ta sauka da kanta ta kawo musu abinci suka ci ita dai daƙyar ta iya shan tea.

Bayan ta gama Mama ta kalle ta ta ce, "muje ki yi wanka." Hannunta ta riƙe har ɗaki da kanta ta haɗa mata ruwan wanka ta ce tayi. Nayla ta shiga banɗakin jiki a sanyaye tayi wanka ta fito, Mama ta fita ba jimawa ta dawo da kaya ta ajjiye mata ta ce, "ki saka wannan" ta faɗa tana bata waje. Salma da Jidda ne suka shigo ta kalle su ta ɗauke kai dan bata iya cewa komai, hawayen ma ya gama ƙafewa a idanunta.

A haka ta saka kayan a kasalance, atamfa ce mai tsadar gaske ɗinkin doguwa bubu. Tana gama sakawa Mama ta shigo ta ɗauki mayafin ta yafa mata ta ɗauki turare akan madubin ta fesa mata ta ce, "mahaifinki yana jiranki, zo mu je" ta kalli Jidda da Salma ta ce, "Ku haɗa mata kayan da zata yi amfani dasu kafin a haɗa mata duka." Amsawa suka yi a sanyaye ganin da gaske anyi auren Nayla har ana niyar kaita gidan mijinta. Ba jimawa sai ga Jalila da babbar trolly bag ta kawo musu, suka karɓa duk kayan da hannun ya kai suke watsawa a ciki.

Abiy yana zaune a falo shida Yaya da Jawad Mama ta shigo da Nayla tana riƙe da hannunta. Tunda Abiy ya ga Nayla a haka sai jikinsa ya yi sanyi matuƙa, ya bita da kallo cikin wani irin yanayi wanda bai yi tunanin zai ji shi a lokacin ba.

Nayla ta zauna a akan carpet Mama ta ce, "Abiy ga ta kamar yadda ka ce." Abiy ya kalle ta ya ga kanta yana ƙasa, ya yi ajiyar zuciya yana kallonta kafin ya ce, "Hauwa!." Wani irin dum taji a zuciyarta ta runtse, hawayen da ta nema ta rasa suka fara cikowa a idanunta tare da sakkowa kan fuskarta.

"Yau zaki tare a gidan mijinki wanda kika zaɓa matsayin wanda kike so ki ke ganin zaki iya rayuwa dashi. Duk da auren yazo a bazata a wani yanayi wanda bai miki daɗi ba ina so ki san aure dai sunan sa aure, duk inda akace kalmar miji to mijinki ne biyayya ta zama dole a gareki. Kar ki yi tunanin komai akan auren, kawai ki yi masa biyayya ki nemi aljannaki a gare shi. Ki yi zaman ki a Kano ki yi bautar aure da biyayya ga mijin da ki ka zaɓa matsayin abokin rayuwarki. Bana so na ganki a

Kaduna har sai lokacin da nace kizo, ba dan bana son ganinki ko dan kin yi min laifi ba, sai dan inaso ki nutsu ki yi zaman aure. Dan haka babu ke babu zuwa gidan nan matuƙar bani na buƙaci hakan ba. Kin san meye aure, kin san me ake nufi da aure, kin san haƙƙin miji a kanki, kin san naki a kansa. Ki yi biyayya ga mijinki, ban da rashin kunya, ki yi ko yi da halin mahaifiyarki wajan biyayya da kyakykyawan zama. Allah ya bada zaman lafiya. Abinda zan ce miki kenan, Allah ya kiyaye hanya, Allah ya kai ku lafiya, Allah yasa haka shine alkhairi a gareki."

Kuka Nayla take yi sosai jin kalaman Abiy na kar tazo gida, ta ƙaraso inda yake, ta miƙe akan guiwarta, ta matsa kusa dashi sosai ta ce, "Abiy ban san meyasa ka yanke wannan hukuncin a kaina ba, ban sani me nayi maka ba, ban san meyasa kayi fushi dani har haka ba. Abiy ban san laifin da nayi har kace kar nazo gidan nan sai ka neme ni ba, Abiy gidan da aka haifeni ka yi min iyaka dashi.....!"

Ta kasa ƙarasa maganar saboda kukan da yaci ƙarfinta. Ta sassauta kukan ta ce, "Abiy nidai burina ka yafe min, ka daina fushi dani, kuma ko meye ya faru har ka yanke wannan hukuncin a kaina wallahi ban sani ba, bani da hannu akai dan ban aikata komai ba." Kuka take yi sosai tana durƙushe a gabansa.

Ta kuma cewa, "Bani da mahaifiyar da zata fahimce ni, inda Ummana tana da rai ita zata iya fahimtar abinda nake so ka fahimta Abiy. Abiy tunda nake ban taɓa jin kewar mahaifiyata kamar wannan lokacin ba, ban taɓa jin zafin rashin uwa ba sai a wannan lokacin.....! Ka cike min gurbin uwa da uba, amma a yau ina kewarta, ina tsananin kewarta. Gashi ko fuskarta ban sani ba, a hoto kaɗai nake ganinta, amma kewarta nake ji har cikin rai Abiy.....!" Kuka ya ci ƙarfinta ta kifa kanta a guiwar Abiy tana kuka sosai.

Dukkan su ta basu tausayi, Jalila da take tsaye kuka take yi haka Jidda da Salma da suka fito. Nayla ta ɗago ido yayi kaca-kaca da hawaye ta ce, "Na ɗauki wannan auren a matsayin ƙaddarata kuma jarabawata, jarabawar mahaliccin mu tana zuwa a lokacin da baka yi tunani ba kuma baka yi zato ba. Na ɗauki wannan abun a matsayin haka amma ba dan ina so ba Abiy. Na san na furta maka ina sonsa amma tunda akace na bari na haƙura gabaɗaya, ka tambayi Mama itace take bani ƙarfin guiwa amma na ce mata tunda baka so na haƙura. Ka yi haƙuri Abiy, wallahi ko me ka ke zargina dashi ban yi ba, ko tafiyata Kano ban je dan na ɓata maka rai ko dan ka kasa bani abinda nake so ba" ta faɗa da kuka sosai.

Abiy yayi shiru yana kallon ta, gabadaya kalamanta sun gama sanyaye masa jiki, zuciyarsa tayi rauni tausayin Naylan ya mamaye masa zuciya. Nayla ta kalli su Yaya ta ce, "Yaya da Yaya J wallahi ban yi komai ba, ku daina fushi dani. Kun ji Abiy yace kar nazo gidan nan, ya ce baya so na zo, na zauna a Kano...!" Ta faɗa tana ƙara ƙarfin kukanta wanda yake nuni da kalaman sun dake ta sosai.

Nayla ta gama raunana zuciyar Jawad, ji yake kamar ya zubar mata da hawaye. Ya ta so da hanzari ya ƙaraso inda take ya miƙar da ita sai ta kwanta a jikinsa tana kuka. Shi kansa sai da yayi hawayen tausayinta, ya ɗagota daga jikinsa ya zaunar da ita akan kujera ya kawo mata ruwa da kansa ya bata ta sha tana sauke ajiyar zuciya. Jawad ya ce, "ki daina kuka, ni bana fushi da ke Nayla, ina tare da ke a ko yaushe. Duk abinda ki ke so a ko yaushe ki kira ni ki faɗa min, kuma ko meye ya faru wanda ki ke neman taimako ki sanar dani zan yi miki."

Kai ta ɗaga tana kallonsa ta kalli Abiy da yake kallonta. Kafin tayi magana ya rigata dan in ya bari ta cigaba da magana bai san abinda zai yi ba saboda tausayi da rauni da ƙaunarta da yake ji a zuciyarsa, hakan ya saka ya katseta ya ce, "Ku tashi ku wuce lokaci yana tafiya" ya faɗa yana miƙewa tsaye.

Nayla ta ce, "Abiy!." Ya kalle ta ba tare da ya amsa ba, sai ta dawo ƙasa ta durƙusa ta ce, "ka yafe min, wataƙila bazan isa Kano da rai ba, wataƙila kuma bazan sake ganinka ba. Ina ji a jikina kamar mutuwa zanyi, don Allah ka yafe min."

Ajiyar zuciya yayi ya kalleta ya ce, "baki yi min laifin komai ba, kuma ni ba fushi nake da ke ba. Zaki je Kano lafiya in sha Allah." Nayla ta ce, "Abiy in na mutu ka yarda a kawo gawata gidan nan? Kar ka ce za a binne ni a Kano don Allah, ina so a kawo maka ni ka yi min wankan gawa da kanka."

"Ya salam!" Abiy ya furta saboda yadda kalamanta suka daki zuciyarsa, kusan irin kalaman da mahaifiyarta ta dinga amfani dasu ne a lokacin da take gab da barin duniya shiyasa kalaman suka dake shi har cikin jininsa. Hannunsa ta riƙe ta ce, "Abiy ka yafe min, ban yi komai ba wallahi. Ina sonka Abiy, bazan iya ɓata maka rai ba, duk abinda ka ce na bari ina barinsa da zuciyata da gangar jikina. Wallahi na bari tunda ka furta baka so, ka daina kallona da wannan laifin don Allah." Abiy da yake kallonta ya yi ajiyar zuciya, ya lura bata cikin hankalinta hakan ya saka ya kalli Yaya da Jawad ya ce, "Ku tashi ku wuce" yana faɗa yana zare hannunsa daga cikin nata ya shige ciki ya barsu a wajan.

Mama ta riƙe Nayla suka fito tana kuka zuwa motar Yaya, duk jikinsu ya yi sanyi har Maman zuciyarta tayi rawa sosai musamman kalaman Nayla na mutuwa. Jalila da su Salma kuwa kuka suke yi sosai, Yaya ma ya kasa magana sai kallon Nayla da yake yi cikin rauni da tsananin ƙauna da tausayinta. A haka aka saka kayanta a booth ɗin motar, Jawad ma ya shiga ta sa motar, Salma da Jidda da Jalila suka shiga mota kuka aka ja mota suka fita daga cikin gidan.

KRB2P027

ArewaBooks@nanahaleema11

Abiy yana tsaye a balcony yana kallon lokacin da motarsu ta fita daga gidan. Wani irin yanayi yake ji a zuciyarsa mai wahalar fassarawa, sai yanzu yake tuhumar kansa akan meyasa ya yiwa gudun jininsa haka? Meyasa bai sake bata lokaci ba? Shin Nayla ta cancanci wannan hukunci daga gare shi kuwa? Anya bai cutar sa marainiyar Allah ba? Haƙƙinta bazai kama shi ba. Ajiyar zuciya yayi ya kulle ido yana tunani.

Abiy ni na san wannan ciwo ba na tashi ba ne, ga amanar yata Nayla nan na bar maka, ka kula da ita yadda ya kamata. Na san za ka yi koda ban ce ba, amma ina sake maimaitawa ne matsayina na mahaifiyarta. Na san zaka bata tarbiyayya mai kyau, na san Zeenatu zata riƙe min ita hannu biyu ta yi mata tarbiyya tare da su Jidda. Abiy! don Allah kar ka bari Nayla ta yi kukan rashina a tare da ita, kar ka bari ta zubar da hawayen maraici, ka zame mata uwa, ka zamar mata uba, ka zamar mata jigo a rayuwarta.

Ido ya buɗe tunawa da wasiyyar mahaifiyar Nayla, ya sauke ajiyar zuciya ya ce, "Allah ya ba ky zaman lafiya Nayla, Allah ya sa wannan auren ya zama alkhairi a gareki." Barin wajan yayi jikin sa a sanyaye ya rufe balcony ɗin ya dawo falo ya zauna zuciyarsa cike da tunani akan abinda ya faru.

••••••••

Dad kallon Mum yake yi tunda ta dawo daga America bai ji ta ce masa komai akan batun Narma ba, hakan ya saka shi tambayarta a wannan lokaci ya ce, "My dear Ina jiranki, me yake faruwa da Narma a can? Ina fatan komai lafiya dai ko?." Mum ta

kalle shi ta ce, "babu lafiya, Narma ta canja kamar ba ita ba, ta rame sosai kamar bata cikin farin ciki."

Da mamaki Dad ya ce, "rashin Lafiya ta yi ta rame?." Mum ta ce, "lafiyarta qalau, kawai ni na ga alama bata jin daɗin zama da Ashraf gabaɗaya. Har yanzu da wannan yaron a zuciyarta, babu Ashraf a rayuwarta yanzu gabaɗaya." Dad ya ce, "wannan masifa har ina? A can ɗin ma bata huta ba?." Mum ta ce, "sannan ka san Narma bata son wahala ko kaɗan, shi kuma Ashraf ya kasa haƙuri da yanayin da take ciki yana raping ɗinta ko yaushe."

Dad ya ce, "wanne irin raping kuma? Mijita ne fa."

"Mijin ta fa, ta ya zai dinga zuwa wajanta ba tare da izini ba? Ai dan yana mijinta ba hakan yana nufin ya dinga amfani da ita duk sanda ya so ba, akwai lokacin da zata ji bata ra'ayi ko da yana ra'ayi sai ya ƙyale ta tunda bata so. Kuma a wannan yanayin da take ciki ni ban ɗauka ma Ashraf zai kai wannan waje ba, na ɗauka zai bata time ya rarrashe ta har ta dawo nutsuwarta sannan sai su yi honeymoon ɗinsu. Amma yanzu ga damuwa, ga wannan tsinannen yaro, ga damuwarsa da me zata ji?."

Dad ya yi murmushi ya ce, "in dai wannan ne babu abin damuwa a nan, na tabbatar faɗar Narma ce babu wani rape, ki manta kawai."

"Na gani da idona ka ce babu wani rape? Ni gabaɗaya aurenta dashi ya fara fitar min daga rai wallahi, bata samun farin cikin da muka so ta samu a gidan."

Dad ya ce, "zan kira Ashraf ɗin naji abinda yake faruwa." Mum ta ce, "ya dai kamata gaskiya, zuwan mu baka ga yadda ta sake ana yawo ba. Amma lokacin da mu je tana ɗaki a kwance shi kuma yana falo. Meye hakan yake nufi? Ni kar ya ɗorawa yarinyata ciwo fa."

Dad ya ce, "gaskiya akwai damuwa, amma ki bari zamu bi komai a hankali mu gani. Zan kira shi na ji in da matsala sai ya dawo da ita nan ayi bikin kawai a huta, sai ta zauna a nan Abuja yadda zamu dinga ganinta ko yaushe." Mum ta ce, "da dai ya fi gaskiya" ta faɗa tana kawar da kai gefe dan gabaɗaya zaman Narma da Ashraf ya fita daga zuciyarta.

•••••••

Kafin sallar juma'a suka shiga Kano, kai tsaye gidan Hajja aka wuce kamar yadda aka ce za a yi. Ana ajjiye motar suka fita zuwa cikin gidan Mama na riƙe da hannun Nayla, fuskarta a buɗe dan mayafin ma ya dawo kafaɗa dan bata da nutsuwa. Gidan cike da mutane suka tarar dashi, matan su da Daddy da yan uwa duk dai dangin mahaifiyar Nayla suna gidan.

Nayla na shiga ta ƙarasa wajan Hajja ta zube a kan guiwarta ta ɗora kanta a jikin Hajja bata ce komai ba. Hajja ta dafa kanta ta ce, "Sannun ku da ƙarasowa Hauwa'u." Ta kalli Mama ta ce, "Zeenatu barka da hanya." Da fara'a Mama ta gaishe da kowa na wajan suka amsa mata da murmushi dan tana burge su bata da matsala ko kaɗan.

Mama ta ce, "To Hajja ga Nayla nan dai Abiy ya saka mun kawo ta, sai haƙuri da yadda abin yazo gabaɗayam mu bamu yi tunanin hakan zai faru ba." Hajja ta murmusa ta ce, "ƙaddarar kenan ai, baka sanin ta inda zata zo ba balle ka yi ƙoƙarin kiyayewa kafin zuwanta. Babu komai, in sha Allah alkhairi ne."

Mama Sa'adatu ta dafa Nayla ta ce, "Nayla sannu, jikinki akwai zafi, kanki na ciwo?." Nayla ta ɗaga kai alamun eh, Salma ta ce, "Mama ba dole tayi rashin lafiya ba, kullum cikin damuwa da kuka take. Yanzu ma tunda muka taho ko ƙala bata ce ba, sai dai tayi hawaye ta gaji ta daina." Mama Sa'adatu ta ce, "ki yi haƙuri Nayla, duk ɗan adam baya tsallake ƙaddararsa kin ji ko?."

Bata ce komai ba ko motsawa ma bata yi ba, tana jikin Hajja da take shafa kanta a hankali cikin shigar rarrashi. Lokacin sallah da ya yi ne ya tashe su gabaɗaya, akayi alwala aka yi sallah sannan aka ci abinci. A lokacin Jawad da Ahmad suka shigo suka gaisa da mutanen gidan kafin su shiga mota su tafi.

Nayla na zaune a ɗakin da take kwana tayi tagumi, Mama Sa'adatu ce ta shiga ta cire mata tagumin ta zauna kusa da ita ta riƙe hannunta ta ce, "Ki daina tagumi kin ji ko?." Nayla ta ɗaga mata kai kafin ta ce, "yanzu me ki ke so?."

"Babu komai Mama."

"Ki faɗa min in akwai abinda ki ke so na kawo miki."

"Babu Mama."

"Kin sha maganin ciwon kan?." Ta ɗaga Kai alamun eh ta ce, "to ki kwanta ki yi bacci zaki ji daɗi."

Nayla ta ce, "bazan iya baccin ba." Mama ta ce, "to me za ki yi?."

"Nima ban sani ba" ta faɗa murya na rawa alamun zata cigaba da kuka. Mama ta ce, "kar ki yi kuka mana, ni kukan ne bana so na gani." Nayla ta ce, "Abiy yana fushi dani Mama."

"Kar ki damu komai zai wuce. Ba dai kina son mijin na ki ba?." Nayla ta sunkuyar da kai ta ƙasa bata amsa ba. Mama ta ce, "Nayla ni ƙanwar mahaifiyarki ce, baki da wata uwa kamar ni. Ki faɗa min abinda yake ranki kar ki ji kunya, kina son mijin ko?."

Nayla ta ce, "Mama da dai nasan ina sonsa, amma yanzu tunda ake kiransa da mijina na kasa tantancewa." Mama ta ce, "zaki tantance sai a hankali, yanzu ma ruɗani da yadda abin yazo bazata shine ya saka ki ke jin hakan. Amma kar ki damu komai zai zo ya wuce ya zama tarihi. Abiy ba ya fushi dake, ki kwantar da hankalinki."

"Fushi yake yi Mama, tunda na furta Ina son sahikenan ya canja. Mama Abiy ne yake cewa kar na je gida sai ya ce na je, in ba fushi ya yi dani ba meye?. Mama daga zuwana Kano na koma na ji labarin wai ya aura min shi."

Mama ta ce, "to ke waye ya ce ki zo Kano baki tambaye shi ba?." Nayla ta ce, "Mama ce. Mama ce tazo zan fi samun nutsuwa a nan, itace ta saka aka kawo ni amma ni ban yi niya ba." Shiru tayi tana kallon Nayla kafin ta ce, "ita ta san kina son Omar ɗin ne?." Gaban Nayla ya faɗi, indai aka ambaci sunansa sai gabanta ya faɗi matuka. A hankali ta ce, "ta sani, itace ta ke bani goyan baya akan shi. Dan koda Abiy ya ce na manta dashi tana cemin kar na damu zata san ya zata yi."

Mama Sa'adatu ta yi ajiyar zuciya ta ce, "shikenan dai ki kwantar da hankalinki, komai zai wuce. Kuma mahaifinki baice kar ki je gida saboda yana fushi ba, yana so

ki nutsu ki yi zaman aure, kar wannan ya dame ki kin ji?." Kai ta ɗaga almaun to. Mama ta tashi ta bar ɗakin zuciyarta cike da zargin wani abu akan Mamansu Jidda.

Bayan an idar da sallar juma'a mutane suka ɗan ragu a gari sai ga Mama Zaliha ƙanwar Abiy itama rarrashinta dai ta dinga yi. Gidan Hajja ya zama gidan biki domin kuwa an cika shi dam da yɷan uwa ana hira ana kuma cin abinci. Nayla da aminanta kuwa suna ɗaki tana kwance akan gado su kuma suna gefen suna aikin rarrashinta da kalamai masu daɗi.

Didi kuwa tana gida ta kasa shiga gidan Hajja, gabaɗaya kunyarsu Hajja take ji, sai ta ga kamar tana da laifi akan abinda aka yiwa Nayla. Tana zaune ya dawo daga masallacin juma'a ta ce, "Yauwa Omar, don Allah zuwa sallar magriba ka dawo saboda akwai abu mai mahimmaci da za a yi." Ya bita da kallo yana taɓe baki ya ce, "to zan duba na gani."

"Ba dubawa zaka yi ba, yi zaka yi don Allah."

"To" ya furta dan shima ta saka shi a tunanin abinda zai farun nan.

Fita ya yi ita kuma ta zauna tana hasaso abinda zai faru, idanunta kallo mata Omar suke yi yana tijara da rashin mutunci a gaban mutane. A bayyane ta ce, "in sha Allah bazai yi ba, zai nutsu ya saurare abinda za a ce masa in sha Allah."

Da yamma Mama Zaliha ta tafi gida sauran matan su Daddy ma sun tafi ya rage Mama Sa'adatu ce kawai su Jidda da Jalila da kuma Mamansu Jidda.

Mama Sa'adatu ta ce, "Ina Aisha ne? Ya kamata ta shigo ta bamu key mu je mu ga inda Nayla zata zauna ko Maman Jidda?" Ta faɗa tana kallon Mama. Mama ta ce, "gaskiya ne, nima a waya na dinga ganin gidan da ana shiryawa, ya kamata muje kam." Mama Sa'adatu ta ce, "bara a kirata, sai mu je mu dawo tunda an ce babu nisa."

Salma aka tura aka ce taje ta karɓo key ɗin, ta shiga ta samu Didin duk tayi tsuru-tsuru kamar mara gaskiya. Salma ta ce, "Hajiya Didi lafiya ki ke kuwa?." Ta yi murmushin yaƙe ta ce, "Lafiya lau Salma, Ya taro?."

"Alhamdu lillah. Su Mama ne suka turo ni akan ki bada key na gidan za a je a gani." Didi ta amsa a sanyaye ta ɗauko ta miƙawa Salma tare da yi mata kwance sa sannan ta ce, "Ya Nayla kuwa?."

Salma ta ce, "Tana nan a kwance."

"Bata da lafiya ko?."

"Kusan hakan gaskiya." Didi tayi ajiyar zuciya ta ce, "Allah ya bata Lafiya, ki gaishe ta zan shigo zuwa anjima in sha Allah." Salma ta ce, "Amin. Ni na ɗauka a gidan ma zamu zo mu same ki." Didi ta ce, "hmm Salma baza ki gane ba, ki je kawai sai na zo." Salma ta amsa mata ta fita ta kai musu key ɗin ta koma inda take zaune.

Bayan sallar magriba Omar ya dawo kamar yadda ta ce, tana ganin shigowarsa ta miƙe ta ce, "Yauwa sannu da zuwa. Ka taimaka min yadda Allah ya taimake ka kayi wanka ka canja kaya, kar kace ƙananun kaya zaka saka, don Allah ka saka manyan kaya."

Ya bita da kallo bai ce komai ba ya zauna sannan ya ce, "ni yunwa nake ji." Didi ta wuce kitchen ta kawo masa abinci ta ce, "ga abinci ka ci." Karɓa ya yi ya fara ci yana kallonta ganin gabaɗaya bata cikin nutsuwarta.

Ajjiye abincin ya yi ya kalle ta ya ce, "Didi wai me ya mayar dake haka ne? Gabaɗaya kin firgice bakya tare da nutsuwa sam. Da kin bani haushi na ce bazan sake tambayarki ba amma na kasa, meye ne don Allah?." Didi ta ce, "samun nutsuwata ka kammala mu je inda zamu je."

"Indai na je na shirya mu ka tafi zaki nutsu?." Kai ta ɗaga alamun eh ya ture abincin ya ce, "shikenan bara a yi sallar i'sha sai na shirya ɗin, bana son wannan yanayin na ki wallahi, gabaɗaya bana jin daɗi in na ganki a haka." Didi ta ce, "ka ci abincin tukunna."

"Ya fita a raina" ya faɗa yana tashi ya fita ta bishi da kallo. Hawaye taji suna sakko mata, tunaninta kawai ta ya Omar zai karɓi auren Nayla? Tuna hakan kawai faɗuwar gab yake sakata, balle ta san bakinsa da bashi da control komai ya zo bakinsa faɗa yake yi ko a gaban waye.

Tana nan zaune taji kiran sallar i'sha ta tashi a sanyaye tayi sallah ko shafa'i da wutir bata yi ba tana zaune tana jiransa. Wayar Didi ce tayi ƙara ta ga sunan Salma ta ɗauka da sallama, Salma ta amsa ta ce, "Didi su Daddy ne suka ce na faɗa miki suna hanya, ku shigo gidan Hajja yanzu zasu ƙaraso." Daƙyar ta iya amsawa sannan ta kashe wayar cike da tsoro.

Babu jimawa taji an dafa kafaɗarta, ta ɗago kai ta kalle shi kamar yadda yake binta da kallo cikin son gano damuwarta. Kamar ta buƙata ya yi wanka ya canja kaya zuwa manyan kaya riga da wando na shadda ash colour. Ya yi mata kyau sosai a idanunta, ta zuba amsa ido tana kallo kafin ta miƙe tsaye ta ce, "ka yi kyau." Kallon fuskarta ya yi ya ce, "kuka ki ka yi?." Kai ta girgiza alamun a'a ya ce, "gashi nan na gani a idanunki, kuka ki ka yi Didi? Ban san wanne abu ne wannan da ki ka kasa sanar dani ba, kodan kin yi aure ne yanzu kina ganim ban kai na san damuwarki ba ban sani ba."

Didi ta ce, "yanzu zaka ji."

"Mu je to, na shirya ko?." Ta kalle shi ta ce, "shiyasa na ce ka yi kyau, dama zaka saka babbar riga."

"Taɓ bazan iya ba, ni bani da babbar riga ma a duniya. Ban sani ba ko sai nan gaba." Didi ta yi murmsushi kawai bata ce komai ba sai ya kalle ta ya ce, "wataƙila sai aurena zan ɗinka." Gabanta ya faɗi sosai a haka ta yafa mayafi ta ɗauki jakarta da wayarta ta ce, "ka kashe hasken gidan sai mu je."

Ya kalle ta da mamaki ya ce, "Kashe hasken na meye kuma? Abinda dai zan dawo." Ta kalle shi ta ce, "Don Allah ka kashe, in ka kashe ka kulle gidan." Zai yi magana ta ce, "Allah na ce." Bai ce komai ba ya yi abinda ta ce suka fito ƙofar gidan ya kulle sannan ya kalleta ya ce, "Sai ina....?."

KRB2P028

Arewabooks@nanahaleema11.

Kallon ƙofar gidan Hajja tayi ta ga manyan motoci da alama su Daddy ɗin sun iso. Ta kalli Omar dsa yake kallonta yana jira yaji inda zasu jw ta ce, "Zo mu je." Gaba tayi yana binta a baya har ƙofar gidan Hajja. Da mamaki yake kallon ta ganin ta tura gate ɗin ta shiga sai ya ce, "na jira ki?."

"Ka shigo dai."

"A'a ban yi niya ba gaskiya, ko na shiga babu lada, kedai ki je ki gaishe ta."

"Ka shigo Omar, don girman Allah." Mamakin wannan magiyar da take yawan yi masa yake yi ta san kuma baya so, babu yadda iya haka ya shiga kamar yadda ta ce.

Sallamarta da shigar falon ya saka suka mutanen falon suka san sun iso aka amsa mata tana bin kowa da kallo. Gaisawa suka yi da kowa da yake zaune, Omar da yake bayanta ya gaishe su cikin gaisuwarsa ta ko yaushe taƙaitacciya. Kallon Didi yayi ya ce, "ina jiranki a waje." Hannunsa ta riƙe ta ce, "ka shigo ka zauna." Kallon mutanen falon ya yi da suke kallonsa ya kalle ta ya ce, "na zauna nayi me kenan? Zan dai jira ki." Didi ta ce, "ka zauna don Allah."

Juya idanu ya yi cikin gajiya ya ce, "wai magiyar nan ta meye? Kin fara isata wallahi." Didi ta yi ƙasa da murya ta ce, "Mutane suna jinka, don darajar annabin Allah ka zauna." Ajiyar zuciya ya yi bai ce komai ba ya ƙaraso ya zauna akan carpet kamar yadda ta zauna.

Daddy ya kalli Abba da yake kallonsa shima suka ɗauke kai a tare. Nayla tun da ya shigo da maganarsa ƙirjinta yake bugawa, tana jin gardama da yake yi akan ya zauna, a nan ta tabbatar da har lokacin bai san abinda yake faruwa ba. Hawaye ta ji na sakko mata cikin tausayin kanta.

Daddy ne ya fara magana bayan an buɗe taro da addu'a ya ce, "kowa ya san abinda ya tara mu a nan,magana ce akan abinda ya faru da kuma wanda zai faru yanzu. Nayla dai an ɗaura mata aure a wani bahagon yanayi wanda mahaifinta ne kaɗai ya san dalilinsa na yin hakan. Amma ya ba mu ragamar kula da komai a yanzu, ya ce mu gyara inda aka ɓata shiyasa mu ka zo aka zauna gabaɗaya domin a tattauna a kai."

Omar jin kalaman Daddy ya saka shi ya kalli Didi zai yi magana ta yi masa alamun don Allah ya yi shiru. Dole ya yi shiru amma shi bai ga amfanin zamansa ba, har ita Didin bai ga amfanin zamanta ba tunda taro ne na familynsu to su me zai kawo su ciki?.

"Omar!." Daddy ya katse masa tunani hakan ya saka ya ɗago yana kallonsa ba tare da ya amsa ba. Daddy ya ce, "ka san wannan?." Ya faɗa yana nuna masa Nayla da take zaune kai a ƙasa. Kallon inda aka nuna masa ya yi ya sake kallon Daddy ya girgiza kai alamun bai santa ba.

Daddy ya yi murmushi shi kuma Omar ya mayar da kai ƙasa dan baya jure magana da manyan mutane irin su Daddy, Daddy ne mutum na biyu bayan Abiy da ya yi amsa kwarjini a duniya. Daddy ya ce, "Omar ranar juma'a da ta gabata sati ɗaya kenan yau, ƙaddara ta gifta a tsakani har aka yanke hukunci ba tare da ka sani ba. Domin kuwa a wannan ranar aka ɗaura aurenka da ita wacce take zaune yanzu." Omar bai motsa ba dan bai ɗauka shi Omar ɗin ake nufi ba, ya yi tunanin akwai wani Omar ɗin a wajan bayan shi.

Ganin bai nuna firgici ba sai Didi ta ɗan ji sanyi tana cigaba da kallonsa. Daddy ya ce, "Mahaifin Nayla ya yanke hukunci cikin wani yanayi na fushi da wani dalili na sa, ya aurawa ƴarsa kai kamar yadda ake ɗaura ko wanne aure. Wakilanka sun shaida dan sune suka karɓi auren, sannan Yayarka ma ta shaida anyi hakan. To mun zauna a nan ne dan mu ji ta bakinka akan auren, dan yanzu ga amarya ma an kawo ta daga Kaduna zuwa nan. Kana ganin zaka iya zama da ita a matsayin mata?. In baza ka iya ba kar kayi mana kara, ka faɗi abinda yake zuciyarka domin muna so komai ya ƙare a nan wajan."

Shiru kowa ya yi ana jiran amsar Omar, shi kuma bai ce komai ba dan har ga Allah bai ɗauka dashi ake magana ba. Ganin shirun ya yi yawa Hajja ta ce, "Ummaru!." Ɗago kai ya yi ya kalle ta ta ce, "baka ji abinda aka ce ba ne?." Omar ya ce, "na ji mana."

"Baka ce komai ba." Ya kalli Hajja ya ce, "Hajja a ganina kamar maganar ai bata shafe ni ba ko? Zamana a wajan nan ma bashi da amfani tunda maganar da ta shafeku ku ke yi. Ba batun aure naji ana yi ba?."

Hajja ta ce, "shi ake yi mana, kuma in bai shafe ka ba ai ba za a ce kazo ka zauna ba Omar." Ya ce, "nima shine nayi mamaki ai. Yanzu me ya shigo da ni cikin maganar?." Didi ta ce, "Saboda kaine mijin! Kaine Omar ɗin da ake zancen ɗaurawa aure da Nayla jikar Hajja!."

Kallon Didi ya yi ya ɗauke kai dan gani yake ba dashi take ba, sake kallon ta ya yi yaga dai shi take kallo ya ce, "Didi!." Ta ce, "Omar!."

"dawa ki ke maganar nan?."

"Da kai nake, da kai nake Omar Osman Omar!. Kai ne wanda aka ɗaurawa aure tun last week a gidan Kawu, ni kaina shaida ce dan a gabana aka yi."

Kallon ta yake yi dan wallahi ya ɗauka ta ɗan samu matsalar kai ne ya saka take cewa haka. Hakan ya saka ya tausasa murya ya ce, "Didi tun ɗazu na faɗa miki ba a nutse ki ke ba, ki bari ki nutsu sai ki yi magana. Me zai kawo ni cikin batun aure kuma? Wani Omar ɗin ne daban amma ba ni ba. Duk inda akace Omar sai ki ɗauka ni ake nufi? Ki nutsu don Allah" ya faɗa yana kallonta har lokacin bai amince dashi ake ba.

Abba ya ce, "Omar ƙanin Aisha kalle ni." Ba musu ya kalli Abban ya ce, "dakai ake, maganar da ake faɗa akanka take ba wani ba. Kai mijin Nayla ne tun waccan juma'ar, Nayla matarka ce ta sunna." Kallon Abba ya ke yi dan ya san dai bazai masa ƙarya ba, ya kalli Didi da take kallonsa ta ce, "E da gaske ne."

Omar ya ce, "E da gaske ne me?."

"An ɗaura aurenka tun wancan satin a gidan Kawu."

"amma dai a mafarki ko? Mafarki ki ka yi akan hakan ko kuma wannan ma mafarkin ne?." Mama Sa'adatu ta fusata da kalaman Omar na rainin hankali ta ce, "Omar ba mafarki ba ne gaskiya ne, da gaske an ɗaura maka aure da Nayla tun waccan juma'ar da ya wuce. Ka daina yi mana wasa da hankali mana."

Shiru Omar ya yi na wani lokaci bai ce komai ba, ya sake kallon mutane falon ya tabbatar dai ba fa mafarki yake yi ba da gaske ne. Ya ɗan girgiza kai ya ce, "Aure!." Kallon Didi ya yi da take kallonsa dan ta kasa ɗauke ido daga kansa, ta san hali ƙiris yake jira yayi wani abun,shiyasa duk motsinsa a kan idonta yake yi. Omar ya ce, "Ni na kasa fahimta ne Didi, wai auren na wasa ko na gaske?."

"Omar ana aure da wasa ne? In auren wasa ne zaka ganmu a zaune a wajan nan ne?, ai mu ba abokan yin wasan ka bane. Ka nutsu mu yi maganar da ta tara mu a nan. Kamar yadda ka ke jin maganar bazata haka mu ma muka ji ta, In kana ganin

ƙarya mu ke yi maka ka kira Kawunka ka tambaye shi sai ka tabbatar" Abba ya faɗa cikin faɗa dan Omar ɗin ya fara fusata shi.

Omar ya yi shiru tare da yin ajiyar zuciya ya ce, "aure dai, kuma dani. To akan me? Meyasa sai ni?." Daddy ya ce, "na faɗa maka tun farko, ɓacin rai ne ya jawo mahaifinta ya aikata hakan, yanzu zaman da muka yi akan mafita ne."

Shi wallahi har lokacin bai gamsu sosai ba shiyasa hankalinsa bai wani tashi ba, to haka kawai za a tara mutane ace wai ga matarsa an ɗaura masa aure tun waccan juma'ar? Hauka yake yi da zai amince da wannan wasan yaran?.

Didi ta fahimci bai yarda ba har lokacin hakan ya saka ta ce, "Omar kalle ni." Ba musu ya kalleta ta ce, "ka daina jin abin kamar ba gaske ba, da gaske an ɗaura maka aure tun waccan juma'ar, ni shaida ce dan har goron daurin aurenka na saka a bakina na tauna. Ka san bazan maka ƙarya ba, Wallahil azim Nayla matarka ce tun kwana bakwai da suka wuce."

Sai a lokacin ya dawo hayyacinsa, ya zubawa Didi ffirgitattun idanunsa cikin kakkausar murya ya ce, "Akan me? Wacece Nayla? Meyasa sai ni, Meyasa baki faɗa min tun ranar ba!?" Ya faɗa cikin murya mai amon gaske.

Didi ta ce, "ka nutsu kar ka...." Katseta ya yi ya ce, "bazan nutsu ba, bazan nutsu ba Didi!. Kin san da wannan maganar ki ka ɓoye min? Kin san da wannan abin ki ka bari har aka kai yanzu ban ɗauki mataki ba?." Daddy ya ce, "Omar ka nutsu mu yi magana duk akan hakan aka taru."

Kallon Daddy ya yi ya ce, "abinda ya ɗaure min kai akan me aka yi haka? Saboda ran mahaifinta ya ɓaci kawai sai a ɗaura min aure da wacce ban sani ba?. Auren hukunci ne a gareta kenan? Hukuncin ɓatawa mahaifinta ran da tayi ko me ye?. In hakan ne kenan ni ne ƙarshen hukuncin da za a yi mata ranta ya ɓaci ko a ƙunatata mata tasan ta yi laifi kenan?" Ya sake kallon Didi ya ce, "kuma wai kin san da wannan maganar amma ki ka kasa faɗa min har aka zo yanzu ban sani ba. Su waɗanda aka ƙulla abin dasu sun san ai nafi ƙarfin hakan, shiyasa aka yi ba tare da na sani ba. Babban abin haushin ma da aka haɗa kai dake aka munafurce ni Didi.....!" Ya ƙarasa faɗar maganar a hankali yana zazzaro idanunsa waje.

Didi ta ce, "kaga Omar ka tsaya ka ji abinda za a ce maka mana, ka yi shiru baka ganin manya ne a gabanka?."

"Sanin su ɗin ne a gabana ya saka nake wannan maganar, tunda na shigo girman su da kwarjininsu ya cika min ido, a karo na biyu a rayuwata da naga wanda nake jin girmansu a idona tunda nazo duniya, in ba dan haka ba babu yadda zan yiwa magana. Aure Didi? Na ce miki ina son aure ne? Ko na ce miki Ina buƙatarsa nan kusa?. Ya muka yi dake? Bana faɗa miki ko da wasa kar kiyi wannan gangancin ba?." Didi ta dafe kai ta rasa abinda zata ce, gashi ta san in bata katse shi ba wallahi zai yi abinda bazata daina jin kunyarsu Daddy ba har abada.

Daddy da yake kallon Omar ganin yadda yake zarewa Yayarsa ido sai yayi murmushi yana girgiza kai ya ce, "mu ne iyayen yarinyar da aka ba ba, duk da mahaifinta baya wajan nan amma mu ma iyayenta ne. Shiyasa muka zauna a nan domin ka san da auren ka kuma tsayar da matsaya akan auren." Abba ya ce, "mu ma duk ba mu ji daɗin hakan ba, yadda ka ke ji ba a kyauta maka ba haka muke ji, itama yarinyar haka taji a ranta, amma babu wanda zai yi kokawa da ƙaddara a cikin mu, yadda Allah ya rubuta sai ta zama matarka sai ta zama koda na kwana ɗaya ne. Don haka yanzu me ka yanke?."

Omar kai tsaye ya raunana murya ya ce, "bana so! Ni ban san ma yarinyar da ake magana a kai ba dan haka bana so. Daman munafurta ta aka yi aka ɗaura auren, to yanzu na sani kuma ban karɓa ba!." Daddy ya ce, "ka tabbatar da hakan?." Kamar ya yi tsaki amma sai ya fasa, wai ya tabbatar da hakan, kamar shi ake yiwa wannan tambayar tsabar rainin hankali.

Mama su Jidda sai a lokacin tayi magana ta ce, "a dai bi komai a hankali." Mama Sa'adatu ta ce, "babu zancen abi komai a hankali Maman Jidda, tunda baya so kawai a datse auren yanzun nan."

Ta kalli Omar ta ce, "kawai ka saketa!." Babu ɓata lokaci Omar ya buɗe baki zai yi magana.....!

End of book 2

Book 2 ya ƙare a nan. Ya ku ke ganin lamarin zai kasance? Omar zai amince da auren nan ko a'a? Zai saki Nayla ko zai zauna da ita? In ya zauna da ita zata ji daɗin zaman aure dashi kuwa? Zai kyautata mata ko burin Mama zai cika?. Me ya haɗa Omar da ahlinsu? Ina labarin Narma? Omar zai aureta ko ya ya?. Ko baki karanta book 1&2 ba ina baki shawara ki karanta book 3, ya tara abubuwa da yawa a cikin wanda zai saka nishaɗi da farin ciki.

Sai mun haɗe....❤❤❤